

Nahawun Hausa Lambun

(البستان في قواعد الهوسا)

Wallafar

تأليف

Farfesa/ Sabry Ibrahim Ali Salama

Shaihun malamin harshen

Hausa da Adabobinta

أستاذ لغة الهوسا وآدابها

Kwalejin Nazarin Ilimomin

Afirka Na Gaba da Digiri-

كلية الدراسات الأفريقية العليا-

Sashen Harsunan Afirka

قسم اللغات الأفريقية

Jami'ar Al- Ƙahira

جامعة القاهرة

2020م



الكتاب

Nahawun Hausa Lambun

(البستان في قواعد الهوسا)

المؤلف : د. صبرى إبراهيم على سلامة

تصميم الغلاف:

رقم الإيداع:

الترقيم الدولي:

الآراء الواردة في هذا الكتاب
لا تعبر بالضرورة عن
دار الفراعنة للنشر والتوزيع والترجمة

النـاشر



رئيس مجلس الإدارة
إكرام عيد

نائب رئيس مجلس الإدارة
زينب أحمد

المدير العام
ياسر حسني

المدير التنفيذي
حبيبة وليد
:الإدارة

هاتف: (+2) 01014555784

واتس: (+2) 01006141645

مقدمة : Gabatarwa

مفهوم الهوسا Qarin bayani akan Hausa

تطلق كلمة هوسا على الشعوب والقبائل المقيمين بين مملكة برنو شرقا، والمنطقة الواقعة في الضفة الغربية لنهر النيجر غربا، ومن حدود مملكة أهير شمالا إلى حدود نهر بنوي جنوبا.

Ma'anar Kalmar Hausa:

Ana ambaton Kalmar Hausa ga mutanen da qabilun da suke zaune tsakanin daular Borno daga gabas, da yankin da yake bangaren yamma da tekun naijar, ta arewa kuma iyaka da daular Ahir zuwa iyakar rafin benwi ta kudu.

كما تطلق هذه الكلمة أيضا على اللغة التي يتحدث بها أهل هذه البلاد.

Kamar yadda ana amfani da wannan Kalmar akan harshe (yare) da mazauna waxannan wuraren suke Magana da shi.

ولغة الهوسا هي اللغة السائدة في شمال نيجيريا وفي المناطق المجاورة من جمهورية النيجر.

Harshen (yare) Hausa shine yaren da ake amfani da shi a arewacin Nigeria, da kuma wasu garuruwan dake maqwabtaka dasu acikin qasar Niger.

كذلك تتكلم بها جماعات أخرى كثيرة في مواقع مختلفة من مدن غرب أفريقيا، حيث تنتشر في كل من نيجيريا وغانا وسيريالون وليبيريا وبنين وتشاد والنيجر وتوجو وبركينافاسو.

Haka zalika, wasu mutane daban masu yawa, suna Magana da wannan harshen a wurare daban daban cikin qasashen Afirka ta yamma. Kuma akoda yaushe yana ci gaba da yaxuwa a dukkanin su Nigeria, Ghana, Seralion, Liberia, Benin, Cad, Niger, Togo, da Burkinafaso.

وتنتمي قبائل الهوسا إلى الجنس الزنجي، وهم زُرّاعٌ مهرة، وتجار مغامرون، وأهل فن حاذقون، ويدين أغلبهم بالإسلام.

Qabilun Hausawa suna dangantuwa ga jinsin baqaqe ne, kuma su manoma ne, zaratan yan kasuwa. Gasu kuma da qwararrun sana'o'i, galibin su suna bin addinin musulunci ne.

وفي بادئ الأمر كانت الهوسا موجودة في سبع أقاليم، وهي: كانو- زاريا- دورا- الجبر- كشنه- برام- رانو.

Da farkon al'amari, Hausa ta kasance a yankuna guda bakwai ne, sune: Kano, Zaria, Daura, Al jibir, Katsina, Biram, Rano.

ولغة الهوسا واحدة من اللغات الحية الكبرى واسعة الانتشار، وهي إحدى اللغات الهامة في القارة الأفريقية، حيث تأتي ضمن أكبر ثلاث لغات بها، العربية في الشمال، والسواحلية في الشرق، والهوسا في الغرب. (شمالا- شرقا- وغربا).

Harshen (yaren) Hausa ya kasance cikin manyan rayayyun harsuna mai saurin yaxuwa. Kuma ya kasance cikin yaruka masu mahimmanci a yankin Afirka. Ta yadda ma tana cikin mafi girman yaruka (harsuna) guda uku a yankin Afirka, su ne: Larabci a jihar arewa, Swahili a jihar gabas, sannan Hausa a yamma. (arewaci- gabsci- .yammaci)

وتنتمي هذه اللغة إلى الفرع التشادي والذي يضم عددا كبيرا من اللغات لا يقل عن ثمانين لغة. تأتي الهوسا في مقدمتها. وهذا الفرع ينتمي إلى أسرة اللغات الأفروأسيوية .

Kuma, wannan yare na Hausa yana komawa ga tushen (reshen) yarukan Cad, wanda yake xauke da adadi mai yawa na yaruka, waxanda bazasu gaza yare guda tamanin ba. Harshen Hausa shi ne agaba garesu. Shi kuwa wannan tushen (reshen) yana komawa ga dangin harsuna mai suna Afro asiyawiya.

Darasi na Farko:

الدرس الأول

Yana qunshe da waxannan abubuwan:

ويحتوي على الموضوعات الآتية:

نظام الكتابة في الهوسا

Tsarin rubutu a Hausa

حروف الهوسا

Harufan Hausa

الحروف الساكنة والمتحركة

Baqaqe da wasula

المقطع الصوتي

Gava

1- Baqaqen Hausa su ne kamar haka:

حروف الهوسا الساكنة هي الآتية:

A- Manyan Baqaqe:

الحروف الكبيرة الساكنة:

B- V- C- D- X- F- FY- G- GW- GY- H- J- K- KW- KY- Q- QW- QY- L- M- N- R- S- SH- T- TS- W- Y- ‘Y- Z.

الحروف الصغيرة   B- Qananan Baqaqe:
الساكنة

b- v- c- d- x- f- fy- g- gw- gy- h- j- k- kw- ky- q- qw- qy- l- m- n- r- s- sh- t- ts- w- y- ‘y-z.

Abin da aka hararo (hango) mai mahimmanci:

ملحوظة:

Baqin “P” ana amfani dashi cikin sakkwatanci, amma an soke shi cikin karvavviyar Hausa.

الحرف الساكن "P" يستخدم في لهجة سوكوتو، ولكن تم حذفه من الهوسا القياسية.

Koda haka acikin karvavviyar Hausa ma ana amfani dashi cikin sunayen mutane da na garuruwa da qasashe waxanda bana Hausa ba, kamr sua:

Pakistan, Paris, Peter, Pierre.

وعلى الرغم من ذلك فإنه يستخدم في الهوسا القياسية في أسماء الأشخاص والمدن والبلاد (الدول) التي ليست هوساوية، مثل: باكستان، باريس، بيتر، بري،

- حروف الهوسا المتحركة :

2- Wasulan Hausa:

Ba su sauya ba, gasu kamar haka:

وهي ليست مغلقة "أي أنها مفتوحة" وها هي:

حروف متحركة كبيرة: A- Manyan wasula:

A- E- I- O- U.

B-Qananan wasula: حروف متحركة صغيرة:

a- e- i- o- u.

Wasulan da suka zama a haxe bibiyu kamar “ai”- “au” sai a ci gaba da rubuta sub a “ay” da “aw” ba.

الحروف المتحركة التي أصبحت مركبة تتابعيا مثل "ai" "au" قد استمر العمل بها وليست "ay" " aw".

(Watau ba kamar yadda aka ce a rubuta a taron Bamako a 1966 ba).

(أي أنه ليست كما قيل بأن تكتب - كما هي- في مؤتمر باماكو المنعقد في عام ١٩٦٦م).

Watau; kamata ya yi a rubuta kamar haka:

أي: ينبغي أن يكتب كما في:

kaifi – حاد- حدة، qauye – قرية، faifai -غطاء

ba kamar haka ba: ولا تكون كما في الآتي:

،kayfi – حاد- حدة، qawye – قرية، fayfay -غطاء

وما يشابههم da sauran su.

وبالنسبة لطبيعة الحركة في الأبجدية الهوساوية، فإنها تنقسم إلى قسمين، حركة طويلة، وحركة قصيرة، وهي تشبه الحركات في الأبجدية العربية إلى حد كبير، حيث في العربية يوجد الفتحة والضمة والكسرة، وهي ما تعرف باسم الحركات الأصلية وهي قصيرة، وهناك الألف، والواو، والياء، وهي ما تعرف باسم الحركات الفرعية وهي طويلة.

والحركات القصيرة في الأبجدية الهوساوية تعرف gajerun wasula وتتميز بعدم وجود أي علامة فوقها "باستثناء" علامة النغمة " tone" وهي ما تعرف في الاصطلاح الإنجليزي باسم short vowels.

أما الحركات الطويلة وتعرف في الهوسا باسم dogayen wasula وتتميز بأحد شيئين إما بوجود شرطة قصيرة ممتدة فوق الحركة، وإما بتكرار الحركة نفسها، وذلك على النحو الآتي:

الحركات القصيرة: gajerun wasula:

a- e- i- o- u

الحركات الطويلة: dogayen wasula:

aa- ee- ii- oo- uu

وهي ما تعرف اصطلاحا في اللغة الإنجليزية باسم long vowels.

وحول هذا يقول بعض نحاة الهوسا:

Akwai dogaye da gajerun wasula gwargwadon halaye.

هناك حركات طويلة وحركات أخرى قصيرة بحسب الحال "ويقصد هنا بحسب بعض الكلمات"

Dogon wasali ana rubuta shi a maimaice, kamar haka:

أي الحركة الطويلة تكتب مكررة هكذا:

aa (a doguwa)

ee (e doguwa)

ii (i doguwa)

oo (o doguwa)

uu (u doguwa)

Gajeren wasali ana rubuta shi shi kaxai ne kamar haka:

أما الحركة القصيرة فتكتب بمفردها هكذا:

a- e- i- o- u

Dogon wasali

الحركة الطويلة:

Ana samun sa a irin waxannan halaye:

ويمكن أن يتحقق وجودها في المواضع الآتية:

A- الأسماء
Sunaye

Yawancin wasulan qarshe na sunaye dogaye ne, kamar doki (dookii), jaki (jaakii), kare (karee), saniya (saaniyaa), kotso (kootsoo), kunu (kunuu), da dai sauransu.

معظم الحركات الموجودة في نهاية الأسماء حركات طويلة، كما في "حصان- حمار- كلب- بقرة- إطار (الطبلة أو الساعة المائية كما تعني التردد النغمي أو الإيقاعي للطبلة".

B. Yawancin siffofi cikakku da siffofin fi’li (ko sunaye maf’ulai) qarshen su dogon wasali ne.

معظم الصفات التامة "المكتملة" وصفات الأفعال (وحتى أسماء المفعول) نهايتها حركة طويلة.

مثل:
misali:

dogo = طويل
doogoo

gajere = قصير
gajeeree

baqi
= baqii

أسود

أحمر

ja = jaa

kore

أخضر
= kooree

qonanne =

محروق- محترق
qoonannee

hamvararre =

مدفوع- مركول
hamvararree

sangameme =

ضخم- كبيرالحجم
sangameemee

kotso =

آلة موسيقية مثل الجيتار
kootsoo

تطويل أو تمديد الحركة:Tsawaita wasali:

A babi na baya mun yi Magana game da Karin sauti, mun bayyana cewa Karin sauti iri uku ne a Hausa. Akwai na sama da na qasa da kuma faxau. Mun kuma yi nuni da cewa dole ne ga mai koyon Hausa ya yi qoqarin faxar kowace gava ta kalma dangane da Karin sautinta na sosai. Domin canjin

Karin sauti kaxan zai iya canja ma’anar kalma ko ma ya komo da ita maras ma’ana. A wannan babi kuma Magana za mu yi akan Tsawaita wasali.

تناولنا في الباب السابق النغمة الصوتية، وبيّنا أن النغمة الصوتية ثلاثة أنواع: هناك نغمة مرتفعة ومنخفضة ثم الهابطة. كما أشرنا إلى ضرورة محاكاة (محاولة) دارس الهوسا في النطق بكل مقطع صوتي كما هو. لأن تغيير بسيط في النغمة قد يؤدي إلى تغيير المعنى أو يحوّل الكلمة إلى عديمة المعنى، وفي هذا الباب سوف نتناول تطويل أو تمديد الحركة.

Lamura iri daban-daban kan shafi wasali a Hausa.
Ma’ana, wasali kan xauki surori da dama dangane da sarrafuwarsa a harshen.

يحدث للحركات أمور كثيرة في الهوسا، يعني تأخذ الحركات صور مختلفة من حيث تحولها في اللغة.

Me ake nufi da tsawaita wasali? Tsawaita wasali shi ne inda ake jan wasali gajere ya komo dogo wajn lafazi. Wannan lamari yakan auku a muhallai daban-daban, wanda yake daga ciki za mu duba biyu. Za mu duba lamarin a muhallin tambaya da kuma muhallin mallaka.

ما المراد بتطويل أو تمديد الحركة؟ تطويل الحركة هو تمديد حركة قصيرة لتكون حركة طويلة في النطق. وهذا الأمر يحدث في أماكن (مواضع) مختلفة والتي

سنتحدث عن اثنين منها. سننظر إلى الأمر في سياق الاستفهام، وسياق الملك (الإضافة).

سياق الإستفهام:

A. Muhallin Tambaya:

Da farko dai bari mu duba waxannan jimloli, waxanda kalmominsu na qarshe suka qare da gajerun wasula.

في البداية، دعنا نتأمل هذه الجمل، التي انتهت حركات أواخرها بحركة قصيرة:

1. Audu yaa gudu

- فرّ عبده

2. Binta taa firgita

- فزعت بنت

3. Zaa su tafi

- سيذهبون

Kowacce daga cikin jimlolin nan uku ta bayani ce. Wato bat a tambaya ce ba. Haka kuma jimla ta farko ta qare da gajeren wasali /u/, ta biyu ta kare da gajeren wasali /a/, ta uku kuma da gajeren wasali /i/. yanzu in muka mayar da kowacce zuwa jimlar tambaya, me zai faru? Bari mu gani:

كلٌّ من هذه الجمل الثلاث جملة خبرية، أي أنها ليست استفهامية. وكذلك الجملة الأولى انتهت بحركة قصيرة /u/، والثانية انتهت بحركة قصيرة /a/، والثالثة

أيضا انتهت بحركة قصيرة /i/. فالآن إذا حوّلنا كلا منها إلى جملة استفهامية مالذي يحدث؟ فدعنا نرى:

1. Audu yaa guduu?

- هل فرّ عبده؟

2. Binta taa firgitaa?

- هل فزعت بنت؟

3. Zaa su tafii?

- هل سيذهبون؟

Babu shakka, a lokacin da aka mayar da irin waxannan jimloli na bayani masu wasula a qarshe zuwa jimlolo na tambaya waxanda gajerun wasula na qarshe take za su koma dogaye. Ma’ana, za su ja su wajen wannan lafazi. Kwatanta lafazin gudu da firgita da tafi na misalanmu na 1, da na 2, da na 3, da kuma misalai na 4, da na 5, da na 6. Bambancin a fili yake.

لا شك أنه حينما تحوّلت مثل هذه الجمل الخبرية ذوات الحركات القصيرة إلى الجمل الاستفهامية تتحوّل معها هذه الحركات إلى حركات طويلة. أي يتم تمديدها في هذا اللفظ. قارِن الألفاظ gudu -فرّ، و firgita- فزعت، و tafi– ذهب، في الأمثلة السابقة الأولى بالأمثلة السابقة الثانية، فالفرق ظاهر.

Duba wasu misalan:

تأمل أمثلة أخرى:

Jimlar bayani:

جملة خبرية:

1. Sun ci

- أكلوا

2. An ji

- سُمع

Jimlar Tambaya:

جملة استفهامية:

1. Me suka cii? -
   هل أكلوا
2. Daga ina aka jii? -
   من أين سُمع

Wannan shi ne yanayin tsawita wasali a muhallin tambaya a Hausa, yayin da Kalmar qarshe ta jimlar bayani ta qare da gajeren wasali, wannan wasali yakan koma dogo in aka mayar da wannan jimla zuwa ta tambaya,

هذا هو محل تمديد الحركة في سياق الاستفهام في الهوسا. عندما تنتهي الكلمة الأخيرة من الجملة الخبرية بحركة قصيرة، تتحول هذه الحركة طويلة إذا حوّلنا الجملة إلى جملة استفهامية.

B. A muhallin Mallaka: سياق الملكية (الإضافة):

A muhalli na mallaka ma akan tsawaita wasali, kamar yadda muka ambata. A wane muhalli na mallaka ne musamman wannan abu ke faruwa? Kowane muhalli in dai na mallaka ne, ko kuwa akwai qaidi? Haqiqa, ba a kowane irin muhalli na mallaka ne yake faruwa ba. Sharaxin shine, inda aka yi amfani da wakilin suna xan mallaka na ajin mutum na farko- naa/taa.

يتم تمديد الحركة أيضا في سياق الملك (الإضافة) كما ذكرنا سابقا. في أي موضع يحدث هذا في مثل هذا السياق؟ هل يحدث في المواضع كلها من السياق أو هناك قيود (حدود)؟ في الحقيقة لا يحدث هذا في المواضع كلها من سياق الملك (الإضافة)، والشرط هو في حالة استخدام ضمير المكتلم (naa) للمذكر و (taa) للمؤنث.

Anan, lokacin da wannan wakilin suna ya biyo bayan Kalmar da ta qare da gajeren wasali, wannan gajeren wasali kan koma dogo wajen lafazi, wato yakan tsawaita.

إذا جاء هذا الضمير بعد الكلمة التي تنتهي بحركة قصيرة تتحوّل هذه الحركة إلى حركة طويلة أي يتم تمديدها.

Misali:

1. Baaba + -naa → baabaanaa

أب + ي = أبي

2. Baaba + -taa → baabaataa

أم + ي = أمي

3. Audu + - naa → Auduunaa

عبد + ي = عبدي

4. Binta + - taa → Bintaataa

بنت + ي = بنتي

Yanayin tsawaita wasali ken an a muhallin mallaka. Yayin da kalma ta qare da wasali gajere kuma wakilin suna xan mallaka na ajin mutum na farko- naa/taa ya byo baya, wannan

gajeren wasali kan koma dogo a lafazi, kamar yadda muka gani.

هذا هو تطويل الحركة في سياق الملكية (الإضافة). عندما تأتي كلمة بحركة قصيرة ثم جاء بعدها ضمير الإضافة للمتكلم naa و taa هذه الحركة القصيرة تتحوّل إلى حركة طويلة في النطق كما رأينا.

Don haka, faxar wannan wasali da gajartarsa a wannan muhalli na mallaka ba daidai bane a Hausa.

ولذلك نُطْق هذه الحركات الطويلة بحركة قصيرة في سياق الملك (الإضافة) يُعتبر خطأً في الهوسا.

1. Baabanaa *
2. Baabataa*
3. Audunaa*
4. Bintataa*

<u>Tambayoyi:</u>

<u>أسئلة:</u>

1. Me ake nufi da tsawaita wasali?

- ما المراد بتطويل أو تمديد الحركة؟

2. Faxi abu guda da ke sharxanta tsawaita wasali a Hausa.
    - اذكر شرطا واحدا لتطويل أو تمديد الحركة.
3. Kawo misali game da wannan abu da ka ambata.
    - اذكر أمثلة على ما ذكرت.
4. Yi amfani da waxannan kalmomi cikin jimloli uku (3) daban-daban yadda wasulansu na qarshe za su tsawaita:
    - استخدم هذه الكلمات في ثلاث جمل مختلفة، بحيث تتحوّل الحركات إلى حركات طويلة.

(a) Baxi — العام القادم

(b) Tanko — تانكو

(c) Kaduna — كادونا

Gajarta Wasali: تقصير الحركة:

ya gabata mun bayyana yadda tsawaita wasali A abinda yake. Mun yi nuni da cewa lamarin ya shafi inda akan ja wasali ne gajere ya koma dogo a lafazi.

في الموضع السابق تناولنا كيفية تطويل الحركة. أشرنا إلى أنه يتعلق الأمر بطريقة تطويل الحركة القصيرة بحيث تصير حركة طويلة في النطق.

Dangane da haka kuma, mun yi nazarin muhalli biyu inda yake faruwa, wato muhallin tambaya da muhallin mallaka. A wannan babi kuma, zamu duba akasin tsawaita wasali. Wato gajarta wasali.

ونظرنا في ذلك إلى سياقين من بين السياقات التي يحدث فيها هذا ، يعني سياق الاستفهام وسياق الإضافة. وهنا سننظر إلى عكس تطويل الحركة يعني تقصيرها.

Kamar yadda muka ambata, gajarta wasali akasin tsawauta shi ne. Gajarta wasali lamari ne inda ake rage tsayin wasali dogo ya koma gajere a lafazi. Kamar tsawaita wasali kuma akwai muhalli biyu na musamman da haka ke faruwa. A nan ma kuwa zamu duba muhalli biyu ne kaxai. Na farko za mu duba lamarin a rufaffiyar gava,Na biyu kuma wajen samar da bayanau.

وكما ذكرنا، تقصير الحركة عكس إطالتها. وهو تغييرها من حركة طويلة إلى حركة قصيرة في النطق، ومثاله تطويل الحركة، أي أن هناك مواضع خاصة يحدث فيها هذا. وهنا يمكن أن ننظر إلى موضعين فقط، الأول: المقطع المغلق، والثاني صيغة تكوين الظرف.

A-Rufaffiyar Gava: المقطع المغلق:

Kamar yadda aka sani cewa cibiyar rufaffiyar gava wasali ne gajere. Don haka misali, idan kalma ta qare da dogon wasali (wato ta qare da buxaxxiyar gava mai cibiya dogon wasali). Sannan aka zo xafa wa wannan kalma madanganci-n/r, wannan dogon wasali take zai koma gajere. Duba waxannan misalai:

كما هو معروف أن المقطع المغلق حركته حركة قصيرة، ولذلك إذا انتهت كلمة بحركة طويلة مثلا (أي انتهت بمقطع مفتوح حركته طويلة) ثم أُلحِقَ بهذا المقطع أداة الإضافة (n/r) هذه الحركة تتحول على الفور إلى حركة قصيرة. انظر إلى الأمثلة:

1. Gidaa + n → gidan

بيت + n = البيت

2. Kiifii + n → kiifin

سمكة + n = السمكة

3. Riigaa + r → rigarsa

قميص + n = القميص

4. Yatsu + n → yatsun

أصابع + n = الأصابع

Haqiqa, in ka kwatanta wasalin qarshe na kowace kalma kafin xafa madangancin nan da lafazin wannan wasali bayan xafin, za ka fahimci gajarcewarsa.

بالتأكيد أنك إذا قارنتَ نطق هذه الحركات من كل كلمة قبل إلحاقها بأداة الإضافة مع نطقها بعد الإلحاق ستلاحظ تقصيرها.

Don haka, faxar wannan wasali da tsayinsa a wannan muhalli, wato cikin rufaffiyar gava ba daidai ne ba.

ولذلك النطق بهذه الحركات طويلةً في هذا الموضع أي مقطع مغلق يُعتبر خطأً.

1. Gidaan*
2. Kiifiin*
3. Rigaar*
4. Yaatsuun*

Ma'ana (1) daan* (BWWB) sai dai dan (BWB), (2) fiin* (BWWB) sai dai fin (BWB), (3) gaar* (BWBB) sai dai gar (BWB), (4) tssun* (BWWB) sai dai tsun (BWB).

يعني في المثال الأول daan* (BWWB)، والصواب dan (BWB)، وفي المثال الثاني fiin* (BWWB)، والصواب fin (BWB)، وفي المثال الثالث gaar* (BWBB) والصواب gar (BWB)، وفي المثال الرابع tssun* (BWWB)، والصواب tsun (BWB).

B- Wajen Samar da Bayanau:

تكوين الظرف

Bayan gajarta wasali a rufaffiyar gava ana gajarta shi wajen samar da bayanau. Bayanau dai kalma ce da ke bayyana aikatau a nahawu. Misali, a jimlar "ya zo jiya" jiya bayanau ce. A Hausa kusan duk sunayen sassan jikin mutum qarewa suke yi da dogon wasali, kamar a waxannan misalai:

وبعد تقصير الحركة في مقطع مغلق يتم أيضا تقصيرها في تكوين الظرف. والظرف كلمة توضح طريقة الفعل في النحو. مثال: "جاء أمس" فكلمة "أمس" ظرف زمان، وفي لغة الهوسا أكثر أسماء أعضاء جسم الإنسان حركاتها طويلة كما في هذه الأمثلة.

1. Qafaa — الرِّجل
2. Hannuu — اليد
3. Qwabri — الساق
4. Levee — الشفت
5. Idoo — العين

Amma kuma, yayin da aka zo mayar da waxannan kalmomi zuwa bayanau ta hanyar qara “a” ko “da” d.s a farko, dogon wasalin nan kan koma gajere. Misali:

ولكن إذا حُوِّلت هذه الكلمات إلى ظروف عن طريق زيادة الأداة ”a“ أو ”da“ وأشباهها في بدايتها تتحول هذه الحركة الطويلة إلى حركة قصيرة، مثال:

6. A qafa — في القدم

Da qafa — بالقدم

7. A hannu — في اليد

Da hannu — باليد

8. A qwabri — في الساق

Da qwabri — بالساق

9. A leeve — في الشفاة

Da leeve — بالشفاة

10. A ido في العين

بالعين Da ido

وذلك مثلا كما في قولنا: أصابه بجرح في قدمه، فبالتالي أصبحت عبارة "في قدمه" عبارة ظرفية مكانية.

A matsayinsu na bayanau, babu xaya daga cikin misalan nan na 6 zuwa na 10 da ke qarewa da dogon wasali. Haka lamarin yake. Duk wani suna na sashen jiki wanda ya qare da dogon wasali, wasalin nan kan gajarce in aka mayar da wannan suna zuwa bayanau.

في هذه الحالة (حالة الظرف) من البند (٦) إلى (١٠) لا يوجد أحد منها ينتهي بحركة طويلة. هكذا كان الأمر، كل عضو من أعضاء جسم الإنسان الذي ينتهي بحركة طويلة، تتحول الحركة من كونها طويلة إلى قصيرة إذا تم تحويلها إلى الظروف.

A gaba xaya, irin yadda ake gajarta wasali ke nan. Ana yin sa a rufaffiyar gava ko wajen samar da bayanau. Amma waxannan muhallai biyu na gajarta wasali ba su kenan ba. Waxannan dai kawai muka bayyana a wannan littafi.

عموما، يتم تقصير الحركات بهذه الطريقة، عن طريق مقطع مغلق أو تكوين الظرف، ولكننا بينّا هذين الموضوعين فقط في هذا الكتاب.

Tambayoyi:

أسئلة:

1. Mene ne gajarta wasali?

- ما هو تقصير الحركة؟

2. Faxi abu guxa da ke sharxanta gajarta wasali a Hausa.

- اذكر شرطا واحدا لتقصير الحركة في الهوسا.

3. Kawo misali game da wannan abu da ka ambata.

- اذكر مثالا لما ذكرت.

4. Yi amfani da waxannan kalmomi cikin jimloli uku (3) daban- daban yadda wasulansu na qarshe za su gajarce:

- استخدم هذه الكلمات في ثلاث جمل مختلفة، بحيث تتحوّل الحركات إلى حركات قصيرة:

(a) Jijiya عِرق

(b) Huhu الرئة

(c) Ciki البطن

Gajeren Wasali

الحركة القصيرة

- Ana samun sa a qarshen sunan mutum

وتوجد في آخر أسماء الأشخاص:

Awwalu	أول
Sani	ثاني
Binta	بنتا

- Qarshe sunayen garuruwa da jihohin Hausa yana da wasula gajeru, misali:

ويوجد في نهاية أسماء المدن والولايات "المحافظات" بلغة الهوسا بها الحركات القصيرة، مثل:

Kano	كانو
Zaria	زاريا
Tawa	تاوا
Sakkwatau	سوكوتو
Katsina	كشنه
Maraxi	مارادي

- Wasulan qarshe na sunayen shiyyoyi su ma gajeru ne

الحركات الواردة في نهاية أسماء الاتجاهات (مفردها جهة shiyya) هي أضا قصيرة.

Misali: مثال:

Kudu	الجنوب
Gabas	الشرق
Arewa	الشمال
Yamma	الغرب
Qasa	أسفل
Sama	أعلى
Hagu	يسار
Dama	يمين
Da dai sauransu.	وما إلى ذلك

Haka kuma wasulan qarshen kalmomi masu nuna yadda ake yin wani aiki ko halin da ake ciki, gajeru ne.

وكذلك الحال أيضا حركات نهاية الكلمات التي توضح كيفية أداء العمل، أو الحال الذي هو فيه أو عليه فهي قصيرة أيضا.

misali	مثال:
a sannu	مبطّئ- بطيئ
a kwance	محلول- مفكوك
mai sauri	مسرع
a tsaye	موقوف

Suma zarufan lokaci musamman na shekaru ko ranaku, suna da wasulan qarshe gajeru.

وكذلك أيضا ظروف الزمان "كلمات ظرف الزمان" خاصة كلمات السنين أو الأيام، فهي تنتهي بحركة قصيرة.

misali:	مثال:
bara	العام الماضي
bana	هذا العام
baxi	العام القادم
jiya	أمس
gobe	غدا
jibi	بعد غد
gata	بعد ثلاثة أيام
citta	بعد أربعة أيام

Gava: المقطع الصوتي:

Idan baqi da wasali sun haxu sunyi gava.

إذا اتحد الحرف الساكن مع الحركة، فإنهما يكونان مقطعا صوتيا واحدا.

Cikin kalma xaya ana iya samun fiye da gava xaya.

في الكلمة الواحدة من الممكن أن يكون هناك أكثر من مقطع.

misali: مثال:

In mun sanya gava cikin xaki, to, zamu sami kamar haka:

Yar	Je	Je	Ni	Ya	Yarjejeniya
1	2	3	4	5	اتفاقية

Gava biyar kenan cikin Kalmar: yarjejeniya

خمسة مقاطع هكذا في كلمة: اتفاقية yarjejeniya

Tsawon wasalin gava yana tasiri akan gavar baki xaya.

فطول حركة المقطع له تأثير قوي على المقطع بصفة عامة.

Watau, gavar kan zama doguwa ko gajera gwargwadon jan wasalin dake tare da ita.

أي أن المقطع ممكن أن يكون طويلا أو قصيرا بحسب طول "تطويل" الحركة الموجودة فيه.

misali: مثال:

kaji = kaajii – دجاج

doki = dookii -حصان

kura = kuuraa -ذئب

guru = guuruu -حزام جلدي عريض

kare = karee -كلب

haba = habaa – ويحك

barewa = bareewaa -غزال

jiva = jibaa -عش نمل صغير

Darasi na الدرس الثاني biyu:

Sunayen Nunau　أسماء الإشارة ('yan wa)

Sune: wannan, misali: wannan mutumin. هذا الرجل

Nan, misali: mutumin nan.
هذا الرجل

wancan, misali: wancan mutumin.
ذلك الرجل

wannan, misali: wannan matar.
هذه المرأة

can, misali: matar can.
تلك المرأة

waccan, misali: waccan matar.
تلك المرأة

waxannan, misali: waxannan mutanen.
هؤلاء الناس

waxancan, misali: waxancan fataken.
أولئك الناس

Jarurruka (Muf. Jarru) حرف الجر)　حروف الجر (المفرد):

في الحقيقة لا أتفق (البروفيسور صبري سلامة) مع النحاة الذين يستخدمون هذا المصطلح (حروف الجر سواء أكانوا نحاة هوساويين أو غيرهم) وذلك لأن لغة الهوسا لا تعرف نظام الجار والمجرور كما هو الحال في العربية الذي يتحدد فيها من خلال بعض علامات الإعراب: الكسرة والياء، كما في قولنا: يجلس في البيتِ، أو مررتُ برجلين، أو ذهبت إلى المعنيين بالأمر.

فالهوسا لغة ليست معربة وبالتالي ليس بها ما يمكن تسميته بعلامات الإعراب بما في ذلك العلامات الدالة على الجر. وبالتالي ما يمكن أن نذهب إليه ونراه صحيحا هو أن نطلق على هذه المفردات اسم (كلمات أو أدوات مساعدة) وهي التي تخلو من المعنى في ذاتها ولا يتحدد معناها إلا من خلال إدراجها في سياق مع كلمات أخرى.

Misalin su sune: a, wa, ma, ga, gare,

مثالها: الباء- اللام- على

Da, daga, banda, sai,

مع- من- سوى- إلا

Cikin, wajen, saboda, garin,

في- عند- لأن (السبب) - كي

Akan/kan, abakin, maimakon,

على- جانب- بدلا من

Bigiren/bagiren, gaban, bayan,

عند- أمام- خلف

Qarqashin, bisan/bisa, tsammanin,

تحت- فوق- رجاء (ظنا)

Tsakanin, tsakar/tsakan, zuwa

بين- وسط- إلى

cikin ibarori: Mu bada misalan waxansu a

Agida, a tudu, a ruwa, gaya masa, faxa mata, gaya ma Audu, ka gaya wa, zafin zuciya ga Audu, zafin zuciya gareshi, ni da ita tare da su, mai yin wannan aiki sai shi.

لنضرب بعض الأمثلة ببعضها في عبارات (تراكيب): بالبيت، في البر، في البحر، قُل له، قُل لها، قل لعبده، لعبده سرعة الغضب، عبده لديه سرعة الغضب، أنا معها، معهم، ليس هناك من يقوم بهذا العمل إلا هو.

Faxakarwa:

ملاحظة:

Kalmar “da” ana amfani da ita a halaye da dama, misali:

تستخدم كلمة "da " في حالات كثيرة، منها:

1. “Da” axafi ne kuma zarfi ne: da in yi sata gwamma in mutu da yunwa.

- حرف عطف أو ظرف: لأن أموت جائعا أحب إلى gwamma من أن أسرق.

2. “Da” lamirin dagantaka ne: mutumin da ya zo.
- اسم الموصول: الرجل الذي جاء.

3. “Da” na bayyana mallaka: suna da kaya da yawa.
- حرفٌ يوضح الملكية : لهم بضاعات كثيرة.

4. “Da” na zuwa gabanin sunaye har a sami sifofi ko zarufa: da sauqi, da dama, da sannu, da wuri.
- ويأتي قبل الأسماء ليفيد الصفة أو الظرف: برخصة، بكثرة- كثيرا، بطيئا، بهدوء، مبكرا.

5. “Da” na zuwa bayan fi’ilai a sami fi’ilan musabbabi: bayyanar da, jefar da, watsar da, mayar da, miqar da.
- يأتي بعد الأفعال ليفيد التعليلfi’ilan musabbabi : ليبيّنَ، لينبذَ، ليرميَ، ليجعلَ، ليمدَّ.

<u>Axafofi (Mahaxai):</u> <u>حروف العطف:</u>

Irinsu su ne misali:

Amma, kuwa, daxa, kuma, ma, in, idan, kur, kadan, ko, kada, tamkar, kamar fa, dai:

ومثالها ما يلي:

أما- لكن- الواو- الفاء- إن- إذا- لئن- أو- مثل- الكاف- أيضا.

To da yake mahaxai suna wuyar ganewa yadda suke a nan sama su kaxai a rarrabe za mu yi amfani da su cikin ibarori domin mu fahimce su sosai, misali:

بما أن حروف العطف يصعب إدراكها كما وردت أعلاه متفرقة وحدها، فإننا سوف نستخدمها في عبارات (تراكيب) حتى نتفهّمها جيدا. مثل:

Kai da Ali	أنت وعلي

Da nonon wuri da na wuri xari duk farin su xaya.

لون لبن ما ولون ألبان مائة أماكن سواء في البياض. (هذا مثل شعبي يشير إلى الأصالة، فمهما تغيرت الأوضاع فالأصيل أصيل لا يتغير، وهذا ما يشير إليه المثل بأن لون اللبن أبيض ناصع البياض، مهما كان المكان الذي هو فيه ومهما تعددت أماكنه)

Jeka gida amma ka dakata sai na iso.

اذهب إلى البيت لكن انتظر حتى آتي.

Babanka zai zo da yamma.

سيأتي أبوك في المساء.

Ita kuwa tsohuwarka sai gobe da safe ne zata zo.

أما أمك فإنها ستأتي صباح الغد.

Ni kuma/kuwa zamu sadu da su gobe da rana.

وأنا سوف ألتقي معهم نهار الغد (غدا نهارا).

Kai ma sai gobe zaka gansu su duka.

وأنت أيضا لا تقابلهم إلا غدا.

In/idan sun zo ka share musu dakin can.

إذا جاءوا فنظف لهم تلك الغرفة.

Kur/kada ka ki yin abin da na ce ks yi zan mare ka.

إذا لم تفعل ما أمرتك فسوف أُشبعك لطما.

Ko ka so ko ba ka so ba naje can.

شئتَ أم أبيت ذهبتُ إلى هناك.

Kada kaje mana.

فلا تذهب.

zan sallame ka. Koda ban gama ba

سوف أصرفك حتى لو لم أنته.

Nayi haka don taimako.

فعلت ذلك للمساعدة.

Kayi tamkar yadda/kamar yadda yayi.

افعل كما فعل- افعل مثلما فعل.

zan yi ba. Ni fa ba

أما أنا فلا أفعل.

yi dai gwargwadon iyawarka. Ka

افعل قدر استطاعتك.

Motsa Rai: أسلوب التعجب

Ana motsa rai saboda ta'ajjubi (wato mamaki) na jin xaxi ko jin ciwon wani abu. Akan ce misali:

علامات الدهشة أو التعجب تظهر نتيجة للانفعالات العاطفية (فرح أو حزن أو خبر مفاجئ) ولها كلماتها التي تعبر عنها. فيقال مثلا:

Um!	اممم!
haba!	والله ! حقا !
madalla!	نِعم الشيء ! أيوا!
ar!	أررر !
tir!	تبا !
assha!	يا للعار !
aha!	أها !
Af/ap!	أَف !
oho!	آه !
kai!	يا !
ya!	يا !

wai! يا (يا خبر) !

<u>ضمائر الملكية:</u> <u>Wakilan Mallaka</u>

وفيما يلي شرح موجز للضمائر الملكية:

تنقسم الضمائر الملكية إلى قسمين: الضمائر المتصلة والضمائر المنفصلة- الضمائر المتصلة: تشير إليها العلامة n والتي تقع رابطة إضافة بين الشيء المملوك والضمير المراد إسناد الملكية إليه إذا كان الشيء المملوك مذكرا، كما في:

Gida+ n+ na= Gidana

Gida+ n+ka= Gidanka

Gida+n+ku= Gidanku

أما إذا كان الشيء المملوك كلمة مؤنثة في الهوسا، فتكون رابطة الإضافة "r"والتي تأتي في نفس الموقع السابق الإشارة إليه، وذلك:

Riga+ r+ka= Rigarka

Riga+r+ki= Rigarki

Riga+r+su= Rigarsu

وفي حالة إسناد الملكية إلى الاسم مباشرة إسنادا إضافيا، كما في:

Gida+n+ Ali= Gidan Ali بيت علي

تجري الصيغة بنفس الطرق السابقة حيث التغيير الوحيد الذي يحدث هو إحلال الاسم محل الضمير، كما في:

Gida+n+ na+ Huzaifah= Gida na Huzaifah بيت حذيفة

وهنا تُستسنَى رابطة الإضافة في حال إسناد ملكية الشيء المفرد المؤنث إلى ضمير المفرد المتكلم، كما في:

Riga+ t+ ta= Rigata

Mama+ t+ ta= Mamata

أما في حالة ما إذا كان الشيء المملوك جمعا فتكون رابطة الإضافة "n" وذلك كما في:

Mata+ n+ na= Matana زوجاتي

Riguna+n+ku= Rigunanku أثوابكم

Gidaje+n+su= Gidajensu بيوتهم

أما ضمائر الملكية المنفصلة فيتم التعبير عنها باستخدام أحد الأداتين: "Na"أو "ta"، كما في:

Gida+ na+ka= Gida naka

Gida+na+shi= Gida nashi

Gida+ na+ mu= Gida namu

Riga+ta+ka= Riga taka

Riga+ta+ta= Riga tata

Riga+ta+su= Riga tasu

أما بالنسبة لهذه الصيغة مع المفرد المتكلم فهناك تغيير يحدث يتمثل في تغيير الضمير من na إلى wa، كما في:

Gida+ na+wa= Gida nawa

Riga+ta+wa= Riga tawa

أما بالنسبة لصيغة الجمع فتتوحد الرابطة حيث تكون "na"، كما في:

Mata+na+wa= mata nawa زوجاتي

Gidaje+na+wa= Gidaje nawa بيوتي

الدرس الثالث | Darasi na uku:

النغمة: Karin Murya (Karin Sauti)

النغمة هي عبارة صورة صوتية معينة تصاحب نطق الكلمة، وهي ما تعرف اصطلاحا لدى اللغويين باسم "tone"، ولها وظيفتها الصرفية والدلالية، ومثال على ذلك كلمة mata فعندما يكون التون أو تكون النغمة منخفضة على الحركة الأولى هكذا: màta تكون بمعنى "امرأة- زوجة" وعندما تكون مرتفعة على الحركتين الأولى والصانية هكذا:mátá فإنها تكون "نساء"- زوجات" وبالتالي فإنها قامت بوظيفة صرفية حيث غيرت معنى الكلمة وحولتها من مفرد إلى جمع.

ومن ذلك أيضا مع نفس الكلمة، حينما تكون الحركة الأولى قصيرة مع نغمة مرتفعة، والثانية قصيرة مع نغمة منخفضة، هكذا: فإنها تدل على معنى الجر "لها".

ومن ذلك أيضا، كما في كلمة "matashi" فإذا كانت الحركة الأولى قصيرة وعليها نغمة مرتفعة والثانية طويلة مع نغمة منخفضة هكذا: matashi كانت الكلمة بمعنى "شاب- مراهق- يافع" مع التنبيه إلى أن الحركة الأخيرة أيضا "i" ذات نغمة مرتفعة وهي حركة طويلة، أما إذا كانت الحركة الأولى قصيرة وذات نغمة مرتفعة، والثانية طويلة ونغمة مرتفعة، والثالثة طويلة ونغمة مرتفعة أيضا هكذا: ، فإن الكلمة تكون بمعنى "مخدة الرأس- وسادة".

ومن ذلك أيضا فيما يتعلق بالوظيفة الصرفية، كلمة "matsala" بمعنى "مسألة – أمر – مشكلة" إذا كانت النغمة على الحركة الأولى منخفضة والحركة قصيرة والحركة الثانية قصيرة وذات نغمة مرتفعة،

والحركة الأخيرة طويلة والنغمة منخفضة هكذا: كانت الكلمة كما ذكرنا بمعنى "مسألة – أمر – مشكلة" أما إذا كانت النغمة على الحركة الأولى مرتفعة والحركة قصيرة والثانية كذلك مرتفعة وحركة قصيرة، والثانية طويلة ونغمة مرتفعة، والرابعة طويلة ونغمة مرتفعة هكذا: فإنها تدل على الجمع أي "مسائل- أمور- مشاكل".

وحول النغمة Karin murya والتي تعرف بـ Karin sauti، يقول بعض نحاة الهوسا:

Aikin Karin murya bambantawa ne.

وظيفة النغمة هي التمييز "بين المفردات من حيث المعنى"

Kuma cikin kalma ana iya samun kare- Karen murya da dama.

وأيضا يمكن أن يكون هناك في الكلمة الواحدة نغمات متعددة.

Kare-karen murya sun kasu kasha uku:

وتنقسم النغمة إلى ثلاثة أنواع:

- Na sama (s)
- Na qasa (Q)
- Mai faxowa (f)

- نغمة مرتفعة، ويرمز لها كتابيا بالحرف (s)
- نغمة منخفضة، ويرمز لها كتابيا بالحرف (q)
- نغمة هابطة، ويرمز لها كتابيا بالحرف (f)

والعلاقات الدولية المتعارف عليها لدى اللغويين والتي تشير إلى نوع النغمة، هي:

وتدل على النغمة المرتفعة (á)

وتدل على النغمة المنخفضة (à)

وتدل على النغمة الهابطة (â)

وأكثر النغمات ورودا في اللغة هي النغمة المرتفعة، والنغمة المنخفضة.

Akan rubuta su akan wasula

وعادة ما تكون التغمة فوق الحركة، أي لا علاقة لها بالحروف الساكنة.

Karin murya yakan bambanta kalmomin da suke kama da juna ta fuskar rubutu.

النغمة عادة ما تقوم بالتمييز بين الكلمات التي تتشابه مع بعضها البعض من ناحية الكتابة.

مثال:

misali:

A-Sànyà (fi'ili ne) فعل بمعنى يرتدي- يجمع

- Sányà (sunan itaciya wadda kuma ake kira uwar magunguna).

- اسم شجرة والتي تعرف بأم الدواء، أو أم الأدوية، وتستخدم في العلاج بالأعشاب.

B- Fára (watau soma, fi'ili ne)

(فعل بمعنى يبدأ- بدأ).

- Fàrá (sunan wani qwaro mai varna a gonaki)

(اسم حشرة ضارة بالحقول – جراد)

C-Súmá (fi'ili)

فعل بمعنى "يغمي عليه – يغشي عليه"

- Sùmá

اسم بمعنى "شعر الرأس الجميل"

Karin murya yana bambanta fasulan nahawu.

التون يميز التقسيمات النحوية.

misali: مثال :

In mun xauki misali- lamarin gabannin fi'ili "ya", to, zamu ga kare- Karen murya za sub a shi ayyuka da ma'anoni iri daban- daban. Misali:

إذا أخذنا على سبيل المثال- الضمير الفعلي "ya" سوف نرى أن النغمات تعدد من مهامه وتعطيه معان مختلفة، كما في:

ya zo jiya   جاء بالأمس

وهذا يدل على الزمن الماضي التام.

Babban lokaci shuxaxxe ko cikakke.

- Ya zo gobe (wataqila ya zo) lokacin zuwa gaba na biyu

سيأتي غدا (ربما سيأتي غدا) وهذا في الزمن المستقبل الثاني.

- Na ce ya zo (sigar fata ko umarni)

قلت فليأت (صيغة التمني أو الأمر).

Zamuyi bayani anan akan Karin sauti.

سوف نبين هنا بالتفصيل مفهوم النغمة الصوتية .

Harshen Hausa kamar mafi yawancin harsunan Afirka, yana yin amfani da Karin sauti.

لغة الهوسا كغيرها من كثير من اللغات الأفريقية، تستخدم النغمة الصوتية.

Me ake nufi da Karin sauti? Karin sauti kaifin sauti ne na murya dangane da yadda ake faxar kowace gava ta kalma bisa qa’ida don isar wa mai sauraro ma’anar wannan kalma ta sosai da sosai.

ما هي النغمة الصوتية؟ النغمة الصوتية هي حدة الصوت بالنسبة لطريق النطق بالمقاطع في الكلمة على قاعدة، لإفهام المستمع حقيقة معنى هذه الكلمة كما هي.

Don haka, kowace gava tana da nata irin kaifin muryar, ko Karin sauti.

ولذلك، فإن لكل كلمة النظام الصوتي الخاص بها، أو النغمة الصوتية.

Wasu gavovin ana faxar su ne da kaifin sauti mai yin sama, wasu kuma da mai yiwowa qasa. Faxi waxannan kalmomi na qasa cikin tsanaki tare da lura da kaifin sautin muryarka bisa kowacce:

بعض المقاطع تُنطَق بنغمة مرتفعة، وبعضها بنغمة منخفضة. حاول أن تنطق بهذه الكلمات الآتية في هدوء مع مراعاة نغماتك الصوتية فيها:

A	B
Suna	Abu
Kifi	Mace
Madara	Ayaba

Haqiqa, za ka ji cewa yayin da ka faxi kowace gava ta Kalmar rukunin A da kaifin sauti mai yin sama (duk cika da kaifin sauti mai yin sama).

طبعا، تلاحظ أنك أثناء النطق بكل كلمة من البند (أ) استخدمت النغمة المرتفعة (كلها بنغمة مرتفعة).

Kowace gava ta rukunin B faxin ta ka yi da kaifin sauti mai yiwowa qasa (duk cika da kaifin sauti mai yiwowa qasa).

وكل كلمة من البند (ب) نطقتها بنغمة منخفضة (كلها بنغمة منخفضة).

Gavar da aka faxe ta da kaifin murya mai yin sama, akan ce tana da Karin sautin sama. Wadda aka faxe ta da kaifin sautin murya mai yiwowa qasa kuma, tana da Karin sautin qasa.

المقطع المنطوق بصوت مرتفع، يقال إنه ذو نغمة مرتفعة. والذي نُطِق بصوت منخفض، يقال إنه ذو نغمة منخفضة.

Yadda zaka rarrabe tsakanin Karin sautin sama da na qasa cikin sauqi, sau da yawa yin fito da baki yakan taimaka. Don haka yayin da ka yi fiton faxar kowace gava ta kalmomin misalan nan namu na baya wataqila za ka fi lura da bambancin da ke tsakaninsu cikin sauqi.

وكثيرا ما يساعد الصفير بالفم (المد) في التعرف على كيفية التفريق بين النغمة المرتفعة والمنخفضة. ولذلك لو صفرت (مددت) في أثناء النطق بالمقاطع في كلمات الأمثلة السابقة لربما تتأمل الفرق بينها أكثر في السهولة.

Sautin fiton da akan yi a Karin sautin sama siriri ne in aka kwatanta shi da wanda akan yi a Karin sautin qasa, wanda yake kakkaura.

صوت الصفير (المد) الصادر من النغمة المرتفعة رقيق في حالة مقارنته بالذي يصدر من النغمة المنخفضة الذي يكون غليظا.

Amma kuma, lalle ne mu qarfafa cewa kalma mai gava fiye da guda ba koyaushe ne take da Karin sautin sama duk gava xaya ba, ko kuma Karin sautin qasa. Za ta iya haxa biyun gaba xaya. Faxi waxannan kalmomi a tsanake tare da lura da kaifin sautin muryarka bisa kowace gava:

ولكن، لا بد من التأكد أن الكلمة ذات المقاطع (أكثر من مقطع) لا تأتي دوما بالنغمات المرتفعة في جميع المقاطع، أو النغمات المنخفضة. قد تجمعهما معا. انطق بهذه الكلمات بهدوء مع مراعاة نغماتك الصوتية في كل مقطع:

1. Hula — قلنسوة
2. Hanya — الطريق- الدرب
3. Bulala — السوط- الجلدة
4. Shugaba — أمير- رئيس

5. Ciniki البيع

Zaka ji cewa dangane da kalma ta 1, hula, kaifin sautin da ke kan gavar farko “hu” qasa ya yiwo, wanda ke kan gava ta biyu kuma “la” sama (Q.S): Kalmar hanya kuma, sama da qasa (S.Q): bulala, sama sama sannan qasa (S.S.Q): shugaba, qasa qasa sannan sama (Q.Q.S) a qarshe kuma Kalmar ciniki, qasa sama sama (Q.S.S).

تلاحظ أنه في الكلمة الأولى hula (قلنسوة)، نغمة الصوت التي في المقطع الأول "hu" انخفضت، والتي في المقطع الثاني "la" ارتفعت. وكلمة "hanya" (الطريق) مرتفعة ومنخفضة، وكلمة "shugaba" (رئيس- أمير) منخفضة، منخفضة ثم مرتفة، وكلمة "bulala" (السوط- الجلدة) مرتفعة، مرتفعة ثم منخفضة، وكلمة "ciniki" (البيع) منخفضة، مرتفعة ثم مرتفعة.

Bayan Karin sautin sama da na qasa waxanda kowannen su ke hawa kan gava guda a lokaci guda, akwai inda ake samun haxuwar biyun a wannan jeri kan gava guda.

وبعد النغمة المرتفعة والمنخفضة اللتين تأتيان في المقطع من الكلمة في الوقت الواحد، وهناك أماكن يوجد اجتماع النغمتين معا في مقطع واحد.

ce da shi Harxaxxen Wannan kaifin sautin murya ana Karin sauti ko Karin sauti faxau. A nan, kaifin sautin yakan yi sama ne da farko sannan kafin ka ce kwabo ya yiwo qasa. Faxi

waxannan kalmomi a tsanake tare da lura da kaifin sautin muryarka bisa kowacce:

ويسمى هذا النوع من النغمة النغمة المتشابكة أو النغمة الهابطة. وهنا يبدأ صوت النغمة يرتفع في أول الأمر وقبل أن تقول قرشا (وقبل لمحة البصر) ينخفض. انطق بهذه الكلمات بهدوء مع مراعاة نغماتك الصوتية في كلها:

1. Su — هم
2. Mai — زيت
3. Zobban — الخاتم
4. Rassan — الغصون- الفروع
5. Yaran — الأولاد- الأطفال

da Zaka ji cewa yayin faxar kowace gava, muryarka ta fara kaifin sauti mai yin sama sai nan da nan kuma ta yiwo qasa. Ma'ana, kowace gava tana da Karin sauti faxau. Kwatanta yadda ka faxi waxannan kalmomi da yadda ka faxi na misalan baya. Haqiqa, bambancin a bayyane yake.

ستلاحظ أنه في حين النطق بكل مقطع، يبدأ صوتك بنغمة مرتفعة ثم بعد ذلك مباشرة تنخفض. يعني لكل مقطع نغمة هابطة. قارِن كيف نطقت بهذه الكلمات وكيف نطقت بالأمثلة السابقة التي قبلها. بالطبع، نجد الفرق ظاهرا.

Amma kuma, Karin sauti faxau, kamar sauran biyun, ba koyaushe ne yake zuwa gaba xaya ba a kalma mai gava fiye

da guda. kamar za ta iya qunsar gavovi masu Karin sauti iri daban- daban. Faxi waxannan kalmomi:

ولكن، النغمة الهابطة كغيرها من النغمات المرتفعة والمنخفضة، أي لا تأتي دوما في جميع المقاطع من الكلمة ذات المقاطع الكثيرة . انطق بهذه الكلمات:

1. Mutum — الإنسان
2. Manja — زيت أحمر
3. Jarrabawa — الامتحان

Za ka ji cewa a kalma ta 1, mutum, Karin sautin gavar ta farko na qasa ne, faxau kuma a gava ta biyu (Q.F): a kalma 2, manja, faxau na a gavar farko na sama kuma a ta biyu (F.S): kuma a jarrabawa, kalma ta 3, Karin sautin sama ne, sai na qasa sai faxau, sannan wani Karin sautin na sama (S.Q.F.S).

ستلاحظ أنه في الكلمة الأولى، "mutum " نغمة المقطع الأول مرتفعة، والمقطع الثاني نغمته هابطة، وفي الكلمة الثانية "manja " نغمة المقطع الأول هابطة، والثانية مرتفعة، وفي كلمة jarrabawa الثالثة، نغمة مرتفعة ثم منخفضة ثم هابطة ثم مرتفعة.

Ba a nuna Karin sauti a hanyar rubutun yau da kullum. Wannan yana daga cikin dalilan da ya sa ake samun wahalar koyon sa. A wajen koyar da Karin sauti ga makoyi akan yi

amfani da wasu alamomi na musamman don sauqaqa fahimta. Waxannan alamomi su ne: (á) a matsayin karin sautin sama, (à) a matsayin Karin sautin qasa, sai kuma (â) a matsayin Karin sauti faxau.

لا يُشار إلى علامة النغمة الصوتية في الكتابة العادية. وهذا من الأدلة التي تجعل تعلّم الكتابة بالحرف اللاتيني أن يكون صعبا. ولكن تُرسم العلامة في حين تعليم الدارس، حيث تستخدم علامات معينة لتسهيل الفهم. وهذه العلامات هي: (á)علامة للنغمة المرتفعة، (à) علامة للنغمة المنخفضة، (â) علامة للنغمة الهابطة.

Bisa al'ada, kowace alama ta Karin sauti na gava ana sanya ta ne a saman cibiyar wannan gava, kamar a waxannan misalai da muka rigaya muka bayar a baya:

وعادةً، توضع كل علامة للنغمة الصوتية فوق آخر المقطع ، كما في هذه الأمثلة السابقة.

Súná (S.S) الاسم

Àyàbà (Q.Q.Q)الموز

Hányà (S.Q)الطريق

Sû (F)هم

Járràbáwá (S.Q.F.S)الامتحان

Karin sauti yana da mahimmanci ainun a Hausa. Makoyi Hausa dole ne ya yi qoqarin faxar kalmomin sosai dangane da Karin sautin kowace gava na sosai. Canjin Karin sauti kaxan, kamar daga na sama zuwa na qasa, ko daga faxau zuwa Karin sautin sama, zai iya canja ma'anar kalma ko ma ya zamo da ita maras ma'ana sam.

للنغمة أهمية بالغة في الهوسا. لا بد لدارس الهوسا أن يحاول (يحاكي) نطق الكلمات كما هي من حيث النغمات الصوتية. لأن تغيير نغمة صوتية قليلا، من مرتفعة إلى منخفضة مثلا أو من هابطة إلى مرتفعة قد يؤدي إلى تغيير المعنى، أو إلى الإخلال بالمعنى (تكون عديمة المعنى).

Faxi waxannan kalmomi da sabon tsarin Karin sautin da aka dangana su da shi:

انطق بهذه الكلمات بأسلوب جديد للنغمة الصوتية المنسوبة إليها:

(F. Q) Sûnà

(Q. F) Hànyâ

(S) Sû

Yanzu kalmomi biyu na farko (suna) da (hanya) suna da wata ma'ana a Hausa? Haqiqa, za ka ce a'a, mene dalili? Domin suna bisa tsarin sautin wanda ba daidai ba. Yaya kuma

kalma ta qarshe su? Tana da wata ma'ana? A take za ka ce I. mene ne dalili? Domin kalma ce ta wakilin suna a harshen.

فهل للكلمتين الأوليين (suna) و (hanya) معنى؟ في الحقيقة تقول لا، فما الدليل إذًا ؟ لأنها على نغمات صوتية غير مناسبة. فكيف للكلمة الأخيرة؟ هل لها معنى ؟ تقول على الفور نعم. فما الدليل؟ لأنها تكون – بهذه النغمة- ضمير من الضمائر الشخصية في اللغة.

Yana da muhimmancin gaske a lura da Kalmar su (da Karin sauti faxau) da kuma su (da Karin sautin sama) a misali da muka bayar. Haqiqa, wannan yana nuna cewa Karin sauti kan rarrabe tsakanin kalmomi masu kama da juna a rubuce. Domin a nan, kalmomin nan biyu suna matsayin zubin kamantau ne.

إنه لذو أهمية كبيرة أن نلاحظ كلمة "su " (بنغمة هابطة) و "su " (بنغمة مرتفعة) في الأمثلة المتقدمة. في الحقيقية هذا يشير إلى أن النغمة الصوتية تميز بين الكلمات ذات الهيئات المماثلة في الكتابة. لأن هاتين الكلمتين بمثابة كلمات مماثلة.

Duba wasu misalan:

انظر إلى هذه الأمثلة:

1. Mákárántá (S.S.S.S) المدرسة

Mákàràntá (S.Q.Q.S)القرّاء

2. Máráyá (S.S.S) المدينة

Màráyà (Q.S.Q)اليتيم

3. Kâi (F) الرأس

Kái (S)أنتَ

4. Ràuní (Q.S) الجرح

Ráuní (S.S) الضعف

5. Gúgà (S.Q) المسح- الكي

Gùgá (Q.S)الدلو

Wani abin sha’awa kuma game da Karin sauti shine, a misalanmu na farko-farko mun nuna inda Karin sauti iri guda ke iya hawa kan dukkanin gavovin kalma guda, mis. Suna (S.S), mace (Q.Q), yaran (F.F). to wannan lamari bai tsaya ga kalma ba kaxai.

والمثير للدهشة حول النغمة الصوتية هو، في الأمثلة السابقة الأولى أشرنا إلى حيث يمكن للنغمة أن تأتي في جميع مقاطع الكلمة. مثل: "Suna" (الاسم) و "mace" (المرأة) و "yaran" (الأولاد)، فهذا الأمر لم يتوقف في الكلمات فقط.

Akan sami jimla suktum da Karin sauti iri guda, ko na sama, ko na qasa ko faxau, kamar yadda zamu misalta:

بل يمكن أن نجد جمل كاملة بنغمة صوتية واحدة، مرتفعة أو منخفضة، أو هابطة، كما سنثمل لها:

(a) Jimla da Karin sautin sama duk cika:

1. ‘yán mákárántá sún kómó gídá
2. Gidán sárkí yá fí kúsá

أ- الجملة ذات نغمة صوتية مرتفعة كلها:

- رجع الطلاب إلى البيت
- بيت الأمير قريب

ب-الجملة ذات نغمة صوتية منخفضة:

- خذ الموز من كافانشان
- أللى و أمالى في إبادن

(b) Jimla da Karin sautin qasa duk cika:

1. Gà àyàbà dàgà Kàfànchàn
2. Dà àlàlà dà àmàlà à Ibàdàn

ت-الجملة ذات نغمة صوتية هابطة:

- اليوم كان الزيت الأحمر فاسدا
- سأعطي الخاتم للأولاد

(c) Jimla da krin sauti faxau duk cika:

1. Yâu mânjân bâ kyâu
2. Yârân zân bâ zobbân

Mun ga yadda Karin sautin yake, abu mai matuwar mahimmanci a Hasua. Akwai Karin sauti iri uku a Hausa kamar yadda muka gani, wato Karin sauti sama da na qasa da kuma faxau.

رأينا حقيقة النغمة الصوتية، أمر مهم في الهوسا. وهناك ثلاثة أنواع للنغمات الصوتية في الهوسا كما رأينا، أي نغمة مرتفعة و نغمة منخفضة ونغمة هابطة.

Kowace gava ta kalma da Karin sautinta. Abin daya rage yanzu shine, mu rufe wannan bayanin da kawo wani xan yankin labari mu nuna Karin sautin dake cikinsa. Wannan muhimmin abu ne domin zai yi taimako sosai alokacin da mutum ya zo yin gwaji da kansa:

ولكل مقطع من الكلمة نغمته. والذي تبقى لنا الآن هو أن نختتم هذا البيان بذكر قطعة صغيرة (من القصة) ونشير إلى النغمات الصوتية فيه. هذا أمر مهم لأنه سيساعد كثيرا إذا جاء الإنسان مرحلة التطبيق بنفسه.

“Ín ákà táshì wânnàn gàrí, àkwái wání bàbbán kógí ánà fítò à cíkínsà. Àcán múkà dáidáità ábìn dà zà mù bíyá à físshé mù dà káyánmù dá dábbóbínmu. Jírágên kánáná né, bá sú xáukàr àbín dà yáfì káyán jákí gùdá dà rábì, mútàné kúmá bá sú wúcè úkù, bán dà mài túqì. Tá hákà ákà yí tá qétàrêwà dà mú, á kái à zúbè á kómó á kwáshì wáxánsú.

إذا جاوزت هذا البلد، هناك بحر كبير، يُصفر فيه (يحدث فيه صوت الصفير). وهناك اتفقنا فيما سندفع (أجرا) مقابل العبور بنا - físshé mù نحن وبضاعاتنا ودوابّنا. والسفن صغيرة، لا تحمل ما يجاوز حِمل حمار ونصف الحِمل، والناس لا يجاوزون ثلاثة فضلا عن السائق. وبهذه الطريقة عبرنا، وأُنزِل بنا ثم أُرجع ليأخذ الآخرين.

Tambayoyi:

أسئلة:

1. Mene ne Karin sauti?

أ- ما هي النغمة الصوتية ؟

2. a) Karin sauti iri nawa ne a Hausa?

b) Kawo su.

ب- كم أقسام النغمات الصوتية في الهوسا؟

- اذكرها

3. Kawo tsarin Karin sautin waxannan kalmomi, ta yin amfani da su a matsayin S, na gava mai Karin sautin sama. Q, na mai Karin sautin qasa da kuma F, a matsayin na gava mai Karin sauti faxau.

- اذكر نوع النغمة الصوتية للكلمات الآتية الارتفاع والسقوط والهبوط.

a- Yau (اليوم)　　　　yau (ريق- لعاب)

b- Bashi (قرضٌ)　　　　bashi (رائحة كريهة مُنْتِنَة)

c- Matashi (مخدة- وسادة)　　matashi (الشاب)

4. Nuna Karin sautin kowane gavar kalma ta wannan yankin labari, ta yin amfani da alamomin bambance karin sautin sama da na qasa na na faxau:

- بين نغمة كل مقطع من الكلمات الواردة في هذه القطعة، باستخدام علامات التمييز بين النغمة المرتفعة والمنخفضة والهابطة:

"Da muka tashi daga nan, ba mu tsaya ba sai a bisa Kadarkon London. Tun da farko ban gaya maku ba cewa Birnin London fa gari ne na bakin teku, saboda haka birnin kansa kamar tasha ce ta jirgin ruwa, wato yadda Ikko take a Najeriya.

"ولما أقلعنا من ثَم، لم نتوقف إلا عند أعتاب "لندن". لم أخُبركم من البداية أن مدينة " لندن" مدينة مطلة على شاطئ البحر، ولذلك كانت المدينة مثل الميناء، مثل إكُّو (لاجوس) في نيجيريا.

الدرس الرابع: Darasi na huxu:

Sifofi: الصفات:

Yana qunshe da waxannan abubuwan:

ويحتوي على الموضوعات الآتية:

Mene ne sifofi? ما هي الصفات؟

Yaya suke a nahawu? ما هي ماهيتها في النحو؟

Bayanin sifofi: توضيح
الصفات

Muna iya cewa sifofi, jam'i ne na sifa (sf).

يمكن أن نقول إن الصفات جمع صفة، وترمز لها اختصارا بالرمز (sf).

Kuma sifa kalma ce da ake amfani da ita a bayyana suna.

وأيضا الصفة هي كلمة تستخدم من أجل توضيح "إظهار الاسم"

Wannan bayani, na iya jivintar kyau ko muni ko inganci ko naqasa ko wasu abubuwa daban.

وهذا التوضيح يمكن أن يظهر "يتولى jivintar" صفات الجمال أو القبح أو الصحة inganci أو النقص أو العلة أو أشياء أخرى مختلفة.

Misali, idan muka xauki Ali, wanda yake suna ne na yanka, watau Ali ko Ahmad muna iya qara bayani akansa, kamar haka:

فعلى سبيل المثال إذا ضربنا مثلا (أخذنا) عليا الذي هو عبارة عن اسم علَم، أي "علي" أو "أحمد" ويمكن لنا أن نزيد الشرح فيه هكذا:

A-Ali baqi ne (anan, baqi na bayyana launin jikin Ali)

علي أسود (فكلمة أسود هنا هي التي تظهر لون جسد علي)

B- Ahmad siriri ne (siriri na bayyana siffar jikin Ahmad na rashin qiba)

أحمد نحيف (صفة نحيف توضح أن جسد أحمد غير سمين)

C- Ahmad dogo ne (dogo na bayyana siffar tsayin Ahmad)

أحمد طويل (كلمة طويل توضح صفة طول أحمد)

D- Ali qaqqarfa ne (anan kuma qaqqarfa na bayyana mana baiwar da Allah yayi masa na rashin ragwanci)

علي قوي "شجاع" (هنا أيضا كلمة قوي أو شجاع تظهر النعمة أو الهبة التي منحها له الله وهي عدم الجبن أو الخوف"

E- Ali kyakkyawa ne (nan kuma, irin siffar Ali kenan mai ban sha’awa, son kowa qin wanda ya rasa

علي جميل (هنا أيضا تم وصف علي بأنه مثير للإعجاب، محبوب لدى الكل (الجميع) (يرفضه) الذي افتقده.

F- Tanimu mahaukaci ne (anan kuma, ana siffanta mana Tanimu ne dangane da rashin hankalinsa ko gushewar hankalinsa)

تنيمو مجنون (هنا أيضا صفة تم وصف تنيمو بأنه عديم العقل أو قد زال عقله).

G-Binta lalatacciya ce (nan kuma muna bayyana vacin Binta ta hanyar amfani da lalatacciya)

بنتا فاسدة (هنا أيضا نستطيع توضيح أو إدراك فساد أخلاق بنتا عن طريق استخدام الصفة "فاسدة"

H-Hatsi buhu- buhu aka wuce da shi (anan buhu - buhu na bayyana mana yadda hatsin ya kasance, watau ba wani yanayi daban ba)

مُرّ بالشعير كيسا كيسا (وهنا كلمة كيسا كيسا تبين "توضح" لنا كيف كان الشعير، وليس في حالة أخرى)

Duk waxannan jumlolin muna iya tsamo abubuwa da za mu kira sifofi kuma kowace sifa anan tana yi mana bayani ne akan sunan da suke tare.

كل هذه الجمل يمكننا ان نستنتج منها ما نسميها بالصفات، وكل صفة فيها تبين (توضح) لنا عن اسم هي مقترنة به.

Ban da waxannan sifofin, watau baqi da siriri da qaqqarfa da lalatacciya da buhu buhu akwai mu da hanyoyi jingin na bayyana sunaye a Hausa.

بعد هذه الصفات، يعني أسود ونحيف وقوي (شجاع) وفاسدة وكيسا كيسا عندنا طرق كثيرة للتوضيح عن الأسماء في الهوسا.

Sifofi tamkar sunaye | الصفة المشبهة
بالأسماء

Kafin mu zurfafa wurin bayanin sifofi dangane da bayyanar su a jumloli da kasancewar su cikin jam'i da tilo ko ta mace ta namiji, ya kamata mu yi wani xan bayani kaxan.

قبل أن نتعمق في توضيح الصفات، خاصة فيما يتعلق بتبيانها في جمل "توضيحا من خلال استعمالها في جمل أو عبارات " أو من حيث كينونتها في "حالات" الجمع والإفراد أو التأنيث أو التذكير، فإنه من الواجب أن نقدم شرحا موجزا.

Yawancin sifofi Hausa, ko da yake sukan zo ne da sunaye, amma wani lokaci sukansu sifofin, sukan zama kamar sunaye ne.

معظم الصفات في الهوسا، في الغالب تأتي مع الأسماء، ولكن أحيانا هي بذاتها (الصفات) تقوم مقام الأسماء.

Watau, wasu sifofin idan an kira su sunaye, babu aibi, musamman ma irin waxannan:

يعني بعض الصفات إذا أطلقنا عليها أسماء فلا عيب (فلا عجب) وخاصة مثل هذه:

- Makaho — الأعمى- أعمى
- Mahaukaci — المجنون- مجنون

Manufa anan, itace ana iya cewa:

والمقصود هنا هو أننا يمكننا القول:

a- Salisu makaho ne (anan, makaho sifa ce)

أ- ثالث أعمى (وهنا كلمة أعمى makaho صفة)

b- Makaho ya zo bara (anan makaho yana aiki ne Kaman suna)

ب- الأعمى جاء للتسول (فهنا كلمة الأعمى makaho قائمة مقام الاسم).

To ashe makaho na iya zama sifa ko kuma ya yi kamar suna ta fuskar yadda ya bayyana a jumla.

إذًا، ندرك أنه يمكن للكلمة "makaho" أن تكون صفة، وأيضا يمكن أن تقوم مقام الاسم أو تؤدي عمله yayi aiki kamar suna من جهة أو من حيث ما اتضح في الجملة.

Haka ma, mahaukaci, kamar waxannan jumloli:

وهكذا أيضا، كلمة مجنون mahaukaci في هاتين الجملتين:

a- Karim mahaukaci ne (mahaukaci anan sifa ce)

كارم مجنون (كلمة مجنون mahaukaci هنا، صفة)

b- Mahaukaci ya wuce (mahaukaci anan suna ne)

المجنون مَرَّ (كلمة مجنون mahaukaci هنا، اسم)

Muna iya sarrafa gurgu ma ta waxannan hanyoyin:

وكذلك نستطيع تصريف كلمة الأعرج gurgu على نفس الطريقة:

a- Sule gurgu ne (gurgu dai dai da sf)

سليمان sule أعرج (كلمة أعرج gurgu تماما هي صفة)

b- Gurgu ne a tsugune (gurgu dai dai da sn)

الأعرج جالس القرفصاء (الأعرج هنا اسم بالضبط)

A taqaice, muna iya cewa yawancin sifofi a Hausa na iya bayyana kamar yadda sunaye suke yi a jumloli, ko da yake sun fi dangantaka da sifofin.

باختصار، نستطيع القول بأن معظم أو غالبية الصفات في الهوسا يمكن أن تبدو كالأسماء في الجمل والعبارات، على الرغم من أنها أكثر التصاقا بالصفات.

أنواع الصفات
Nau'o'in sifofi

Yanzu kuma sai mu shiga cikin rabe- raben sifofin mu kuma mu riqa bayar da sifa tare da namiji da kuma jam'in, kamar haka:

Lalatacce (sf, nj)

Lalatacciya (sf, tm)

Lalatattu (sf, jam)

والآن سنتناول الصفات في صيغ المذكر والجمع، كالآتي:

فاسد (صفة، مذكر)

فاسدة (صفة، مؤنث)

فاسدون (صفة، جمع)

Kamar yadda aka sani, bazata yiwu mu bayar da duk misalan sifofinmu ba, saboda wannan littafi ne guda zai mamaye. Sai dai za mu qoqarta mu ga rabe-raben sifofin tare da 'yan misalai a kowane rabo, sannan mu ga yadda za su iya bayyana a jumlolin Hausa.

وكما نعرف، أنه لا يمكننا أن نعرض أمثلة لكل الصفات، فذلك يجتاج إلى مجلد كبير لتغطيتها، ولكننا سنحاول أن نقدم أنواع الصفات مصحوبة ببعض الأمثلة في كل قسم (من الصفات) ثم نرى كيف تظهر (الصفات) في الجمل الهوساوية.

1- <u>Sifofi masu bayyana Launi</u>

الصفات المحددة للألوان:

Akwai mu da sifofi masu bayyana launi iri- iri:

لدينا صفات كثيرة تدل على الألوان وهي:

Namiji (til) مفرد مذكر	Ta mace (til) مفرد مؤنث	Jam’i (jam) الجمع بنوعيه
Baqi أسود	Baqa سوداء	Baqaqe سُودٌ
Fari أبيض	Fara بيضاء	Farare بِيضٌ
Ja أحمر	Ja حمراء	Jajaye حُمْرٌ
Kore أخضر	Koriya خضراء	Koraye خُضْرٌ
Shuxi أزرق	Shuxiya زرقاء	Shuxaye زُرْقٌ
Rawaya أصفر	Rawaya صفراء	Rawayoyi صُفْرٌ

su idan an Waxannan duk kana iya amfani da tabbatar da launin abinda ake Magana akai.

كل هذه يمكن استخدامها إذا تم التأكّد من لون الشيء المتحدَّث عنه.

Kuma Hausawa ma kan ninka waxannan kalmomi don nuna launuka iri-iri idan basu fito sosai ba.

وأيضا الهوساويون يضاعفون هذه الكلمات من أجل توضيح الألوان المختلفة إذا لم تكن واضحة تماما.

Watau idan abu ba fari bane sosai ba, amma yayi kama da fari, sai Hausawa su ce fari-fari.

وهذا معناه أن الشيء إذا لم يكن أبيضا جدا أو ناصعا، ولكن يبدو- يشبه- كأنه أبيض، فالهوساويون يقول fari-fari أي يميل إلى اللون الأبيض.

Haka ma idan abin ba baqi bane sosai ba, amma kamar baqi, sai su ce baqi- baqi.

وهكذا إذا لم يكن الشيء أسودا خالصا، ولكن يشبه الأسود فيقولون إنه baqi- baqi، أي أنه يميل إلى اللون الأسود.

Saboda haka, duk waxannan kalmomi da ke nuna launi, muna iya ninka su don su bamu launi ragagge ba cikakke ba.

ولذلك، كل هذه الكلمات التي تدل على الألوان، يمكننا أن نضاعفها لتعطينا ألوانا ناقصة لا الكاملة (التامة).

Ma’ana, launin abu baqi-baqi bai kai baqi ba.

بمعنى أن الشيء (إذا كان) baqi-baqi، أي الذي يميل إلى اللون الأسود، فهو دون الأسود الخالص.

Bari mu ga yadda zamu nuna kalmomin mu masu nuna launi idan muka rubuta su qarqashin su:

هيا بنا لنرى كيف سنبين ألفاظنا الدّالة على اللون حينما نكتبها تحتها.

Namiji (til) مفرد مذكر	Ta mace (til) مفرد مؤمث	Jam’i (jam) الجمع بنوعيه
Baqi- baqi أسود فاتح- يميل إلى السواد	Baqa- baqa لونها أسود فاتح	Baqaqe- baqaqe سوادهم فاتح
Fari- fari أبيض فاتح- يميل إلى البياض	Fara- fara تميل إلى البياض	Farare- farare يميلون إلى البياض
Ja- ja أحمر فاتح- وردي	Ja- ja تميل للاحمرار	Jajaye- jajaye يميلون إلى الأحمر

Shuxi- shuxi أزرق فاتح	Shuxi- shuxi تميل إلى الأزرق الفاتح	Shuxaye- shuxaye يميلون إلى الأزرق الفاتح
Rawaya- rawaya أصفر فاتح	Rawaya- rawaya تميل إلى الأصفر الفاتح	Rawayoyi- rawayoyi يميلون إلىالأصفر الفاتح
Kore- kore يميل إلى الأخضر	Koriya- koriya تميل إلى الأخضر الفاتح	Koraye- koraye يميلون إلى الأخضر الفاتح
Qasa- qasa اللون البني	Qasa- qasa بنية اللون	Ruwan qasa- qasa ألوان بنية

Kuma muna iya qari anan, kamar haka:

وكذلك نستطيع أن نضيف كلمات (صفات) كالتالي:

Qasa- qasa	Qasa- qasa	Qasa- qasa

ألوانهم بنية	لونها بني- بنية اللون	اللون البني

Wannan nau'i na sifa kusan ko yaushe a ninke yake zuwa.

هذا النوع من الصفات في الأغلب الأعم (أغلب الأوقات) يأتي مكررا (تكرار الصفات).

Watau, wando qasa-qasa ya sa.

ارتدى (yasa) سروالا يميل إلى البني.

Wasu kuma kan ce "mai ruwan qasa- qasa"

ويقول البعض: "ذو اللون البني".

Kamar yadda akan ce "mai ruwan- toka" ko "mai ruwan makuba" ko "mai ruwan xorawa".

مثلما يقال "ذو اللون الرمادي" أو "ذو اللون الأخضر" أو "ذو اللون الأصفر" وما يشابهها.

Duk launuka ne daban- daban.

كلها ألوان مختلفة.

Kuma har yanzu dai, muna da wani launi mai ban sha'awa, watau "wankan- tarwaxa".

وكذلك إلى الآن، لدينا لون مثير للدهشة، ألا وهو "wankan- tarwaxa" أي اللون القمحي.

Anan, ana nufin mutum wanda yake shi ba fari ba, shi kuma ba baqi ba.

ويراد به هنا الشخص الذي ليس بالأبيض وليس بالأسود.

Ana iya samun kalmomi da dama masu nuna launi, amma waxannan su muka fi amfani dasu.

وقد يوجد كلمات كثيرة الدّالة على الألوان، إلا أن هذه هي الأكثر استخداما عندنا.

2- Sifofi masu bayyana tsawon mutum ko abu

الصفات المحددة للأطوال (الإنسان أو غيره).

Namiji (til) مفرد مذكر	Ta mace (til) مفرد مؤمث	Jam'i (jam) الجمع بنوعيه
Dogo طويل	Doguwa طويلة	Dogaye أطوال
Matsakaici متوسط	Matsakaiciya متوسطة الطول	Matsakaita متوسطوا الطول
Gajere قصير	Gajeriya قصيرة	Gajeru قصار

3- Sifofi masu bayyana Girman mutum ko abu

الصفات المحددة للأحجام (الإنسان أو غيره).

Namiji (til) مفرد مذكر	Ta mace (til) مفرد مؤمث	Jam'i (jam) الجمع بنوعيه
Qato ضخم- سمين	Qatuwa ضَخْمَةٌ- سمينة	Qatti ضَخَمَةٌ- سمان
Qanqana صغير- قليل الحجم	Qanqanuwa صغيرة- قليلة الحجم	Qanana صغار- ضغيرة- قليلة
Qarami صغير- ضئيل	Qarama صغيرة- ضئيلة	Qanana صغار- قليلوا الحجم
Kakkaura ضخم	Kakkaura ضَخْمَةٌ	Kaurara ضَخَمَةٌ
Siriri نحيف	Siririya نحيفة	Sirara نحيفون- نحاف
Guntu قصير- قزم	Guntuwa قصيرة- قزمة	Guntaye قصار- أقزام

4- Siffofi masu bayyana yanayin abubuwa.

الصفات المحددة لحالات وطبيعة الأشياء .

Namiji (til) مفرد مذكر	Ta mace (til) مفرد مؤمث	Jam'i (jam) الجمع بنوعيه
Xanye نـيء	Xanya نيئة	Xanyu نيئة
Busasshe جاف- ناشف	Busasshiya جافة- ناشفة	Busassu أشياء جافة
Qyafaffe مجفف- مشوي	Qyafaffiya مجففة- مشوية	Qyafaffu أشياء مجففة- نواشف
Sabo جديد	Sabuwa جديدة	Sabbi أشياء جديدة
Tsoho قديم- عجوز	Tsohuwa قديمة- عجوزة	Tsofaffi/tsaffi قدماء- عواجز

5- Siffofi masu bayyana Halin da Mutum ke ciki ko yanayi

الصفات المحددة لأوضاع الإنسان أو حاله.

Namiji (til) مفرد مذكر	Ta mace (til) مفرد مؤمث	Jam'i (jam) الجمع بنوعيه
Gwauro أعزب	Gwauruwa عزباء	Gwauraye عُزّاب
Makaho أعمى – ضرير	Makauniya عمياء- ضريرة	Makafi عَميٌ
Gurgu أعرج	Gurguwa عرجاء	Guragu عرُجٌ
Maraya يتيم	Marainiya يتيمة	Marayu أيتام
Mai fitina فتّان- مُزعِج	Mai fitina فتّانة- مزعِجة	Masu fitina فتّانون- مزعِجون

Waxannan su ne irin rebe-reben da za mu iya yi a siffofi dangane da irin abubuwan da suke bayyanawa.

هذه هي كل الأقسام "الأنواع" التي في وسعنا عملها للوصف.

6- Zuwan sifofi a Jumla

مجيء الصفات في الجملة.

Yanzu kuma, sai mu ga yadda sifofi ke zuwa a jumla.

والآن أيضا، لنرى كيف أن الصفات تأتي "ترد" في الجملة.

Mun dai rigaya munce, su sifofi sukan bayyana ko siffanta sunaye ne.

لقد سبق أن قلنا أن الصفات تبين أو تصف الأسماء.

Abin tambaya anan shine, idan sun zo da sunaye xin, kafin sunayen suke zuwa, ko kuwa bayansu?

وهنا سؤال، وهو، لو أنها "الصفات" جاءت مع الأسماء، هل تأتي قبل مجيء الأسماء أو بعدها؟

A- Zuwan sifofi kafin suna ko bayansa.

مجيء الصفات قبل الاسم أو بعده.

Bari mu duba wannan jumla mu gani.

دعونا نفحص هذه الجملة ونرى:

Jum(1):

- Doki ya vata

الحصان ضاع

Ba shakka, wannan jumla bata xauke da wata sifa.

لا شك أن هذه الجملة لا تحتوي على صفة.

Waxannan kuwa fa?

وماذا عن هاتين الجملتين؟

Jum(2):

- Farin doki ya vata.

الحصان الأبيض ضاع "فَقَدَ"

jum(3):

- Doki fari ya vata

- الحصان الأبيض ضاع "فَقَدَ

A waxannan jumloli, za mu ga cewa sifa “fari” na iya zuwa kafin suna ko kuma bayan suna a cikin jumla.

في هاتين الجملتين سنرى أن الصفة "أبيض" يمكن أن تأتي قبل الاسم أو بعد الاسم في الجملة.

Yawancin sifofi na iya bayyana kamar haka, a jumloli:

فمعظم الصفات يمكن أن تظهر هكذا، في الجمل.

B- Sifofi masu zuwa bayan suna.

الصفات الواردة بعد الاسم.

Akwai kuma wasu sifofi kamar iri-iri da kashi-kashi waxanda su sukan zo ne kurum bayan suna ya zo kamar a:

وهناك بعض الصفات أيضا مثل "متنوع- أنواع- عديدة (iri-iri)، "أقسام متعددة " kashi- kashi " التي يمكن أن تأتي فقط بعد مجيء الاسم كما في (kamar a):

Jum(4):

- Ya karvo littattafai iri- iri

أخذ كتبا متنوعة "كثيرة"

Ba’a cewa:

ولا يقال:

- Ya karvo iri- iri littattafai.

أخذ متنوعة (كثيرة) كتبا.

Jum(5):

- Mata kashi- kashi sun nufi gidan biki.

النساء توجهن إلى دار الاحتفال أفواجا أفواجا.

Ba’a cewa:

ولا يقال:

- Kashi- kashi mata sun nufi gidan biki.

أفواجا أفواجا النساء توجهن إلى دار الاحتفال.

Kuma sifofi biyu ko fiye na iya zuwa ajumla xaya kamar haka:

كذلك يمكن أن تأتي صفتان أو أكثر في جملة واحدة، هكذا:

Jum(6):

- Musa baqi ne, siriri, kuma mai fara'a.

موسى أسود، ونحيف ، وطلق الوجه.

Anan, zamu ga cewa bayan bayanin launin fatar Musa, watau shi ba fari bane, ba kuma wankan tarwaxa shi da qiba. bane, kuma ba

وهنا سنرى، أنه بعد توضيح لون بشرة موسى، أنه ليس أبيض، ولا رمادي أو قمحي، وأيضا ليس سمينا.

Yana kuma da son mutane saboda haba-haba da shimfixar fuska.

وهو أيضا يحب الناس لأنه رحب الصدر وبشوش الوجه.

A qarshe, muna iya cewa akwai mu da sifofi iri-iri a Hausa waxanda suka rarrabu da dama dangane da yadda ake sarrafa su.

وفي الختام، يمكننا القول بإن لدينا أنواع مختلفة للصفات في الهوسا التي انقسمت إلى أقسام كثيرة من حيث كيفية تصريفها.

Wasu sifofin na iya bayyana kafin sunaye su zo, ko kuma bayan sunaye sunzo.

فقد تظهر (تأتي) بعض الصفات قبل الأسماء، أو بعد مجيء الأسماء.

Wasu kuwa, sukan zo ne kurum bayan sunaye.

وبعض الصفات تأتي فقط بعد الأسماء.

Amma ko ta yaya suka zo, babban aikin da suke yi shi ne bayyana mana sunaye ta hanyoyi da dama.

إلا أنه كيفما جاءت (الصفات)، أهم وظيفة تقوم بها (الصفات) هي توضيح الأسماء لنا من خلال طرق متعددة.

Tambayoyi

الأسئلة

Ka/ki/ku amsa waxannan tambayoyi:

أجب عن هذه الأسئلة:

1- Me ka fahimta da sifa a Hausa? Qawata bayaninka da misalai?

- ماذا تعرف عن الصفة في الهوسا؟ برهن على إجابتك بأمثلة.

2- Rarraba sifofin Hausa zuwa aqalla gidaje biyar dangane da yadda ake sarrafa su.

- قسِّم الصفات في الهوسا إلى خمسة أقسام على الأقل من حيث كيفية تصريفها.

3- Sarrafa waxannan sifofi cikin ingantattun jumlolin Hausa, ka kuma yi bayanin yadda suke bayyana tare da sunaye:

- Mahaukaci - siririya - baqi -buhu-buhu - qato

- صرّف هذه الصفات في جمل صحيحة هوساوية، ثم اشرح كيف تظهر (تكون) مع الأسماء:

- مجنون - نحيفة - أسود - كِيسًا- كِيسًا - ضخم (كبير- سمين)

4- Bayyana alaqar wannan rukuni na sifofi.

a- Koore	koriya	koraye
b- Baqaqe	baqi	baqa
c- Ja	jajaye	ja

- بين (اشرح) العلاقة الوصفية بين هذه الأركان:

أ- أخضر خضراء خُضْرٌ

ب- سُودٌ أسود سوداء

ت- أحمر حُمْرٌ حمراء

5- Tsamo sifofi a wannan xan labari

- استخرج الصفات من هذا النص (هذه القطعة)

An yi wani mutum qato, wanda ya auri wata yarinya fara a garinsu.

هناك إنسان ضخم الذي تزوج من فتاة بيضاء في بلدتهم.

Da suka tashi haihuwa sai suka haifi ‘ya baqa.

وعندما حان وقت الإنجاب، أنجبا فتاة سوداء.

Suka kuma sami wani xa qato bayan shekara biyar da haihuwar ‘yarsu ta farko.

ثم أنجبا طفلا ضخما (سمينا) بعد مرور خمسة أعوام من إنجابهم لابنتهم الأولى.

Da za ayi sunan xan nasu, an yi shagali iri- iri har da wata waqa mai daxi da Isa Makaho ya rera.

ولما كانوا سيضعون (سيختارون) اسما لصغيرهم، أقيمت (نصبت) الزينة والأفراح المختلفة، إضافة إلى القصيدة التي أنشدها علي مَكَاهُو (الأعمى).

مفردات:

Kalmomi

- Haba haba عملية
  الترحاب
- Shimfixar fuska
  وجه بشوش
- Mai Qiba
  بدين- سمين
- Ya vatar da doki أضاع
  الحصان
- An batar da doki ضيّع
  الحصان

- Mai ruwan qasa-qasa ذو اللون البني
- Mai ruwan Toka ذو اللون الرمادي
- Toka الرماد الناتج بعد انطفاء الفحم المشتعل
- Mai ruwan makuba ذو اللون الأخضر
- Mai ruwan xorawa ذو اللون الأصفر
- Mai ruwan qwai ذو لون صفار البيض
- Mai ruwan tarwaxa ذو اللون البني المائل للرمادي
- Wankan tarwaxa التي هي قرموط السمك tarwaxa ويقال فقط مع

Darasi na biyar: الدرس الخامس:

الأسماء والتسمية في الهوسا Sunaye a Hausa

Suna shine abinda yake nuni akan wani abu, ba tare da lokaci ba, zamu bayyana ra'ayoyin wasu daga cikin malaman nahawun Hausa akan suna da nau'o'insa da karkasuwan sa.

الاسم هو ما دل على ذات، ولم تقترن بزمن، وسوف نبين آراء بعض نحاة الهوسا حول مفهوم الاسم وأنواعه وأقسامه:

يقول Ahmadu Bello :

Sunaye dai a sanin Hausawa

الأسماء في مفهوم الهوساويين

Suna iya zamantowa "sunayen yanka ko kuma laqabi".

أي: الأسماء يمكن أن تكون أسماء أعلام أو ألقاب.

Alal misali, Muhammadu "suna ne na yanka" amma "Auwalu" laqabi ne", wanda ke ma'ana na "na farko".

فعلى سبيل المثال كلمة "محمد" فهي اسم علم، ولكن "أول" فهي لقب، حيث أنها تعني "الذي وُلِدَ أولا".

wa yarinya suna “Safiya” Haka kuma ana sa amma ariqa kiranta “Ladi” idan ranar Lahadi aka haifeta.

وهكذا أيضا يمكن أن تسمى الفتاة باسم "صفية" ولكن ينادي عليها باسم "لادي" وذلك إذا كانت قد وُلِدَتْ في يوم الأحد.

Ko kuma “Atine” ko “Tani” idan ranar Litinin aka haife ta.

أو تنادى أيضا بلقب "أتيني" أو "تني" وذلك ما إذا كانت ولدت في يوم الاثنين.

Watau, anan Safiya ne suna na yanka, amma “Ladi” ko “Atine” ko “Tani” laqabi ne.

فهذا يعني أن "صفية" هو اسم العلم، أما "لادي" أو "أتيني" فهو الاسم اللقب.

Anan kuma ana iya samun sunan yanka “Abdullahi” laqabi “Tanko”. Watau wanda aka Haifa bayan an haifi ya’ya mata da dama.

ومن هنا أيضا يمكن أن يكون هناك اسم "عبد الله" وهو اسم علم ولكن يلقب باسم "تانكو" أي "يدل على أن عبد الله هذا" هو الذي ولد بعد عدد كثير من البنات.

Wani lokaci kuma, ana kiranshi (sa) “wadata” maimakon “Tanko”.

وأحيانا أخرى يلقب باسم "وداتا" بدلا من تنكو.

وحول الأسماء في الهوسا، لا يزال Ahmadu Bello يقدم لنا رأيه فيها، فيقول:

Bayan irin waxansu rabe- rabe da zamu iya yi, waxanda suka dace da yanayin sunaye a qasar Hausa,

وبعد هذه التقسيمات العديدة التي سنقوم بها "للاسم" والتي تتناسب مع أوضاع أو طبائع الأسماء في بلاد الهوسا.

Masana nahawun Harsuna suna ganin cewa muna iya samun sunaye kashi -kashi, a harsuna daban-daban, waxanda zamu iya rarraba su.

علماء النحو في اللغات العامة يرون أننا نستطيع أن نجد أسماء متنوعة وفي لغات مختلفة، والتي بمكن لنا أن نقوم بتقسيمها.

To, a Hausa ma, akwai rabe- raben sunaye da dama[١]

ففي لغة الهوسا أيضا، هناك أقسام عديدة للاسم.

Kafin mu zurfafa cikin irin waxansu rabe-rabe, a lura mun nuna cewa sunaye na iya zama na yanka ko kuma laqabi.

---

[1] - Ahmadu Bello- Sabon Nahawun Hausa- Ahmadu Bello Univeristy press limited, Zaria, Kaduna state- Nigeria 2013. P. 4-5

وقبل أن نتعمق في – بيان- بعض هذه التقسيمات "الخاصة بالاسم" يلاحظ أننا قد أوضحنا أن الأسماء قد تكون أسماء أعلام أو ألقاب.

Ya kamata mu yi xan bayani kaxan akan dalilan da ya sa Hausawa ke kallon sunaye ta wannan fuska, kafin mu bayyana irin rabe-raben sunayen gaba xaya.

ومن الضروري أن نقدم شرحا مختصرا حول الأسباب التي حعلت الهوساويين ينظرون (يتعاملون مع) الأسماء من وجهة النظر هذه، وذلك قبل أن نوضح (نشرح) هذه الأنواع المختلفة للأسماء بصفة عامة.

Na farko: Sunan yanka

أولا: أسماء العلم

لقد وضع Ahmadu Bello رمزا مختصرا يشير إلى مصطلح أسماء الأعلام وهو (sn- ynk) .

فيقول:

Me ya sa muke kiran sunaye kamar "Safiya da Hadizatu da Zainabu da Aishatu da Saudatu da Abdurrahman da Ahmadu da Sauransu" sunayen yanka?

ما الذي دعانا لأن نطلق على الأسماء الآتية (صفية- خديجة – زينب – عائشة- سودة – عبد الرحمن – وأحمد) وغيرهم أسماء أعلام؟

Babu shakka, idan muka xauki irin waxannan sunaye kamar yadda suke a qasar Hausa, zamu ga an sanya su ne kan waxannan dalilai:

فبدون شك، لو أننا أخذنا هذه الأسماء كما هي في بلاد الهوسا، فسنرى أنها وضعت بناء على هذه الأسباب:

A-Kowanne daga cikin waxannan sunayen, akan zava ne azartar a kuma raxa wa yaro ko yarinya kafin kwana bawkai da haihuwa ko bayan haka.

أ- فكل "اسم" من بين هذه الأسماء، أختير وأخذ (تم انتقاؤه) بعناية، وأطلق على الولد أو البنت قبل سبعة أيام من الولادة أو بعد ذلك.

Shi kuma, sunan yanka, yana da dangantaka da ragon da akan yanka lokacin suna a qasar Hausa.

واسم العلم هذا له صلة بالخروف أو الذبيحة التي تذبح وقت تسمية المولود في بلاد الهوسا.

B-Kuma kowane suna akoyaushe, ana danganta shi ne da wani tushe wanda yake qarvavve ga jama'a, musamman ta fuskar addini, dm.

ب- وكذلك كل اسم دائما ما يكون مرتبطا بأساس اختياره "مرتبطا بالقاعدة المتفق عليها" عند جماعة المولود، خاصة من الوجهة الدينية، وما إلى ذلك.

Waxannan, aganin mu, su ne dalilai biyu qwarara, waxanda zasu haskaka mana dalilin da yasa Hausawa ke cewa “sunan Yanka” ga irin wannan sunaye.

فهذان من وجهة نظرنا هما السببان الرئيسان اللذان سيظهر لنا السبب الذي جعل الهوساويين يقولون "Sunan Yanka" على هذا النوع من الأسما.

Na biyu: ثانيا: اللقب

Laqabi

To, mene ne kuma ake nufi da “Laqabi”?

ما هو المقصود – كذلك – باللقب؟

Wannan shima suna ne, amma shi ba tsayuwa ake a zauna a raxa wa yaro ko yarinya ba.

هو اسم أيضا، ولكنه ليس الاسم الذي يوضع للولد أو البنت أساسا.

Sai dai shi wannan sunan yakan dace ne da irin halin da aka Haifa yaro ko yarinya (dangane da rana ko yanayin qasa ko jerin maza ko mata wajen haihuwa, ds).

إلا أن هذا الاسم "اي اللقب" يناسب الظروف عندما يولد الولد أو البنت (حسب اليوم أو أحوال البلد أو ترتيب الذكور أو الإناث في الولادة) إلخ.

مفهوم الاسم عند M.A.Z. Sani: يقول:

Me ake nufi da suna?

ما المقصود بالاسم؟

فيجيب على نفسه قائلا:

Abin da ake nufi shi ne sunan abu mai rai, ko maras rai, wanda ake iya gani da ido da wanda ba a iyawa, wanda ake iya tavawa da hannu da wanda ba a iyawa.

المقصود به هو اسم الشيء أو الكائن الحي أو الجماد، الذي في الإمكان رؤيته بالعين، وهو الذي يمكن ملامسته باليد وغيره الذي لا يمكن ملامسته باليد "المحسوس والمعنوي".

Don haka, mutum, dabba, qwaro, dutse d.s kowane suna ne.

ولذلك فالإنسان، والحيوان، والحشرات، والأحجار إلخ. كلها أسماء.

Haka kuma suna yana nuni da “jinsi” da “adadi”.

فالاسم يظهر بالجنس والعدد.

Suna iri iri ne, amma zamu duba biyar daga ciki, kamar haka;

والاسم أنواع مختلفة، نركز منها على الآتي:

أسماء الأعلام
الأسماء الشائعة

- Na yanka
- Gama gari
- Gagara- qirga
- Tattarau
- Xan aikatau.

ويوضح اسم العلم بقوله:

Na yanka, kamar yadda sunan ke nuni, "sunan yaka" shi ne suna fitacce, kevantacce ga mai shi, ya Allah na mutum ne ko na wuri.

تأمل هذه الأمثلة:

عبده	مذكر	Audu nm
علي	مذكر	Aliyu nm
بنتا	مؤنث	Binta tm
حواء	مؤنث	Hauwa tm
كانو	مؤنث	Kano tm

Waxannan sunaye da ire irensu bana kowa da kowa bane, ko komai da komai.

هذه الأسماء المختلفة ليست لجميع الناس أو للأشياء كلها.

Da zarar an faxi xayan su an san wanda ake nufi, ko wurin da ake nufi takaimaimai.

فبمجرد أن ينطق بأحدها فإنه يعرف من هو "الشخص أو الشيء" الذي يقصد، أو المكان باليحديد.

ثالثا: البلاد "المدن" أو الأماكن | Na uku: Sunayen Garuruwa ko wurare

يقول Ahmadu Bello:

Yanzu kuma da yake mun bayyana waxannan, ya kamata mu duba waxansu sunaye daban da muke dasu aqasar Hausa, musamman na garuruwa, ko wurare, kamar Kano, da Sakkwato, da Zariya, Neja da Binuwai.

والآن –أيضا- على الرغم من أننا أوضحنا هذا، إلا أنه ينبغي أن ننظر إلى بعض الأسماء الأخرى المختلفة والتي هي لدينا هنا في بلاد الهوسا، خاصة المدن أو الأماكن، مثل كانو، وسوكوتو، وزاريا، ونيجر (نيجا)، وبينوي.

Su ma waxannan, a ganinmu sunaye ne irin na yanka, amma kuma ba an sa su ne akan dalilai irin na sunayen mutane ba.

وهذه أيضا، في رأينا "من وجهة نطرنا" أسماء من نوع أسماء الأعلام، ولكن لم توضع بناء على أسباب مثل أسماء الأشخاص.

Sai dai ana iya cewa, an sa waxannan sunaye ne saboda kowane wuri tabbatacce ne mai tarihi, kuma ba shi da waninsa a ko ina, kuma da zarar an ambaci sunan, an san wurin da ake nufi.

إلا أنه يمكن القول بأنه قد وضعت هذه الأسماء لأن كل مكان من المؤكد أن له تاريخه، وأيضا ليس هناك مثيله "في الاسم والحجم والمكان" في أي مكان، فبمجرد ذكر هذا الاسم، يعرف المكان المقصود (مباشرة).

Anan, zamu iya raba sunayen yanka zuwa gida biyu, kamar haka:

وهنا، بإمكاننا أن تقسيم أسماء العلم في جانبين، هما:

Mutane أشخاص	Wurare أماكن
Aminatu أمينة	Kano كانو
Abdul Qadir عبد القادر	Katsina كاتسينا
Muhammadu محمد	Sakkwato سوكوتو
Ibrahim إبراهيم	Neja نيجا
Ismai'l إسماعيل	Xanbatta طمبتا
Hafsatu حفصة	Binuwai بينوي
Asma'u أسماء	Niger نيجر "ولاية نيجر"
Zainabu زينب	Zinder زيندر

رابعا: الأسماء العامة أو الشائعة — Na Huxu: Sunaye Gama Gari

وقد رمز لها Ahmadu Bello: اختصارا بالرمز (gm-g)
وتشتمل على بعض أنواع الأسماء المختلفة، وذلك على النحو الآتي:

أ- <u>أسماء الحيوانات</u> <u>Sunayen Dabbobi</u>

Kamar yadda kowa ya sani, akwai mu da sunayen dabbobin gida dana daji.

كما يعرف الجميع أن هناك "في وجود" أسماء الحيوانات عندنا: الحيوانات البرية والأليفة.

1- Dabbobin gida su ne, kamar:

- الحيوانات الأليفة، مثل:

الحمار jaki

الحصان Doki

الجدي.... إلخ Bunsuru ds.

2- Kuma a cikin dabbobin dawa, akwai:

- وكذلك هناك الحيوانات البرية "حيوانات الغابة" منها:

الأسد Zaki

النمر Damisa

الفهد Gwanki

الجاموس الوحشي Vauna

Kunkuru ds. السلحفاة....إلخ

3- Muna iya samun wasu dabbobi a ruwa kamar:

- وممكن أيضا أن نعثرعلى حيوانات أو كائنات مائية مثل:

Kada التمساح

Dorina فرس النهر

Kifi السمك

Kunkuru ds السلحفاة....إلخ

4- Kuma muna da sunayen Tsuntsaye, kamar:

- كذلك لدينا أسماء الطيور، مثل:

Kaza الدجاجة

Gauraka بلبل – كروان

Kurciya اليمامة

Tantabara ds. الحمامة....إلخ

5- Akwai mu kuma da Qwari, kamar:

- وهناك الحشرات، مثل:

Tana الدودة الطينية

cinnaka النمل الأسود متوسط الحجم

shazumami ds. النمل الأبيض....إلخ

Duk waxannan abubwa ne, masu rai, sai dai wurarensu daban daban, wasu na daji (kamar Zaki), wasu na gida (kamar Jaki), wasu na yawo a sararin samaniya (kamar Kurciya), wasu ma na qarqashin qasa (kamar Tana).

فكل هذه الكائنات "المذكورة" كائنات حية، إلا أن أماكنها مختلفة، فبعضها يعيش في الغابة (مثل الأسد)، وبعضها في البيت (كالحمار)، وبعضها يسبح في أجواء السماء (كاليمامة)، وبعضها أيضا تحت الأرض (مثل الدودة الطينية).

A ganin mu, kowane daga cikin waxannan zai iya faxuwa cikin yankin suna daza mu kira “gama gari”.

وفي رأينا، إن كل واحد من بين هذه "الكائنات" يمكن أن يندرج ضمن قطاع أو شريحة الاسم الذي سنطلق عليه اسم "الأسماء العامة أو الشائعة".

B- Sunayen Abubuwa Fai — ب- الأسماء الحسية:

Bayan irin waxannan sunaye da muka gabatar, idan muka lura da kyau, zamu ga cewa muna da wasu irin sunaye a Hausa na abubuwa marasa rai, amma mukan xauka muyi amfani da su.

وبعد هذا النوع الذي قدمناه في الأسماء، لو أننا انتبهنا جيدا، سنرى أننا لدينا بعض أنواع الأسماء في الهوسا يخص الجمادات، ولكننا أخذناها لنستعملها.

Irin waxannan abubuwan suna cikin sunaye fai, waxanda suka haxa da “tavarya, wuqa, kwalba, madubi, lauje” dm.

مثل هذه الأشياء موجودة في الأسماء الحسية، التي امتزجت بـ "الفأس، السكين، الزجاجة، المرآة، والمنخل... وما شابهها".

Abin da ya sa muka kira irin waxannan sunaye, sunayen abubuwa fai, shi ne saboda za a iya ganin su, kuma a tava su, har ayi amfani da su.

فالسبب الذي جعلنا نسمي هذه الأسماء بالأسماء المحسوسة هو أنه، لأننا نستطيع رؤيتها، وأيضا ملامستها، لدرجة أنه يمكن استعمالها.

ث- الأسماء المعنوية المجردة : C- Sunayen Abubuwa Voyayyu

To, sai kuma wani vangare na sunaye da muke da su, wanda zamu kira, “sunayen abubuwa voyayyu.”

وهناك قطاع آخر من الأسماء، وهو ما سوف نطلق عليه اسم "الأسماء المعنوية أو أسماء المجردات".

Irin waxannan sunaye, sun haxa da “soyayya, da sanyi da zumunci” ds.

ومن هذه الأسماء "الحب، البرد، والصداقة" ألخ.

Su waxannan sunaye, kishiyoyin sunayen abubuwa fai ne.

وهذه الأسماء مخالفة "متضادة" مع الأسماء المحسوسة.

Meyasa zamu kira su voyayyu?

ما هو السبب الذي جعلنا أن نطلق عليها "الأسماء المعنوية أو المجردة؟

Waxannan sunaye ne na abubuwan da ba ma iya gani, balle ma mu tava, ko mu kai ga sarrafa su.

فهذه الأسماء الخاصة بالكائنات التي لا نستطيع رؤيتها، ولا ملامستها، أو نصل إلى تصريفها.

Sai dai kurum, xan Adam yana iya shiga cikin wani hali da zai amfani da irin waxannan sunayen don bayyana irin wannan halin da yake ciki.

إلا أنه يمكن للإنسان فقط أن يدخل في الحال الذي يتناسب مع طبيعة هذه الأسماء من أجل إظهار هذا الحال الذي هو عليه.

Alal misali, idan muka xauki “soyayya” babu yadda zamu yi muzo muce ga soyayya a fili, balle mu

kai ga tava ta, sai dai kurum idan muka sami wani abu ya shiga zukatanmu. da

فعلى سبيل المثال، إذا أخذنا "حالة الحب" مثالا، فليس هناك طريقة تجعلنا نقول ها هو الحب في الساحة "أمام أعيننا" أو نصل إلى درجة ملامسته، إلا إذا وجدنا الإحساس فقط في قلوبنا.

Ya zamana, muna qaunar abin, har mu kwana mu tashi da abin, don qauna.

والذي سيجعلنا نحب هذا الشيء (المحبوب لدينا) لدرجة أننا ننام ونستيقظ به، من أجل الحب.

To, wannan irin halin da muke ciki, yana iya zama hali na son wannan abin.

حسنا، مثل هذا الحال الذي نحن عليه، يمكن أن يصبح حالة حب لهذا الشيء (المحبوب).

Akwai mu da sunayen irin waxannan abubuwa jingin, waxanda muke faxinsu, a koyaushe cikin harkokin mu na yau da kullum.

فلدينا مثل هذه الأسماء كثيرة التي ننطق بها دائما في تحركاتنا اليومية والمعتادة.

D- <u>Sunayen Haxaka</u> <u>أسماء شاملة (الأجناس):</u>

ويرمز لها أحمدو بللو Ahmadu Bello اختصارا بالرمز (sn-hxk) ويقول:

Akwai mu kuma da wasu irin sunaye a Hausa waxanda suka haxa da bil’adama da dabbobi da abubuwa.

يوجد لدينا كذلك بعض أنواع الأسماء في الهوسا والتي تشترك بين الناس والحيوانات وسائر الكائنات.

Sunaye kamar : “mutum ko dabba ko hutu” d.s

فأسماء مثل "الإنسان" أو "الحيوان" أو "العطلة" إلخ.

Abin lura anan, shine, kowane suna daga cikin waxannan yakan haxa abubuwa ne da yawa ba tare day a fito fili ya nuna zavinsa ko bambanci ba.

ويلاحظ هنا أنه كل اسم من بين هذه إنما يحتوي على أو يضم عناصر كثيرة بدون أن يظهر ليبين أو يوضح اختياره أو حتى الفرق.

Muna iya xaukar “mutum” a misalinmu:

إننا نستطيع أن نضرب مثالا "بالإنسان".

Mutum anan, na iya zama “Buhari ko Hadiza” waxanda suke sunaye ne na Yanka.

فالإنسان هنا قد يكون "بخاري" أو "خديجة" واللذان هما من جنس أسماء الأعلام.

Suna ma iya zama. “Tanko ko Audi” waxanda suke sunaye ne amma na laqabi.

والاسم كذلك قد يكون "تانكو" أو "أودي" واللذان هما أسماء ألقاب.

Haka ma “hutu” yana iya zama na “sallah” ko na “kirismeti” ko kuma na “makaranta”.

وهكذا أيضا "العطلة" فقد تكون "عطلة العيد" أو "عطلة عيد الميلاد" أو "العطلة المدرسية" إلخ.

Kuma “Gari” shi ma suna ne, wanda zai iya zama “Zaria” ko “Kwantagora”.

وكذلك المدينة "هي أيضا اسم، فقد تكون "زاريا" وقد تكون "كوانتجورا"

Sunaye kamar “mutum” da “hutu” da “gari” su ma kowannen su gama gari ne.

فأسماء مثل "الإنسان" و "العطلة" و "المدينة" هي أيضا أسماء عانة شائعة.

Yanzu bari mu taqaita sunayen da muka kira gama-gari, cikin jadawali, mu kuma yi qarin bayani akan su:

Gama- gari (gm-g)

Dabbobi	Tsuntsaye	Qwari	Sunayen	Sunayen	Sunayen

Haxaka أسماء شائعة	abubuwa voyayyu أسماء معنوية	abubuwa fai أسماء حسية	حشرات	طيور	دواب
إنسان Mutum	شجاعة Jarumtaka	مسمار Qusa	دودة طينية Tana	دجاجة Kaza	حمار Jaki
عطلة- إجازة Hutu	حرارة Zafi	زجاجة Kwalba	قرادة Kaska	ديك Zakara	حصان Doki
مدينة Gari	سوء- شر Mugunta	فأس Fartanya	عقرب Kunama	حمامة Tantabara	جاموسة وحشية Vauna
	حب- عاطفة Soyayya	بلطة Gatari	قرادة Kaska	حدأة Shirwa	أسد Zaki
	برد Sanyi	ملعقة Cokali	النمل الأسود متوسط الحجم Cinnaka	بوقة Mujiya	تمساح Kada
	هواء Iska		النمل الأبيض	صقر Shaho	الفهد Gwanki

		Shazuma mi			

To, me yasa muke kiran irin waxannan sunaye gama gari?

فما الذي حملنا على أن نطلق على هذه الأسماء، أسماء عامة أو مشتركة؟

A kowane rukuni cikin guda huxun nan, zamu ga cewa duk sunan da muka xauka,

في كل خانة من الخانات الأربع هنا أن كل اسم أخذناه،

Kuma idan muka xauka abin duk inda yake, ko a ina ne, haka zamu kira shi da wannan suna, bazamu canza ba.

وأخذنا المحتوى كله حينما يكون، وأينما يكون، فسوف نسميه بهذا الاسم ولا نغيره.

Sai dai fa, idan munji an laqaba masa wani sunan ne daban, sai mu ma mu riqa kira haka, kada mu zama bare a cikin dangi.

إلا إذا علمنا بأنه لُقِّب باسم آخر، عندئذ سنناديه به حتى لا نصير شاذين عن (مخالفين القواعد) العائلة.

Amma , ko an san wani sunan, mu dai mun san asalin sunan wannan abin, watau “zaki” ko “kare” ko “kwalba” ko “soyayya” ko “mutum” duk inda muke, ko kuma suke, kowannen su haka yake, kuma haka zamu kira shi da wannan sunan da muka sani.

ولكن حتى إذا وُضِع له اسم آخر، فإننا نعرف أصل اسم هذا الشيء، يعني "الأسد" أو "الكلب" أو "الزجاجة" أو "الحب" أو "الإنسان" المطلق عليه حيث كنا أو حيث كانو، فكل منهم هكذا سوف نناديه بالاسم الذي عرفناه له.

Sunaye a taqaice

ملخص عن الأسماء:

A qarshe, muna iya taqaita rabe- raben sunaye, kamar haka:

وفي النهاية يمكن أن نقدم ملخصا لأنواع الأسماء هكذا:

Sunayen Yanka أسماء الأعلام	Gama- gari (gm-g) الأسماء العامة أو الشائعة
أ- الأشخاص Mutane Wurare ب- الأماكن	a- Dabbobi da tsutsaye da kwari أ- الدواب والطيور والحشرات b- Sunayen abubawa fai ب- أسماء الأشياء الحسية c- Sunayen abubuwa

	voyayyu ت- أسماء الأشياء المعنوية d- Sunayen haxaka ث- الأسماء الشاملة

Watau, anan muna iya cewa zamu iya raba sunaye zuwa gidaje biyu, waxanda suka haxa da sunayen yanka, da ke qunshe da nau’o’in biyu. Sai kuma sunaye gama gari masu vangarori huxu.

ويعني هنا، نستطيع أن نقول أنه بإمكاننا أن نقسم الأسماء في قسمين: والذي يشتمل على أسماء الأعلام والذي يضم نوعين "الإنسان والأماكن" وأيضا قسم الأسماء العامة الشائعة والذي يقع في أربعة أنواع.

Sunaye a ganin Neil Skinner da Ibrahim Yaro Yahaya.

الأسماء من منظور نايل سكينر وإبراهيم يارو يحي:

يتكلمان عن الأسماء وأنواعها من منظور مختلف عن الذي سبق، فيقولان:

Yanzu sai kuma muyi Magana akan sunaye.

والآن سنتكلم عن الأسماء.

To, su dai sunaye kamar wakilan suna suke. Watau maganar mufuradi tilo da jam’i da maganar namiji da mace, sun tava su.

فالأسماء تشبه الضمائر الشخصية، ويعني لكل منها المفرد والجمع والتذكير والتأنيث، وله علاقة بالأسماء.

Muna faxar haka domin kowane suna ana iya cewa yana da mufuradin sa /tilo yana kuma da jam’insa. Ga waxansu misalai:

ونقول هذا لأن كل اسم منها ممكن أن يكون له مفرده وجمعه وها هي بعض الأمثلة:

mufuradi/tiloالمفرد	jam’i الجمع
gida بيت	gidaje بيوت
xaki حجرة	xakuna حجرات
mutum رجل- شخصي	mutane رجال- ناس- أشخاص
tafiya سفر	tafiye- tafiye أسفار- سفريات

Sai dai waxansu sunaye basu da jam’i, kamar: dawa, da wake, da ruwa.

إلا أن بعض الأسماء ليس لها جمع، مثل: الذرة، والبقول "اللوبيا" والماء.

Har yanzu kusan kowane suna ana iya cewa ko namiji ne kamar su: gida, doki, da dutse ko na mace ne, watau kamar su “tabarma da tunkiya”.

وحتى الآن إن معظم الأسماء يمكن أن يكون مذكرا مثل البيت والحصان، والجبل، أو يكون مؤنثا مثل: الحصيرة، الحلة "إناء".

Anan ma mun samu hanyar raba sunaye gida gida ta yadda zamu yi amfani dasu cikin zance.

وهنا أيضا عرفنا طريقة تصنيف الأسماء في خانات أو أقسام متنوعة مثلما أو بالكيفية التي نستخدمها في الكلام.

Manyan gidaje biyu sune masu sarrafuwa da sarrafaffu.

القسمان الكبيران هما أسماء مستقلة قائمة بذاتها وأخرى صفات لها.

Muna nufi da masu “sarrafuwa” sunayen da suke su da kansu na miji, ne ko na mace.

ونقصد بالأسماء القائمة بذاتها أو الأسماء المستقلة التي تعتمد على ذاتها أو مستقلة بذاتها سواء أكانت للمذكر أو للمؤنث.

Watau kamar waxanda muka ambata xazu-xazu.

يعني مثل التي ذكرناها منذ قليل "الأسماء المذكورة هنا في الدرس".

Sarrafaffu ko, siffofi, kuma muna nufin waxansu kamar su “qarami” da “babba” da “ja” da “baqi” da

da taimakon wani suna zamu “fari” waxanda galibi sai san ko na miji ne ko namace ce.

وأما "الصفات" فنقصد بها أيضا مثل "صغير" و"كبير" و "أحمر" و "أسود" و "أبيض" التي أغلبها بمساعدة أسماء أخرى نعرف أنها مذكرة، أو مؤنثة.

Misali: in maganar gida ake yi, sai mu ce qarami, ba qarama ba.

فعلى سبيل المثال: إذا كان الحديث عن "البيت" فعندئذ نصفه مثلا فنقول "بيت صغير" وليس "بيت صغيرة".

In riga muke Magana, sai mu ce qarama, ba qarami ba.

وإذا كان الحديث عن "الثياب- الثوب" فنقول "ثوب صغيرة" وليس "ثوب صغير" (وذلك لأن كلمة ثوب "riga" في الهوسا كلمة مؤنثة).

Amma lallai sai mun duba suna mai sarrafuwa, watau “gida” ko “riga” kafin mu iya siffanta shi da “qarami” ko “qarama”.

ولكن لا بد من التنبّه إلى الاسم القائم بذاته، يعني "البيت" أو "الثوب أو القميص" وذلك قبل أن نقوم بوصفه بكلمة "صغير" أو "صغيرة".

To, bari mu qara duba na gida na farko, watau na masu sarrafuwa.

فهيا بنا نتعمق أكثر في القسم الأول، الذي هو الأسماء المستقلة أو القائمة بذاتها.

Ko shi ma za mu raba shi qananan gidaje guda uku. Ga sun nan:

وهو أيضا سنقوم بتقسيمه إلى أقسام فرعية ثلاثة، وهي:

1- Sunaye gama gari da sunayen yanka

- الأسماء العامة أو الشائعة، أو أسماء الأعلام.

Duk abubuwan duniya da mutanenta da muka sani, muna sa musu sunaye daban- daban.

وكل كائنات الدنيا وأناسها الذين نعرفهم، قد وضعنا لهم أسماء مختلفة.

Su ne sunayen gama gari.

هي ما تسمى بالأسماء العامة الشائعة.

Watau, misali “gari” da “gida” da “yaro” da “aiki” da “hutu” da “yunwa” da “qaqari” da sauransu masu yawa.

يعني على سبيل المثال "المدينة" و "البيت أو المنزل" و"الولد" و"العمل" و"العطلة-الإجازة" و "الجوع" و"المحاولة" وغيرها كثيرة.

Za’a iya cewa su sunfi duk sauran kalmomi, sai dai waqilan fi’lai/ aikatau.

Sunan yanka kuma shi ne irin wanda akan rubuta da babban baqi a farkonsa, kamar “Kano” ko “Audu” ko “Najeriya” ko “Turai” ko “Tafkin cadi”.

واسم العلم هو أيضا الاسم الذي عادة ما يكتب بالحرف الكبير في أوله، مثل "كانو" أو "أودو" أو "نيجيريا" أو "أوربا" أو "بحيرة تشاد".

Watau su ne sunaye sosai, ko na mutum, ko na wuri kaza, ko na harshe kaza, kamar Hausa ko Turanci, ko Yarbanci.

يعني هي أسماء بحتة سواء أكانت اسم شخص، أو مكان كذا، أو لغة كذا، كالهوسا، أو الإنجليزية أو اليوربا.

To kunji babban gida xaya na sunaye masu sarrafuwa.

وهذا هو القسم الأول الكبير من الأسماء المستقلة القائمة بذاتها.

2- Sai kuma sunayen hali, sune masu bayyana halin abinda ake ciki.

- وأيضا أسماء الحال، وهي التي توضح أو تشرح الحال الذي عليه الشيء.

Suna kuma faxa mana yadda akayi abin ko wurin da aka yi shi ko lokacin da aka yi shi.

وتخبرنا أيضا عن كيفية فعل الشيء أو المكان الذي تم فيه عمله أو الزمن الذي فُعل فيه.

Su ne kamar “sannu” da “nan” da “yau” da “gobe” da “baya” da “gaba” da “ciki” da sauransu.

فهي مثل "بهدوء- مرحبا" و"هنا" و"اليوم" و"غدا" "وبعد- خلف" و"أمام" و"في- داخل"...إلخ.

su nan a waxannan maganganu: Ga

وهذه هي بعض الأقوال (الجمل) :

ذهب (رجل) في هدوء

a- Ya tafi da <u>sannu</u>

تعال إحضر إلى هنا

b- Ka zo <u>nan</u>

سيعود غدا

c- Zai komo <u>gobe</u>

غدا لله (لا يعلم الغيب إلا الله)

d- <u>Gobe</u> ta Allah ce

التمهّل لا يمنع الوصول

e- <u>Sannu</u> bata hana zuwa

القادم أغنم مما مضى

f- <u>Gaba</u> tafi <u>baya</u> yawa

رجعوا للداخل (عادوا لما كانوا عليه).

g- Sun koma <u>ciki</u>

3- Gida na uku na sunaye masu sarrafuwa shine gidan adadi.

- القسم الثالث من الأسماء المستقلة والقائمة بذاتها، هو الأعداد.

Watau, su (xaya, biyu, uku, huxu, dasauransu har kaiwa su miliyan miliyan).

يعني الأعداد (واحد، اثنان، ثلاثة، أربعة، إلى آخره حتى لو وصلت إلى ملايين الملايين).

To, sai kuma sarrafaffun sunaye, watau su ne waxanda sukan sami jinsinsu, watau zamantowar su namiji ko mace da suna waxanda suke siffanta shi.

فالصفات "الأسماء المتصرفة إلى الصفات" أي التي تتناسب جنسها، يعني المرتبطة أو الملازمة لجنسها ذكرا كان أو أنثى، والاسم الذي تصفه (هي).

Misali: ga Qaramin gida, ga qaramar riga. Anan da gida da riga sune sunaye masu sarrafuwa, har suna sarrafa qarami da qarama, har ya zama ko namiji ko mace.

على سبيل المثال "كقولنا" ها هو "بيت صغير"، وها هو "قميص أو ثوب صغيرة". فهنا كلمة "بيت" و"قميص – ثوب" هما اسمان مستقلان قائم كل منهما بذاته، حتى اتصفا بـ "صغير- صفة مذكر" "صغيرة- صفة مؤنث" حتى أصبح اسم الصفة إما مذكرا، وإما مؤنثا.

Amma ko sarrafaffun sunaye muna iya raba su gida biyu, ga su nan:

ولكن حتى الأسماء غير المستقلة – الأسماء الواصفة أو المحددة للصفة، أو أسماء الصفات، يمكن أن نقسمها إلى قسمين، هما:

a- Saffofi

- الصفات

b- ‘yan “wa”

- الكلمات ذوات "wa"

A-Din nan, watau “siffofi” sune kalmomi masu bayyana halin wani suna, ko wajen girma, ko launi ko kyau.

أما الصفات هذه فهي كلمات تصف الاسم من حيث طبيعة أو من حيث الحجم، أو اللون أو الجودة.

Ga waxansu nan alal misali:

وها هي بعضها على سبيل المثال:

a- Babban gida ne

- بيت كبير

b- Idanun sa <u>jajaye</u> ne

- عيناه محمرتان

c- <u>Qananan</u> yara sun zo

- جاء الأولاد الصغار "الأطفال"

d- Motoci <u>manya- manya</u> sun wuce

- لقد مرّت سيارة ضخمة

e- <u>Baqar</u> al'ada ce

- عادة سيئة (سوداء).

To, sai kuma ('yan wa) haka muke kiran waxannan kalmomi da suke farawa da "wa".

حسنا، أما عن "صفات أونوع 'yan wa " فهكذا نطلق هذا الاسم 'yan wa على الكلمات التي تبدأ بالمقطع "wa "

Ga su nan:

وها هي:

Mufuradi/tilo-namiji	Mufuradi/tilo-mace	Jam'i
Wani	Wata	Waxansu
Wannan	Wannan	Waxannan
Wanda	Waxxa	Waxanda
Wane?	Wace?	Waxanne
Wancan	Waccan	Waxancan

To, kunji gidajen sunaye, amma akwai Magana xaya wadda ya kamata ayi anan.

فقد عرفتم تقسيمات الأسماء، ولكن هناك قول آخر هو ما ينبغي طرحه هنا.

Shi ne, bayanin yadda akan xauki kalma daga gida xaya aro, ayi aiki da ita awani gida.

وهو ، بيان أو توضيح كيفية استعارة كلمة واحدة من القسم الخاص بها، وتوظيفها لدى قسم آخر.

Ga misali, “lafiya”

فا هي كلمة "عافية lafiya" على سبيل المثال.

To, wannan ba shakka suna ne, mai sarrafa. Na gama-gari.

فهي اسم ولا شك في ذلك، اسم مستقل قائم بذاته ومن الأسماء العامة الشائعة.

Jinsinsa kuma mace ce.

ومن جنس المؤنث

Domin muna cewa lafiya ta qaru, ba lafiya ya qaru ba

وذلك لأننا نقول "العافية" أو الصحة زادت، وليس العافية أو الصحة زاد.

Amma idan mun dubi “lafiyayye” zamu gani cewa ashe ya koma gidan “sarrafaffun sunaye”.

ولكن إذا نظرنا إلى طلمة "lafiyayye" سنرى أنها انتقلت إلى قسم "أسماء الصفات".

Domin gwargwadon sunan da muke so mu siffanta, ko “lafiyayye” zamu ce, ko kuma “lafiyayya” ko kuma “lafiyayyu”.

وذلك بحسب الاسم الذي نريد وصفه، فنقول إما "معافا- للمذكر" وإما "معافاة- للؤنثة" أو "معافون- للجمع بنوعيه".

Haka ma tana aukuwa da yawa wajen fa’ili/aikatau.

وأيضا كثيرا ما يحدث هذا بالنسبة للفاعل والفعل.

In mun duba “rube” amisali, ai fa’ili/aikatau ne, amma “ruvavve” ya koma gidan suna.

لو نطرنا أو أخذنا كلمة "أفسد/ فاسد ruve" مثلا فهي فعل وفاعل، أما كلمة "فاسد- ruvavve فقد عادت إلى خانة الاسم.

Sannan kuma ya zama sarrafaffen suna, sifa har muna ce “ruvavven mangwaro” amma “gwanda” ruvavviya, da kuma misali “ruvavvun ganyaye”.

ثم إنه أصبح من "أسماء الصفات" حتى لنقول مثلا: "المنجو الفاسد"، أما الباباو فنقول "الباباو الفاسدة (ذلك لأن الباباو في الهوسا مؤنث) ومثل "الأوراق الفاسدة".

Sai mu riqa lura da irin wannan rikixa domin sau da yawa akan sami haka.

لا بد أن ننتبه لمثل هذه التغيرات، لأنه كثير ما يحدث هذا.

Sunaye a ganin M. H. Jinju الأسماء عند محمد حنبلي جنجو:

-

لقد تناول الأسماء من حيث كون جنسها مذكرا أو مؤنثا، وحدد أولا مفهوم الجنس بقوله:

Jinsi, shi ne iri na mutane, ko waxansu abubuwa.

الجنس، يقصد به الأسخاص، أو بعض الكائنات الأخرى.

Cikin Hausa an raba halittu iri biyu: maza da mata.

في لغة الهوسا تم تقسم الكائنات إلى نوعين، مذكر ومؤنث.

Hanyar bambanta su ita ce wasulan qarshen sunaye.

وطريقة التفريق بينهما "المذكر والمؤنث" هي الحركة الأخيرة في الأسماء.

Na farko: Jinsin na miji أولا: جنس المذكر:

Sunaye masu qarshe (e-i-o-u) yawanci na maza ne, misali:

الأسماء المنتهية بأحد هذه الحركات (e-i-o-u) أغلبها مذكر، مثل:

Wasalin suna na qarshe حركة الاسم الأخيرة	suna	الاسم
E	babe	الفراش
	bante	لباس ستر العورة
	dantse	الساعد
	gefe	جانب- شاطئ
	jemage	خفاش
	kare	كلب
	reshe	غصن- فرع
I	akushi	جفنة
	babi	باب "منهجي"
	biki	حفل
	curi	قطعة
		سياج من أعواد الذرة

والبوص darni اتساع faxi مدينة/ دقيق gari حشو- أحشاء hanji جسد jiki رفض- كراهية qi الإسقاط عن النظر- احتقار raini مكان wuri	
ضيف – غريب baqo صندوق- علبة فارغة fanko تأديب horo مقلاة kasko تربية reno بعوض- ناموس sauro حب so	O

	radiyo مذياع
U Da sauransu.	bugu ضرب – طباعة gemu لحية lemu برتقال- عصير maruru قرحة rumbu مخزن- مستودع إلخ.

Na Biyu Jinsin Mace ثانيا: جنس المؤنث:

Wasali "a" yawanci, shi ke bambanta shi da jinsin namiji, kamar:

الحركة "a" غالبا ما تكون هي المحدد أو التي تميز "الاسم المؤنث" عن المذكر. مثل:

Wasalin suna na qarshe حركة الاسم الأخيرة	suna الاسم
A	abarba أناناس fara جرادة

	jaka حقيبة loma لقمة mara (ta tuwo) وجبة soyayya محبة zakanya لبوءة- أنثى الأسد

Sunayen ranaku, da shekaru, da dukkanin kusurwoyin duniya, da na wuraren zama, da garuruwa, da qasashe, da irga, dukansu jinsin mata ne.

أسماء الأيام، والسنوات، وجميع اتجاهات الكرة الأرضية، والأحياء السكنية، والمدن، والبلاد، والأعداد، كلها من جنس المؤنث.

Sunayen mata suna zama na mata har abada, ko menene a qarshensu kamar:

والأسماء الخاصة بالنساء، تكون مؤنثة للأبد، مهما كانت نهاياتها، مثل:

- Kande
- Ige
- Lamishi (ko Lami)
- Abu (ko zainabu)
- Jummai
- Asabe

- Hawwa

Sunayen ranaku mata ne, misali:

أسماء الأيام مؤنثة، مثل:

- الاثنين		Litinin
- الثلاثاء		Talata
- الأربعاء		Laraba
- الخميس		Alhamis
- الجمعة		Jumama'a
- السبت		Asabar
- الأحد		Lahadi

Haka kuma:

ومثلها أيضا:

- اليوم		Yau
- غدا		Gobe
- بعد غدٍ		Jibi
- بعد ثلاثة أيام		Gata
- بعد أربعة أيام (وتعني الزنجبيل)		Citta

Sunayen shekaru mata ne, misali:

أسماء السنوات مؤنثة، مثل:

- العام الماضي		Bara
- هذا العام		Bana

- العام القادم Baxi

Sunayen kusurwoyin duniya mata ne, kamar:

أسماء اتجاهات الكرة الأرضية مؤنثة، مثل:

- الشرق Gabas
- الغرب Yamma
- الجنوب Kudu
- الشمال Arewa
- الشمال الشرقي Gabas maso arewa
- الشمال الغربي Gabas maso yamma
- الجنوب الشرقي Kudu maso gabas
- الجنوب الغربي Kudu maso yamma

Haka kuma sunaye masu nuna shiyyoyi:

وهكذا أيضا الأسماء التي تشير إلى الاتجاهات:

- أمام Gaba
- خلف Baya
- فوق- أعلى Bisa/sama
- تحت- أسفل Qasa
- يمين Dama
- يسار- شمال Hagu

Sunayen ungowoyi dana garuruwa dana qasashe jinsinsu mata ne, kamar:

أسماء الأحياء السكنية والمدن والبلاد مؤنثة:

الأحياء السكنية Unguwoyi	المدن Garuruwa	البلاد والقارات Qasashe
Qakari	Zazzau	Masar مصر
Gambarawa	Batagarawa	Najeriya نيجيريا
Lugu	Damagaran	Jamus ألمانيا
Kurawa	Dogon Dutsi	Amurka الأمريكة
Zazzau	Caranci	Afirka الأفريقيا
GRA	Dutsin ma	Asiya آسية
Qofar Sauro	Katsina	Turai الأوربا
Nasarawa	Kano	Ustireliya الأستراليا

Aduda su ma jinsinsu mata ne, (Komai yawan adadin kuwa).

الأعداد أيضا من جمس المؤنث (مهما كانت كثرتها).

- واحد Xaya
- اثنان Biyu
- ثلاثة Uku
- عشرة Goma

- خمسة عشر Goma sha biyar
- عشرون Ashirin
- خمسة وعشرون Ashirin da biyar
- تسعون Tasa’in
- مائة Xari
- ألف Dubu
- ألف ألف (مليون) Zambar dubu
- إلخ. Ds

استثناءات جنس المؤنث: Togiyar Jinsin Mace

Wasu sunaye, krshen su “a” ce, amma duk da haka jinsin su na miji ne, kamar:

هناك بعض الأسماء المنتهية بـ "a" ولكن رغم هذا فإن جنسها مذكر، كما في:

- قوس Baka
- ماء Ruwa
- عبد Bawa
- ديك Zakara
- كاهن Boka
- قربة Gora
- بطل Goga
- قمر Wata

- إلخ. Ds

<u>معنى إضافي للمؤنث:</u> <u>Qarin ma’ana ta mace</u>

<u>اشتقاق التأنيث:</u>

Yawanci akan iya jeranta jinsoshin biyu daura – daura alhali kuwa asalin sunaye xaya ne, kamar:

غالبا ما يمكن إدراج الجنسين "المذكر والمؤنث" ليكونا بإزاء بعضهما، مع أن أصلهما واحد، مثل:

Namiji مذكر	Mace مؤنث
Bawa عبد	Baiwa أمة
Boka كاهن- عرّاف	Bokanya كاهنة- عرّافة
Gurgu أعرج	Gurguwa عرجاء
kuturu أبرص	kuturwa برصاء
Mutum إنسان	إنسانة -Mutumniya Mutuniya
شجرة "اسم مذكر في الهوسا" Itace	شجرة "اسم مؤنث في الهوسا" Itaciya
Kurege سنجاب- يربوع	Kureganya سنجابة- يربوعة
Zomo أرنب	Zomanya أرنبة

Qarin ma’ana – “uwa”

اشتقاق الاسم باستخدام المورفيم uwa

مثل: Kamar

Kalma mai qarin ma’ana اشتقاق الاسم باستخدام المورفيم uwa	Kalmar farko المعنى الأول للكلمة
عجوزة- شيخة Tsohuwa	عجوز- شيخ Tsoho
عزباء (أرمل) أو (مطلقة) Gwauruwa	أعزب Gwauro

جنس المذكر أو المؤنث: Jinsin Namiji ko mace

-

Waxansu sunayen halittun da ake nufi, saiwarsu xaya ce.

بعض أسماء الكائنات المقصودة جذرها واحد "الجذر اللغوي".

A wannan hali, ba agane jinsi farat xaya, sai fa a cikin mahalli, ko kuwa in an qara wa sunan halittar Kalmar mace, ko na miji, kamar:

وفي هذه الحالة لا يُعرَف له جنس معين واحد بالضبط ، إلا في موضعه، أو إذا زيد لاسم هذا الكائن كلمة تأنيث أو كلمة تذكير، مثل:

نوع الاسم	الاسم
مذكر أو مؤنث mace ko namiji	النمر damisa
مذكر أو مؤنث mace ko namiji	فرس النهر dorina وتعني كرباج أو سوط لضرب التلاميذ
مذكر أو مؤنث mace ko namiji	وحيد القرن karkanda
مذكر أو مؤنث mace ko namiji	غزال barewa
مذكر أو مؤنث mace ko namiji	نعامة jimina
مذكر أو مؤنث mace ko namiji	الديك/ أنثى- رومي tolo-tolo
مذكر أو مؤنث mace ko namiji	بطة agwagwa
مذكر أو مؤنث mace ko namiji	حمامة tantabara/ tattabara
إلخ.	Da sauransu

Kalmomi “xan- ‘yar” الوحدتان الصرفيتان "ابن- بنت":

Ana iya kuma amfani dasu, domin nuna jinsi, kamar:

وأيضا يمكن استعمالهما لبيان جنس أو نوع الاسم، مثل:

Xan sanda	شرطي-
‘yar sanda	شرطية-
Ds.	إلخ.

Saiwoyin Sunayen abubba daban-daban

جذور أسماء الكائنات المختلفة اللغوية:

Ko da yake halittun iri xaya ne.

على الرغم من أن نوع المخلوقات واحد.

Amma fa jinsin, namiji daban, na mace daban, misali:

إلا أن جنس المذكر مختلف عن جنس المؤنث. مثال:

Namiji جنس المذكر	Mace جنس المؤنث

Bunsuru	جدي الماعز	Akuya	معزة- عنزة
Doki	حصان	Goxiya	مُهرة
Rago	خروف- كبش	Tinkiya (Tunkiya)	نعجة
Raqumi	جمل- بعير	Taguwa (Raquma)	ناقة
Ds.			إلخ.

Faxakarwa — تنبيه- ملاحظة:

Amma anan sunayen (rago, ragonya, raqumi, raquma) saiwowin su xaya ne (rag- raq).

لكن هنا الأسماء (خروف- كبش- ونعجة، وجمل، وناقة) جذورها اللغوية واحدة ، وهي : (rag- raqum).

Dacewar Suna da Jinsi — توافق الاسم مع الجنس:

Mu xauki suna biyu.

a- Rago
b- Akuya

فلنأخذ اسمين: عنزة وخروف.

Mun dai riga mun san cewa “rago” namiji ne, ita kuwa akuya mace ce.

لقد سبق لنا أن عرفنا أن كلمة "خروف- كبش rago" كلمة مذكرة، وكلمة "عنزة- معزة akuya" كلمة مؤنثة.

Mu kan ce:

إننا نقول:

الخروف كبر	Rago ya girma
العنزة كبرت	Akuya ta girma

أو نقول: Ko kuwa

إنه خروف	Rago ne
إنها معزة	Akuya ce

Muna kuma cewa, lallai “ragon” da muke ambata, xaya ne tak. Haka ma “akuyar” xaya ce tak.

أي إننا مع جنس المذكر نستخدم الأداة (ne)، ومع جنس المؤنث نستخدم الأداة (ce). وكذلك نقول إن كلمة "خروف" التي ذكرناها ، هي كلمة "مفردة" تماما. وكذلك أيضا كلمة "عنزة" مفردة تماما.

Har ila yau kalmomi “ya” da “ta” da “ne” da “ce” suna da jinsi, wato namiji, ko mace. Mu kan ce:

وحتى يومنا هذا وإلى يوم الدين، الكلمات "هو-ya وهي- ta"و دالة المذكر "ne " ودالة المؤنث "ce " كلمات لها جنسها ، يعني مذكر ومؤنث. فنقول: الأدوات "ne و ya " تتوافقان مع كلمة "خروف" لأنها مذكرة.

- و "ce و ta " توافقتا مع كلمة "عنترة" لأنها مؤنثة.

Baya yiwuwa cikin Hausa qarvavviya a ce”

- Rago ta girma
- Ko kuwa:
- Rago ce. Haka kuma ba a cewa:
- Akuya ya girma
- Akuya na.

فليس من الممكن في الهوسا القياسية الفصحى أن يقال :

- الخروف كبرت، أو

- إنها خروف. وكذلك الحال لا يمكن أن يقال:

- المعزة كبر، أو

- إنه معزة.

Qa’idar dacewar suna da jinsi tana nuna cewa, suna mufuradi (xaya tak), yana dacewa da jinsi.

فقاعدة توافق الاسم مع جنسه تبين أن الاسم المفرد "الواحد فقط" يتناسب مع الجنس أو النوع "الذي ينتمي إليه".

A taqaice in suna namiji ne, shi jinsin sai ya dace da suna ya zama namiji.

وباختصار، إذا كان الاسم مذكرا، فلا بد أن يتوافق النوع مع الاسم ليكون مذكرا.

In kuma suna mace ne sai jinsi ya zama mace a mufuradance (wato abubuwan da suna ke wakilta, basu fi xaya ba).

وإذا كان الاسم كذلك مؤنثا فلا بد للنوع أو الجنس أن يكون مؤنثا في حالة إفراده (يعني أن الأشياء التي ينوب عنها الاسم لا يتعدى أن يكون واحد).

توضيح: الشيء أو النوع الذي يعبر عنه الاسم الموضوع له، ينبغي أن يكون مفردا، مذكرا كان أم مؤمثا، وذلك لأن الجنس أو النوع يكون في معظم الأشياء التي في صيغة الجمع صعب التحديد. فلا نستطيع أن نصفه، فنقول جمع مذكر، أم جمع مؤنث، إلا إذا وضعت كلمة أخرى عن طريق الإضافة لتحديد ماهية هذا الجنس الوارد في صيغة الجمع.

<u>Faxakarwa</u> <u>ملاحظة:</u>

In ance	إذا قيل:
Raguna	خراف- أكباش
Awaki	ماعز- عنزات
Shanu	أبقار
to, an dai san cewa	يُفهَم أنه:
rago xaya bane	ليس خروفا أو كبشا واحدا
	ba
ba akuya xaya bace	ليس عنزة واحدة
ba sa xaya bane	لبي ثورا واحدا
ko ba saniya xaya bace	أو ليست بقرة واحدة
Amma	وإنما:

أكباش كثيرة	Raguna da yawa ne
أبقار كثيرة	Shanu da yawa ne
معيز كثيرة	Awaki da yawa ne
فيقال:	Akan ce

Raguna sun sha ruwa (ko maza da mata ne, ko maza kawai, ko mata kawai, sai dai wanda ya gani da idonsa).

الأكباش شربت الماء (ذكورًا كانت أم إناثًا، أو ذكورا فقط، أو إناثا فقط، إلا الذي يرى بعينه).

توضيح: <u>Bayani</u>

المقصود هنا لا يمكن حمل الجمع من هذه الكائنات المذكورة أعلاه على أنها مذكرة، أو مؤنثة، إلا إذا تأكد الشخص منها، بعينه ، ليعرف ما إذا كانت ذكورا أم إناثا.

Wato, jinsin jam'i na miji ne ko da ainihin abibuwan da suna ke wakilta mata ne ahalittar jinsinsu.

يعني: جنس الجمع مذكر، حتى لو كان أصل الأشياء التي ينوب عنها الاسم مؤنثا في نوعية جنسها.

Kuma Hausawa suna amfani da dukkanin sunayen larabci –lura da cewa su musulmai ne- musamman sunayen musulmai.

ويستخدم الهوساويون – باعتبارهم مجتمع إسلامي- كل الأسماء العربية وخاصة أسماء المسلمين.

Maza suna da sunayen maza, mata na da sunayen mata.

فالذكور لهم نفس أسماء الذكور، والإناث لهن نفس أسماء الإناث.

Tana iya yiwuwa, asama xan canji wajen ginin sunayen Hausawa, musamman ma a qarshen su.

وقد يعتري الاسم الهوساوي بعض التغيير الطفيف في بنيته، وخاصة في نهايته.

Hakan na nufin sunayen Hausawa galibinsu, suna qarewa da wasali, saboda asalin kalmomin Hausa suna qarewa da wasali ne, ko kuma abinda ake cewa “buxaxxiyar gava” togiyar wasu kalmomi kaxan waxanda suke qarewa da “rufaffiyar gava” misali: malam.

وهذا يعني أن الاسم الهوساوي في أغلبه ينتهي بحركة، وذلك لأن الكلمات الهوساوية الأصل فيها أن تنتهي بحركة، أو ما يسمى مقطع مفتوح، باستثناء بعض الكلمات القليلة التي تنتهي بمقطع مغلق، نحو: "معلم malam".

Kuma akwai wasu sunayen waxanda suka savawa tsarin Larabci, mafi yawansu suna kasancewa na arna ne, ko maza ko mata.

وهناك بعض الأسماء التي تخالف النظام العربي، وهي في أغلبها تكون لغير المسلمين، أكانوا ذكورا أم إناثا.

Ga misalin sunaye a Hausa

وفيما يلي نموذج للأسماء في الهوسا.

Na farko: Sunayen Musulmai:

أولا: الأسماء التي تختص بالمسلمين، نذكر منها:

na miji مذكر		Mace مؤنث	
Muhammad	محمد	Fatimatu	فاطمة
Muhammadu	محمدُ	Aisha	عائشة
Ali	علي	A'isha	عايشة
Aliyu	عليُ	A'ishatu	عائشةُ
Abubakar	أبوبكر	Hindu	هندُ

Osman	عثمان	Hindatu	هندةُ
Omar- Umaru	عمر	Hadiza	خديجة
Abdurrahman	عبد الرحمن	Hadija	خديجة
Abdul Rahman	عبد الرحمن	Khadijatu	خديجةُ
Saifu	سيفُ	Hasana	حسنة
Ishak	إسحاق	Hosaina	حسينة
Yakubu	يعقوبُ	Zainab	زينب
Ya’kub	يعقوب	Zainabu	زينبُ
Hasan	حسن	Nuru	نورُ
Yusuf	يوسف	Aminatu	أمينة
Yusufu	يوسفُ	Lubabatu	لبابةُ

Nuhu	نوحُ	Jamila	جميلة
Ibrahim	إبراهيم	Ummi	أُمي
Ahmad	أحمد	Mariya	ماريا
Ahmadu	أحمدُ	Mariam	مريم
Nasiru	ناصرُ	Sara	سارة
Nazir	نزير	Misbahatu	مصباحةُ
Naziru	نزيرُ	Asma'u	أسماء
Yasir	ياسر	Marwanatu	مروانةُ
Sabiru	صابرُ	Sa'adatu	سعادة

Cikin sunaye akwai waxanda suke da alaqa da faruwar wani abu,- kamar yadda akayi nuni gareshi- ko (suke da alaqa) da wata al'ada. Misali:

وهناك من الأسماء ما هو مرتبط بحدث معين- وذلك كما سبقت الإشارة إليه- أو بعادة أو تقليد معين. فمثلا:

a- Idan jaririn ya kasance –ko namiji ko mace- an haife shi bayan tagwaye (‘yan biyu) ana kiranshi “Gambo” sai a ambace shi ko a ambace ta dashi, qari akan sunan yanka.

أ- إذا كان المولود، سواء أكان ذكرا أم أنثى جاء بعد توأم يسمى "جامبو Gambo" وهذه التسمية لقب يلقب به أو تلقب هي به، وذلك إضافة إلى اسم العلم له أو لها.

Idan hakan ya maiamaitu, sai a sake kiran jaririn da “Gambo” sai a ambaci na farkon da Gambo Babba” domin a bambanta tsakanin su.

وإذا تكرر الأمر، فالمولود يلقب أو تلقب بجامبو فيطلق على الأول أو الأولى لقب "جامبو الكبير" وذلك للتفريق بينهما.

b- Wanda aka Haifa ranar Jumma’a ana masa laqabi da “Xan Jummai” ita kuma mace “Juma” ko “Jummala” ko “Jummai”.

ب- المولود في يوم الجمعة، يلقب بـ "Xan juma’a" أو "Xan jummai"، والمولودة تحمل لقب "juma " أو " jumma" أو " jummala".

c- Wanda aka Haifa ranar Asabar ana masa laqabi da “Xan Asabe”, yarinya kuma da “Asibi” ko

“Asabe” a sakkwato kuma ana kiranta da “Ashshibi”.

ت-   المولود يوم السبت، يحمل لقب "Xan Asabe" والبنت تحمل لقب "Asibi" أو "Asabe" وفي ولايو سوكوتو يقال للبنت "Ashshbi".

d- Wanda aka Haifa ranar Lahadi, ana masa laqabi da “Xan Lami” yarinya kuma “Ladi” ko “Ladidi”.

ث-   المولود يوم الأحد، يقال له "Xan Ladi" والبنت يقال لها "Ladi " أو "Ladidi"

e- Wanda aka Haifa ranar Litinin, ana masa laqabi da “Xan liti” yarinya kuma “Altine”. Wannan a Katsina kenan, da Sakkwato da Zamfara, amma a Kano ana kiranta “Atine” a Katsina ana kiran duk jinsin biyu da “Atti”.

ج-المولود الاثنين، يقال له "Xan Liti" والبنت "يقال لها "Altine". وهذا في كاتسينا، وسوكوتو، وزامفارا، أما في كانو فيقال لها "Atine ". وفي كاتسينا يقال للجنسين معا Atti.

f- Wanda aka Haifa ranar Talata, ana masa laqabi da “Bature” yarinya kuma “Baturiya” a Sakkwato kuma da Zamfara suna kiran namiji “Modi” amma a Kano ana kiran namijin “Xan Tala” ko “Xan Talata” yarinya kuma “Talatuwa”.

ح-والمولود يوم الثلاثاء، يقال له "Bature" والبنت "Baturiya "، وفي سوكوتو وزامفارا يقولون للذكر Modi. وأما في كانو

فيقولون للولد "Xan Tala" أو "Xan Talata" أما البنت فيقولون "Talatuwa".

g- Wanda aka Haifa ranar Laraba, ana masa laqabi da “Balarabe” yarinya kuma “Larai” ko “Laraba”.

خ-والمولود يوم الأربعاء، يقولون له "Balarabe" والبنت يقولون لها " Larai" أو "Laraba ".

h- Wanda aka Haifa ranar Alhamis ana masa laqabi da “Xan Lami” yarinya kuma “Lami”.

د- المولود يوم الخميس، يقولون له "Xan Lami" والبنت يقولون لها "Lami ".

Akwai kuma sunan dangantaka.

وكذلك هناك اسم النسب.

Abinda ake nufi dashi shine a danganta wani mutum zuwa ga wani gari inda yake.

والمراد به أن يسمى "ينسب" الشخص نفسه باسم البلدة التي ينتسب إليها.

Sau da yawa, sunan dangantaka yana zuwa bayan sunan yanka ne. kamar yadda yake acikin:

وعادة ما يأتي الاسم المنسوب إليه بعد اسم العلم، وذلك كما في:

- أحمد الكنوي	Ahmad Bakane
- محمد كبير جلادنثي	Muhammad Galadanci
- علي الكشنوي	Aliyu Bakatsine

- حذيفة الكدوناوي	Huzaifah Bakadune
- علي نمانجي	Aliyu namangi
- يوسف بيثي.	Yusuf Bicci

Bugu da qari akan wasu sunayen siffofi, misali:

هذا بالإضافة إلى أسماء الصفات، مثل:

صاحب الجسم- يقال للمريض	Mai jiki
السابق- ويقال للمتوفى	Marigayi
ابن بائع الجورو	Xan mai goro
التاجر	Xan Kasuwa
إلخ.	Ds

أسئلة: Tambayoyi: (Auna fahimta)

1- Kawo misalan sunayen yanka guda uku, kuma na laqabi guda biyu daga wannan labarin mai zuwa:

٢- استخرج ثلاثة أسماء أعلام، واثنين من أسماء الألقاب من القطعة الآتية:

"A wata rana, a wani gari, an haifi wata yarinya, lokacin tana jaririya ce, an hango kamar wani haske yana fitowa daga cikin fuskarta, wannan yarinya an sa mata sunan Nuru".

"ذات يوم، وُلِدَتْ طفلةٌ في بلد ما. وحينما كانت طفلة رضيعة لوحِظَ في وجهها كأن النور ينبثق منه، فلذلك سميت هذه الطفلة بـ "نور".

3- Ka hiddo (fitar da) suna namiji guda biyu, sai kuma na mace guda biyu.
   - استخرج اسمين للمذكر واسمين للمؤنث.
4- Yi cikakken sharhi akan sunayen voyayyun abubuwa tare da misali,
   - اشرح بالتفصيل "أسماء المجردات" مع التمثيل لما تذكر.
5- Bayyana ma’anar laqabi tare da misalai.
   - اشرح معنى اللقب مع الأمثلة.
6- Menene bambanci tsakanin sunaye masu sarrafawa da sarrafaffu?
   - ما الفرق بين الأسماء المستقلة بذاتها وأسماء الصفات؟
7- Me ake nufi da sunaye gama-gari?
   - ما المقصود بالأسماء العامة والشائعة؟
8- Ka gwada lafiya da lafiyayya da lafiyayyu, kawo misali.
   - قارن بين "العافية" و "معافاة" و "معافون" ثم مع ذكر الأمثلة.

Darasi na   الدرس السادس:
Shida:

“ضمائر الأسماء   Wakilan suna (w- sn)
"الضمائر الشخصية

A wannan darasi zamuyi bayani kan wakilan suna

في هذا الدرس سوف نقدم شرحا وافيا لمفهوم الضمائر

A wannan gava, ba tare da wani kokwanto ba, zamu qudura a zukatan mu cewa, akwai mu da wasu abubuwa waxanda sukan wakilci sunaye a Hausa.

في هذا الجانب gava وبدون أي استغراب أو اندهاش، سوف نتصور أو نتخيل من الضمائر الشخصية أنه هناك بعض الأشياء التي تنوب عن الأسماء في الهوسا.

Anan, ya kamata mu yi xan bayani game da abin da ake nufi idan ance “abu kaza” na wakiltar “abu kaza”, ko kuma wannan wakilin wancan ne. mecece manufa anan?

هنا، ينبغي علينا أن نقدم شرحا مختصرا حول الشيء الذي نقصده حينما يقال او إذا قيل "شيء ما" ينوب عن "شيء ما" أو "هذا" ينوب أو نائب عن "ذاك" فما هو القصد إذا؟

A Hausance dai, idan ance “waziri” yana wakiltar “sarki” ko kuma wakilin sarki ne, manufa itace, idan “sarki” bai sami damar fitowa ba, sai aka turo waziri.

في المفهوم الهوساوي إذا قيل "الوزير" ينوب عن "الأمير" فالقصد هو، إذا لم يجد الأمير فرصة للذهاب إلى مكان معين فقد يرسل الوزير.

Ya cike gurbin sarki bisa wakilci

يملأ خانة الأمير بالإنابة (أي لينوب عن الملك).

Sabo da rashin halartar sarki

بسبب عدم حضور الأمير أو الملك.

Kuma waziri zai bada irin uzurin sarki a matsayinsa na Wakili.

وكذلك الوزير سوف يقدم اعتذار الأمير وهو نائب عنه.

Idan ma akwai wani saqo na sarki, sai waziri ya gabatar.

وإذا كانت هناك رسالة من الملك سوف يبلغها الوزير.

Kamar yadda wani lokaci waziri kan wakilci sarki,

وكما أنه في وقت ما ناب الوزير عن الأمير

Haka ma wakilan suna kan wakilci sunaye, idan su sunayen ba su bayyana ba.

وهكذا أيضا ضمائر الأسماء تنوب عن الأسماء إذا كانت الأسماء غير ظاهرة "غير موجودة في السياق".

Amma kuma akwai lokuta da dama, da walilan kan fito tare da sunaye a jimlolin Hausa, kamar yadda zamu gani anan gaba.

ولكن كثيرا من الأحيان تظهر الضمائر مع الأسماء في الجمل الهوساوية، وذلك مثلما سنرى لاحقا.

Wakilcin wakilan suna — إنابة ضمائر الأسماء

Wani abin ban sha'awa dangane da wakilan suna a Hausa, shine idan sun fito ko a madadin sunaye, ko kuma tare da sunaye, a kullum sukan kasance ne cikin wani tsari na musamman ta fuskar yanayin sunayen bisa la'akkari da jinsi da adadi.

هناك أمر مثير للدهشة بخصوص ضمائر الأسماء في الهوسا، ألا وهو إذا ظهرت "الضمائر الشخصية" نائبة عن الأسماء أو ظهرت "في

السياق" مع الأسماء فعادة ما تكون في نظام معين، من حيث نوعية الأسماء على اعتبار الجنس والعدد.

Abin nufi anan, shi ne a kullum idan suna ya kasance tilo, to shi ma wakilin suna zai zama tilo ne, idan kuma sunaye ne a wurin ko kuma sunan cikin jam'i ne, to wakilin sunan ma sai ya zama cikin jam'i.

والمراد هنا، هو أنه كلما كان الاسم مفردا، فالضمير النائب عنه لا بد أن يكون مفردا. وإذا كانت الأسماء في صيغة الجمع فالضمير الشخصي أيضا لا بد أن يكون في صيغة الجمع.

Idan kuma mutum na Magana ne da kansa, wakilin haka yake nunawa.

وإذا كان الشخص يتكلم عن نفسه، فالضمير النائب يكن كذلك أيضا.

Wakilin kuma kan nuna wanda ake yiwa Magana, da kuma wanda ake Magana kansa.

والضمير أيضا يبين المخاطب، وكذلك يبين الذي تم التحدث عنه "الغائب".

A ko yaushe kuma, wakilin kan bambanta abinda ake Magana akai, watau ko namiji ne ko kuma ta macece.

وهكذا دائما الضمير يميز أو يوضح الشيء المتحدث عنه، أيا ما كان مذكرا، أم مؤنثا.

Sunaye da wakilan su a jumla

الأسماء وضمائرها الشخصية في الجملة

Bayan wannan xan taqaitaccen bayani game da wakilan suna, ya kamata mu bada misalin wata jumla wacce take da sunaye cikinta, mu kuma ga yadda ake wakiltar sunayen.

بعد هذا العرض الموجز حول الضمائر الشخصية، ينبغي علينا أن نقدم مثالا لجملة تحتوي بداخلها على ضمائر شخصية، ونرى كذلك كيفية إنابة الضمائر الشخصية عن الأسماء.

Bayan mun idar da wannan, sai kuma mu zurfafa cikin yadda tsarin su yake da yadda sukan kasance cikin jimloli.

بعد أن انتهينا أو فرغنا من بيان هذا، من الواجب أيضا أن نتعمق في كيفية صياغتها والكيفية التي تكون عليها داخل الجمل والعبارا.

Ga wannan jumlar: وها هي الجملة:

1- Isa da Fatima sun tafi makaranta

عيسى وفاطمة ذهبا إلى المدرسة

Da zarar mun karanta wannan jumlar zamu ga cewa muna magana ne akan tafiya makarantar Isa da Fatima.

بمجرد أن قرأنا هذه الجملة، سندرك أننا نتكلم عن ذهاب عيسى وفاطمة إلى المدرسة.

Kuma duk waxannan sunaye ne na yanka.

وندرك أيضا أن كل هذه الأسماء أسماء أعلام "عيسى – فاطمة".

Tun da muna Magana ne akan su Isa da Fatima, idan alal misali, Musa ya tambayemu, cewa:

ولطالما أننا نتكلم عن عيسى وفاطمة، فإذا – على سبيل المثال- سألنا موسى قائلا:

- Ina Isa da Fatima?
- أين عيسى وفاطمة؟
- Muna iya cewa:
- نستطيع أن نقول:
- Sun tafi makaranta.
- ذهبا إلى المدرسة

Idan muka gwada jumla ta (1) da ta (3) zamu ga cewa jumla ta (3) ta fito ne daga jumla ta (1).

فإذا قمنا بمقارنة بين الجملة الأولى والجملة الثالثة، سنجد أن الجملة الثالثة تولدت من الجملة الأولى.

Watau, maimakon amfani da sunayen yanka kamar yadda suke a jere a jumlar farko, sai muka sa wakilin suna “sun” wanda ya wakilci su sunayen.

يعني بدلا من أن نستخدم أسماء الأعلام كما هي في الجملة الأولى فإننا جعلنا الضمير الشخصي "هما sun" هو الذي ناب عن الأسماء.

Manufa anan itace, “sun” xin ne yazo maimakon Isa da Fatima.

المقصود هنا هو أن "هما sun" الضمير الذي يشير إليهما جاء في الجملة بدلا من عيسى وفاطمة.

Bugu da qari kuma, wannan wakilan sunan a jam’i yake.

إضافة إلى ذلك فإن هذا الضمير الشخصي في حالة الجمع.

Wannan kuma haka yake, tinda akan mutane biyu muke Magana.

هذا، لأننا نتحدث عن شخصين اثنين. (يعني هذا الضمير sun) يخص الجمع ويخص المثنى.

<u>أنواع الضمير الشخصي</u> <u>Nau’o’in Wakilin Suna:</u>

Yanzu abin tambaya shine: shin su wakilan suna guda nawa ne? yaya zamu karkasa su don sauqin fahimta?

والآن هناك سؤال يطرح نفسه، وهو: ما هو عدد الضمائر الشخصية ؟ كيف "سنصنفها أو نقسمها karkasa" من أجل سهولة الفهم؟

Bari mu ga abubuwan da zamu iya kira wakilan suna da yadda suke kasancewa a jumloli:

دعنا نتعرف على الأشياء التي يمكن أن نسميها ضمائر الاسم الشخصية وكيف تكون في الجملة:

1- Ni na sha kankana jiya

(أنا) أكلت بطيخا بالأمس

2- Kai ka tafi makaranta

(أنت) اذهب إلى المدرسة

3- Kee kika qwace waya

(أنتِ) اغتصبتِ الهاتف بالقوة

4- Shii ya mari almajiri

(هو) لطم الطالب

5- Ita ta shanye fura

(هي) شربت العصيدة

Ko wace jumla anan ta fara ne da wakilin suna.

كل جملة هنا بدأت بضمير شخصي.

Watau “ni” da “kai” da “kee” da “shi” da “ita” duk wakilan suna ne.

بمعنى أن "أنا- nii" و "أنت- kai" و "هو- shi" و"أنتِ- kee" و"هي- ita" كلها ضمائر شخصية.

Na biyu kuma, kowane wakilin suna a nan tilo ne.

ثانيا، أن كل ضمير شخصي هنا مفرد.

Waxannan abubuwa guda biyu su ne suka haxa su.

فهذان الأمران "الضمائر المذكورة أعلاه، وكونها مفردة" قد اجتمعا معا.

Ma’ana, duka wakilai ne na suna kuma kowannen su tilo ne.

بمعنى أن كل الضمائر الشخصية، كل منها مفرد في ذاته.

Dukan su kuma guda biyar ne.

وهي "المذكورة أعلاه" خمسة ضمائر فقط

Kuma me ya bambanta su?

وما الذي يميزها عن بعضعا؟

Da farko dai: ko wace kalma yadda aka rubuta ta daban ne.

أولا: كل كلمة كما هي مكتوبة مختلفة عن غيرها.

Bari mu xauke su bi da bi don bayyana muhimman abubuwa game da kowannen su.

دعنا نأخذها أو نتناولها واحدا تلو الآخر حتى تتضح أهمية هذه الأمور "الضمائر الشخصية" بالنسبة لكل واحد منها.

Idan muka xauki wakilin suna “nii” daga jumlar farko, zamuga cewa yana nuna mai yin Magana ne ko na miji ko mace,

فإذا أخذنا الضمير "أنا" في الجملة الأولى سوف نجد أن المتكلم قد يكون مذكرا أو مؤنثا.

Amma idan anyi amfani da “kai” wannan na nuna wanda ake yi wa Magana.

ولكن إذا استُخدِم الضمير "أنتَ- kai" فهذا يشير إلى الذي وجه الكلام إليه (المخاطب).

Bugu da qari, akoyaushe yana nuna cewa na miji akewa Maganar.

إضافة إلى ذلك فإنه دائما يشير إلى المذكر الذي تم توجيه الكلام إليه "المخاطب".

“Kee” ma na nuna wadda ake yi wa Magana ne, amma kuma mace.

وضمير المفردة المؤنثة "أنتِ- kee" هو الآخر يشير إلى تلك التي يتم توجيه الكلام إليها "المخاطبة" وأنها مؤنثة.

Haka kuma idan an yi amfani da wakilin suna "shi", wannan yana nuna wanda ake Magana kansa ne. Da ma kuma na miji ne.

وهكذا إذا ضُرِب مثلٌ بالضمير الشخصي"هو- shii" فهذا يشير إلى الذي تم الحديث عنه " الغائب". وهو أيضا مذكر.

"ita" kuma na nuna wadda ake Magana kanta, kuma tilas mace ce.

والضمير "هي- ita" أيضا يشير إلى أن تلك التي يُتحدَّث عنها "الغائبة" وهي لزاما مؤنثة.

Ya ya jam'o'in waxannan wakilan suka kasance?

كيف يكون جمع هذه الضمائر الشخصية "المفردة"؟

Idan muka xauke su daki- daki kamar yadda muka gabatar a jimlolin mu guda biyar, zamu iya bayar da kamar haka: jam'in kowannen su,

إذا تناولناها "ضمائر الجمع الشخصية" كلا على حدة مثلما قدمنا في الجمل الخمس السابقة سنرى أننا نستطيع أن نقدم صيغة الجمع لكل واحدة منها. هكذا:

1- "muu" watau jam'in "nii"

"نحن" هي جمع "أنا"

2- "kuu" watau jam'in "kai"

"أنتم" هي جمع "أنتَ" (مفرد مذكر)

3- "kuu" watau jam'in "kee"

"أنتن هي جمع "أنتِ" (مفرد مؤنث)

4- "suu" watau jam'in "shi"

"هم" هي جمع "هو" (مفرد مذكر)

5- "suu" watau jam'in "ita"

"هن" هي جمع "هي" (مفرد مؤنث)

Anan muna iya tsara wakilan suna ta fuskar tilo (til) da jam'i (jam), kamar haka:

ومن هنا نستطيع أن نرتب الضمائر الشخصية وفقا أو حسب صيغة المفرد أو الجمع. هكذا:

الضمائر Wakilai	Tilo المفرد	Jam'I الجمع
Wakilin farko (na miji ko ta mace) الضمير الأول "للمذكر والمؤنث"	nii-أنا	نحن - muu
الضمير الثاني مذكر	أنتَ	أنتم

Wakili na biyu (na miji)	Kai	Kuu
الضمير الثاني مؤنث Wakili na biyu (ta mace)	أنتِ Kee	أنتن Kuu
الضمير الثالث مذكر Wakili na uku (na miji)	هو Shii	هم Kuu
الضمير الثالث مؤنث Wakili na uku (ta mace)	هي	هن

Muna iya sake tsara su kamar haka ataqaice:

ونستطيع أن نرتبها "الضمائر" بطريقة أخرى مختصرة، هكذا:

الضمائر Wakilai	مفرد Tilo	جمع Jam'i
الضمير الأول (مذكر أو مؤنث) Wakili na farko (nj-ko-tm)	أنا Nii	نحن Muu
الضمير الثاني (مذكر) Wakili na biyu (nj)	أنت Kai	أنتم Kuu

الضمير الثاني (مؤنث) Wakili na biyu (tm)	أنتِ Kee	أنتن Kuu
الضمير الثالث (مذكر) Wakili na uku (nj)	هو Shii	هم Suu
الضمير الثالث (مؤنث) Wakili na uku (tm)	هي Ita	هن Suu

Abin ban sha'awa da lura anan shine, akoyaushe ba ruwan wakili suna da ke qarqashin jam'i da nuna cewa akwai bamabnci tsakanin namiji da ta mace kamar tilo.

المثير للدهشة واللافت للنظر هنا، هو أنه دائما ليس من شأن الضمير الشخصي المندرج في حالة الجمع بالإفصاح عن وجود فرق بين المذكر والمؤنث كما في المفرد.

Qarin Bayani :　　　　مزيد من الشرح:

أن الضمائر في صيغة الجمع لا تفصح بذاتها عن كون هذا مذكرا والآخر مؤنثا، كما هو الحال في ضمائر المفرد المخاطب والغائب، فحينما نقول "نحن- mu" فإنها تشير إلى المتكلم مذكرا كان أم

مؤنثا، ومثلها في ذلك ضمير المفرد المتكلم "أنا- ni" فإنه يشير إلى أن المتكلم قد يكون مذكرا وقد يكون مؤمثا.

أما حينما نتكلم عن المخاطب فهناك تمييز بين المفرد المذكر المخاطب "أنتَ- kai" والمفردة المؤنثة المخاطبة "أنتِ- kee" وكذلك الحال بالنسبة للضمير المذكر المفرد الغائب "هو- shi" والمفردة المؤنثة الغائبة "هي- ita".

Alal misali dubi yadda wakilan suna tilo na biyu ya bambanta tsakanin na miji da ta mace, watau “kai” da “kee”, haka ma tskanin na ukun “shi” da “ita”.

فعلى سبيل المثال، انظر كيف أن الضمير الشخصي المفرد الثاني تميز بين المذكر والمؤنث، أي أن هناك "أنتَ- kai" للمذكر وهناك "أنتِ- kee" للمفردة المؤنثة. وكذلك الحال أيضا في الضمير الشخصي الثالث "هو- shii" و"هي- ita".

Bayan lura da yadda wakilan suna ke kasancewa tilon su da jam’in su, abin tambaya anan shine, shin su waxannan wakilan haka suke Zama akoyaushe kamar yadda muka tsara?

بعد ملاحظة أو الانتباه إلى كيف أن الضمائر الشخصية كانت مفردة وجمعا، يبقى السؤال: هل هذه الضمائر السخصية ستظل هكذا مثلما رتبناها أو قمنا بتصنيفها؟

Ko kuma suna canza kamanni dangane da bayyanar su a jimloli?

أم أنها تتغير ملامحها بالنسبة إلى بيانها أو ورودها أو دورها الوظيفي في الجمل ؟

Babu Shakka, xaya daga cikin hanyoyin da za'a bi, mu amsa waxannan tambayoyi itace, mu yi nazarin bayyanar da wakilin suna a wurare daban- daban a jimlolin Hausa.

لا شك أن الطريقة التي سنتبعها لنبحث عن هذه الأسئلة هي : أن نقوم بدراسة توضيحية مفصلة nazarin bayyanar عن الضمائر الشخصية في سياقات أو مواضع مختلفة wurare dabn- daban في الجمل الهوساوية.

Muna ma da wakilan suna na huxu (w- sn4) wanda zamu kira saakaayu (sky) a taqaice.

لدينا أيضا الضمير الشخصي الرابع، والذي نطلق عليه اسم أو نسميه "المبهم" أو المضمر "المبني للمجهول"

Misali, idan muka ce: "anyi aiki" zamu ga an bayyana aiwatar da aiki ne, ba tare da an faxi "wanda" ko "wacce" sukayi aikin ba.

إذا قلنا "تم أو عُمِل أو أُدّي العمل" فسوف نرى أنه أظهر "تبين" القيام بالعمل، ولكن بدون أن يذكر أو يقال "الذي" أو "التي" أو "الذين" قاموا فعلا بأداء العمل.

Ma'ana, sakayau babu ruwan sa da jinsi ko adadi.

ومعنى هذا أن "المبني للمجهول" ليس له علاقة بالجنس أو العدد.

wakilin suna a jumla: Bayyanar

الضمير الشخصي في الجملة:

Idan mun tuna a misalan jumloli da muka bayar guda biyar a baya, mun ga yadda wakilan suna kanzo a farkon jumla.

إذا رجعنا بالمذاكرة إلى الجمل الخمس التي أخذناها أمثلة فيما سبق، سوف نرى كيف أن الضمائر الشخصية تأتي في أول الجملة.

Watau, kowanne daga cikin “nii” da “kai” da “kee” da “shi” da “ita” na iya zuwa a farkon jumla.

وهذا يعني أن كل من الضمائر "أنا" و "أنت" و "أنتِ" و"هو" و"هي" يمكن لها أن تأتي في أول الجملة.

Kazalika, jam’in kowannen su, watau “muu” da “kuu” da “suu” da “suu”.

وكذلك جمع كل منها، يعني "نحن" و "أنتم- للمذكر" و"أنتن- للمؤنث" و"هم- للمذكر" و"هن- للمؤنث".

Ma’ana muna iya cewa:

بمعنى أنه يمكننا القول:

- Muu ma mun tafi نحن أيضا سافرنا
- Kuu ma mun tafi أنتم أيضا سافرتم/ أنتن أيضا سافرتن
- Suu ma mun tafi هم أيضا سافروا/ أنتن أيضا سافرتن

Wani abin ban sha'awa game da wakilin suna shine, wani lokaci sukan zo kamar haka afarkon jumla:

هناك ما يدعو للدهشة تجاه الضمائر الشخصية، وهو: في بعض الأوقات تأتي هكذا في أوائل الجمل كالآتي:

1- Naa zo Kano (wakili na farko)

جئتُ إلى كانو (الضمير الشخصي الأول)

2- In zo Kano xin? (wakili na farko)

هل يمكن أن آتي إلى كانو (الضمير الشخصي الأول)

3- Kaa cika gardama (wakili na biyu, namiji)

أنت كثير المشاكل "الشجار" (الضمير الشخصي الثاني، مذكر)

4- Kin faye feleqe (wakili na biyu,ta mace)

أنت كثيرة التدلل أو التكلف (الضمير الشخصي الثاني، مؤنث)

5- Yaa tafi gabas, (wakili na uku, namiji)

لقد اتجه شرقا، (الضمير الشخصي الثالث، مذكر)

6- Taa faxa rijiya, (wakili na uku, ta mace)

لقد وقعت في البئر (الضمير الشخصي الثالث، مؤنث)

Idan muka kwatanta waxannan wakilan da waxanda muka fara amfani dasu a jumlolin mu guda biyar tun farko, zamu iya fito da wata dangantaka.

إذا قارنّا هذه الضمائر بتلك التي بدأنا نستخدمها في الجمل "أمثلتنا- التي ضربناها أمثلة" الخمس من البداية، لاستطعنا أن نخرج بعلاقة "بينها".

هكذا:

kamar haka:

1- Wakilin suna na farko namiji “nii” na iya rikixa zuwa “na” ko “in”

الضمير الشخصي الأول المذكر "أنا- nii" ممكن يتحول إلى "na" أو "in"

2- Wakilin suna na biyu namiji “kai” na iya zama “kaa”

الضمير الشخصي الثاني "مذكر- أنت" ممكن يتحول إلى "kaa"

3- Wakilin suna na biyu, ta mace “kee” na iya juyewa “kin”

الضمير الشخصي الثاني "مؤنث- أنتِ" ممكن يتحول إلى "kin"

4- Wakilin suna na uku, namiji “shi” na iya rikixa zuwa “yaa”

الضمير الشخصي الثالث مذكر- هو" ممكن يتحول إلى "yaa"

5- Wakilin suna na uku, ta mace “ita” na iya sauyawa “taa”

الضمير الشخصي الثالث "مؤنث- هي" ممكن يتحول إلى "taa"

Saboda haka, waxannan wakilan suna “naa/in” da “kaa/kin” da “yaa/taa” na iya zuwa farkon jumlolon Hausa, kamar yadda muka nuna.

ولذلك فهذه الضمائر الشخصية "أنا naa/in"و "أنتَ- أنتِ kaa/kin" و "هو- هيyaa/taa " ممكن أن تأتي في أوائل الجمل الهوساوية، مثلما أوضحنا.

Jam’in kowannen su zai kasance kamar haka:

وجمع كل منها سيكون هكذا:

1- Wakili na farko “naa- in” zai sami jam’i “mun- mu”

الضمير الشخصي الأول "أنا naa/in" سيكون جمعه "نحن- mun/mu"

2- Wakili na biyu “kaa- kin” zasu sami jam’i “kun”

الضمير الشخصي الثاني "مذكر- أنتَ ومؤنث- kin" سيكون الجمع منه "أنتم- أنتن- kun"

3- Wakili na uku “yaa- taa” zasu sami jam’i “sun”

الضمير الشخصي الثالث "هو- yaa، هي- taa سيكون الجمع منه "هم- هن sun"

Jam’in kowannen su na iya zuwa a farkon jumla, kamar haka:

جمع كل منها ممكن يأتي في أول الجملة، هكذا:

1- Mun- mu bar garin

لقد غادرنا المدينة

2- Kun biya tarar Naira tara- tara

لقد دفعتم "كل منكم" تسع نيرات غراما، (تسعة تسعة)

3- Sun tafi Kaduna garin Gwamna

ذهبوا إلى كدونا مدينة الحاكم

<u>Wakilin suna a tsakiyar jumloli</u>

<u>الضمير الشخصي في وسط الجمل</u>

Bayan lura da yadda wakilan suna kan zo afarkon jumloli, sai kuma mu ga yadda sukan kasance a tsakiyar jumloli, kafin muyi nazarin bayyanar su a qarshen jumloli.

بعد أن لاحظنا "عرفنا" كيفية ورود الضمائر الشخصية في أول الجمل، علينا أن نرى أيضا كيف تكون في وسط الجمل، وذلك قبل أن ننتقل إلى "نقوم بدراسة توضيح ورودها في نهاية الجمل.

1- Musa ya ba ni dabino jiya

موسى أعطاني تمرا (بلحا) بالأمس

2- Aliyu ya ba ka gyaxa da maraice

علي أعطاك فول سوداني مساء

3- Yara sun baki mangwaro da safe

الأولاد أعطوكِ مانجو صباحا

4- Jama'a sun bashi kasha

الناس أشبعوه ضربا.

5- Ahmad ya ba ta hankicin tawul

أحمد أعطاها منديلا مصنوعا من القطن

Jam'in kowane wakilin suna ma na iya zuwa a tsakiya kamar haka:

وصيغة الجمع لكل ضمير شخصي يمكن أن تأتي في وسط الجملة هكذا:

1- Musa ya ba mu dabino jiya

موسى أعطانا تمرا (بلحا) أمس

2- Aliyu ya ba ku gyaxa da maraice

علي أعطاكم "قدم لكم" فول سوداني مساء

3- Yara sun ba ku mangwaro da safe

الأولاد أعطونكن مانجو صباحا

4- Jama’a sun ba su kasha

الناس أشبعوهم ضربا

5- Ahmad ya ba su hankicin tawul

أحمد أعطاهم منديلا من القطن

Anan, ya kamata mu lura cewa duk wakilin suna a kullum da qananan harufa ake rubuta su, in sun zo a tsakiyar jumla.

وهنا علينا أن ننتبه إلى أن كل ضمير شخصي يكتب بالحرف الصغير عادة وذلك إذا جاء في وسط الجملة.

<u>Wakilan suna a qarshen jumloli</u>

<u>"موقع" الضمائر الشخصية في آخر الجمل</u>

Daga nan kuma abin tambaya shi ne, shin yaya waxannan wakilan suna ke kasancewa idan sun zo a qarshen jumloli.

وهنا أيضا ما يدعو للتساؤل، وهو، كيف حال أو وضع هذه الضمائر الشخصية إذا جاءت في آخر الجمل؟

1- Musa ya ba ni (wakilin suna na farko namiji ko ta mace, kuma tilo)

موسى أعطاني (الضمير الشخصي الأول مذكر أو مؤنث- مفرد)

2- Aliyu ya ba ka (wakilin suna na biyu namiji- tilo)

علي أعطاك (الضمير الشخصي الثاني، مذكر مفرد)

3- Yara suka ba ki (wakilin suna na biyu ta mace- tilo)

الأولاد أعطوكِ (الضمير الشخصي الثاني، مؤنث مفرد)

4- Jama'a suka bashi (wakilin suna na uku namiji- tilo)

الناس أعطوه (الضمير الشخصي الثالث، مذكر مفرد)

5- Ahmad ya ba ta (wakilin suna na uku ta mace- tilo)

أحمد أعطاها (الضمير الشخصي الثالث ، مؤنث مفرد)

Jam'in kowane xaye daga cikin waxannan wakilan suna, da kanzo aqarshen jumla, na iya kasancewa kamar haka:

جمع كل واحد من هذه الضمائر الشخصية التي في آخر الجملة، يمكن أن تكون هكذا:

1- Musa ya ba mu

موسى أعطانا

2- Aliyu ya ba ku

علي أعطاكم

3- Yara suka ba ku

الأولاد أعطوكم/كن

4- Jama'a suka ba su

الناس أعطوهم

5- Ahmad ya ba su

أحمد أعطاهن

Anan, zamu fahimci cewa, wakilan suna, suna iya bambanta a kamanninsu dangane da bayyanar su a jumloli.

وسنفهم هنا أن الضمائر الشخصية يمكن أن تختلف عن بعضها بحسب ظهوورها في الجمل.

A yanzu muna iya taqaita su wakilan kan kasance farkon jumla da tsakiyar jumla ko qarshen jumla, kamar haka:

والآن بإمكاننا اختصار كيف أن الضمائر الشخصية تكون في أول الجملة ووسطها أو حتى نهايتها، وذلك كالآتي:

Taqaitawar bayyanar wakilan suna a jumloli:

شرح موجز للضمائر الشخصية في الجمل:

Wakilin suna afarkon jumla الضمير الشخصي في أول الجملة		Wakilin suna a tsakiyar jum qars الشخصي في وسط الجملة أو نهايتها		
w. sn 1	Tilo (til)	Jam’i (jam)	Tilo (til)	

الضمير الأول	المفرد	الجمع	المفرد	
	Nii/naa/in أنا	Muu/muu/mu نحن	Shi هو	
nj-٢w. sn tm الضمير الثاني	أنتَKai/kaa أنتِKee/ki	أنتمKuu/kun أنتنKuu/kun	أنتَKa أنتِKi	
nj-٣w. sn tm الضمير الثالث	هوShii/ yaa هيIta/taa	همSun/sun هنSun/sun	هوShi هيTa	

Duk yadda aka kaxa aka raya dai, za’a ga wakilan suna “tilo” guda biyar ne waxanda sukan kasance “nii” da “kai” da “kee” da “shi” da “ita” a farkon jumloli, kuma “naa- in” da “kaa” da “kin” da “yaa” da “taa” wani lokaci.

ومهما يكن الأمر، فإننا سنرى الضمائر الشخصية على خمسة أنواع أو أقسام، هي "أنا- nii" و "أنتَ- ka" و "أنتِ- kee" و "هو- shi" ثم "هي- ita" في أول الجملة، وكذلك "أنا in-naa" و "أنتَ- kaa" و "أنتِ- kin" و "هو- yaa" و "هي- taa" في أحيان أخرى.

A tsakiyar jumlolin kuma sukan kasance “ni” da “ka” da “ki” da “shi” da “ta”

أما بالنسبة لوسط الجملة أيضا فهي تكون هكذا "أنا – ni"، "أنتَ- ka" مفرد مذكر، "أنتِ- ki" مفرد مؤنث، "هو- shi" مفرد مذكر، "هي- ta" مفرد مؤنث.

Haka suke ma aqarshen jumloli.

وتكون الضمائر أيضا هكذا في نهاية الجمل.

Kuma ba a amfani da manyan baqaqe idan za’a rubuta su a tsakiya ko qarshen jumla.

وكذلك لا تكتب الضمائر بالحروف الكبيرة إذا جاءت في وسط الحملة أو في نهايتها.

Wakilan suna kuma jam’i na da nau’i uku ne kurum.

الضمائر الشخصية أيضا، من حيث الجمع والنوع كذلك، هي ثلاثة أنواع فقط.

A farkon jumla, suna iya kasancewa “muu” da “kuu” da “suu” ko kuma “mu-mun” da “kun” da “sun”.

في أول الجملة يمكن أن تكون هكذا "نحن muu" و"أنتم- أنتن- kuu"، و "هم- هن- suu" أو تكون "نحن- mun-mu"، و "أنتم- أنتن kun–" ، و"هم- هن – sun".

A qarshe, muna iya cewa su waxannan wakilan suna iya wakiltar sunayen mu na Hausa, ko na yanka (sn- ynk), ko voyayye (sn-voy), ko suna fai (sn- fa), ko ma gama gari (gm-g).

وفي النهاية، نستطيع أن نقول أن هذه الضمائر الشخصية كلها يمكن أن تنوب عن الأسماء الخاصة بكل ضمير منها في الهوسا، سواء أكانت أسماء أعلام " sunayen yanka" أو أسماء معنوية مجردة "sunayen voyayyu" أو أسماء حسية "sunayen fai" أو أسماء شائعة عامة "sunayen gama- gari".

Kuma duk yadda sunayen suka kasance.

ومهما تكون الأسماء.

Watau ko tilo “namiji ko ta mace” ko jam’i, wakilan ma haka zasu kasance.

أي سواء أكانت مفردة مذكرة أو مؤنثة أو جمع فإن الضمائر "التي تنوب عنها" هكذا –أيضا – ستكون.

Bugu da qari kuma, duk yadda sunayen suke bayyana acikin jumloli, watau ko a farko ko a tsakiya ko kuma a qarshe, wakilan na iya wakiltar su sosai a waxannan wurare.

بالإضافة إلى هذا أيضا، فحيثما تظهر الأسماء واضحة أو ظاهرة في الجمل، في أولها أو في وسطها أو في آخرها، فالضمائر يمكن أن تنوب عنها تماما وفي كل هذه المواضع (الأماكن).

Anan muka zo qarshen bayani akan wakilan suna.

إلى هنا نكون قد وصلنا إلى ختام أو نـهاية الشرح لضمائر الأسماءِ.

Tambayoyi أسئلة

1- Zavi wakilan suna guda uku daga wannan labari kuma ka faxi sunayen da suka wakilta.

“ Anyi wasu yara guda uku, Ali da Isa da Lantana. Su waxansu yara ne abokan juna, kuma kullum barci kawai ke raba su. Amma fa kowa yana da irin halin sa. Shi dai Ali yaro ne mai hankali, kuma ba ya son yawan wasa, Isa kuwa, shi banda wasa ba ya son komai. Lantana kuma daga ta tafi gaxa sai zuwa talla. Saboda irin wannan savanin hali, jama'a suna matuqar mamakin yadda abotar su ke xorewa. Saboda yawan surutun jama'a, sai yaran suka shiga cewa: muu dai baa abin da ya dame mu da ku, kwa ci kanku, kwa sha baqin ruwa, kuma tilas ku bar mu, yadda kuka gan mu”

- استخرج من هذه القطعة ثلاثة ضمائر ثم اذكر الأسماء التي تعود عليها.

"هناك ثلاثة أولاد: علي وعيسى ولانتانا. وكلهم أصدقاء، لا يفرق بينـهم إلا النوم. ولكن لكل واحد منهم طبيعته الخاصة. فأما علي فهو ذو عقل

راجح، ولا يحب اللعب، أما عيسى فلا يحب شيئا سوى اللعب. وأما لانتانا فهي ما بين المرح gaxa والذهاب للبيع، ولأجل اختلاف طبائهم، يتعجب الناس غاية كيف دامت صداقتهم لبعضهم. وبسبب ثرثرة الناس، بدأ الأولاد يتكلمون قائلين: ليس عندنا ما يضايقنا بكم (يشغلنا)، فكونوا في حالكم (kwa ci kanku)، تعستم في حياتكم (kwa sha baqin ruwa)، فكما رأيتمونا انفضوا من حولنا.

2- Kawo misalan suna uku daga wannan labari, kuma kowannensu ya kasance tilo.
- استخرج ثلاثة أسماء من هذا النص على أن يكون كل منها اسما مفردا.
3- Shi me wakilin suna da muka fara amfani dashi watau “su” yake wakilta?
- ما هي الضمائر الشخصية التي بدأنا باستخدامها (التي تنوب عن الاسم).
4- Kawo misalan wakilan suna uku, kowannensu ya kasance jam’i.
- حدد ثلاثة ضمائر شخصية في صيغة الجمع.
5- Bayyana abinda ya bambanta waxannan wakilan suna:

ku muu- ta- Shii-

- وضح (السبب) الذي يميز بين هذه الضمائر:
6- Mayar da duk wani wakilin suna “tilo” zuwa “jam’i” a wannan labari.

- حوّل كل الضمائر الشخصية المفردة - والواردة في القطعة السابقة – إلى ضمائر الجمع.

Darasi na Bakwai:

الدرس السابع:

Lokaci a Hausa — الزمن

في الهوسا

Ma’anar lokaci da amfaninsa “aikinsa”

مفهوم الزمن وأهميته "وظيفته"

Wannan darasi zai qunshi sashi guda uku, sune;

يحتوي هذا الدرس على ثلاثة مباحث، هي:

1. Ma’anar lokaci- sharhi tare da cikakken bayani.
   - مفهوم الزمن – شرح وتفصيل
2. Alaqar lokaci da aikatau
   - علاقة الزمن بالفعل
3. Muhimmancin lokaci “aikinsa”
   - أهمية الزمن "وظيفته"

1. Ma’anar lokaci- sharhi tare da cikakken bayani

مفهوم الزمن - شرح وتفصيل

Na farko; Ma’anar lokaci acikin Hausa

A taqaice, muna iya cewa “lokaci” a Hausa na iya zama wani zamani da aka yi abu ko za ayi shi abin, ko kuma ake yinsa. ([٢])

أولا: معنى كلمة "lokaci" عند الهوسا

جملة القول أن كلمة "الزمن" في الهوسا، يراد بها الزمن أو الوقت الذي يؤدي فيه الفعل أو تم أداؤه، أو سيتم فيه.

Kuma yadda akan nuna lokaci a Hausa shine ta hanyar amfani da wakilin suna xauke da takamaiman Karin sauti (ko na sama ko na qasa ko faxau) sai aikatau.

وطريقة إظهار الزمن في الهوسا تتم باستخدام الضمائر الشخصية "ضمائر الفاعل" مصحوبة بالنغمات "المرتفعة أو المنخفضة أو الهابطة" ثم الفعل.

Kuma shi dai “lokaci” wata kalma ce “mufuradi-tilo” jam’inta shine “lokuta”.

وكلمة "الزمن- الوقت" هي كلمة مفردة تجمع على "أزمنة- أزمات"

Haka ma wasu qamus na Hausa, suka ambata cewa Kalmar “lokaci” tana nufin “lokaci” shine wani yanki na zamani, idan aka haxata da Kalmar “da” don ta zama “lokacin da” to, tana nufin “lokacin da”

[2]- Ahmadu Bello- sabon nahawun Hausa- ABU Press Limited, Zaria- Kaduna- Nigeria 2014- p. 57

وكذلك ذكرت بعض معاجم لغة الهوسا أن كلمة "الزمن lokaci" تعني "الوقت- جزء من الزمن" وحينما تضاف إليها الأداة "da" تصبح " lokacin da" فتكون بمعنى "عندما" كما في:

Misali; Lokacin da ya tashi na ganshi.

أي عندما نهض رأيته

Kuma ana amfani da ita wajen kawwana “bunqasa” wasu lafuza “jimloli” kamar haka:

وكذلك تستخدم في تكوين بعض المصطلحات الأخرى، كما في:

a- Lokacin yaqi, lokacin razana ne

أ- وقت الحرب هو وقت فزع

b- In lokacin Azahar ya yi, ka tashe ni

ب- إذا حان وقت صلاة الظهر أيقظني

c- Da lokacin cin tuwo ya yi, ka kirani

ج- إذا حان وقت العَشاء ناديني (المعنى الحرفي إذا حان وقت أكل الثريد ناديني)

Kuma daga Kalmar “lokaci”aka samo “loki” kuma na mijin kalma ce a Hausa, tana nufin tsawon zamani “mai zuwa” kuma tana nufin karshen zamani.

ويشتق من كلمة "الزمن lokaci" كلمة " loki" وهي كلمة مذكرة في الهوسا، وتعني "الزمن البعيد المستقبلي القادم" كما تعني "آخر الزمان".

Kuma kamar yadda ake amfani da ita wajen waje mai nisa sosai.

كما تستعمل كذلك بمعنى " المكان البعيد جدا"

Kuma lokatai sune ,yan kalmomi masu nuna lokaci, ko daxewar yin abu.

والأزمنة كلمات تدل على نوع الوقت حتى مهما طال حدوث الفعل.

Suna kuma da wuyar furtawa, domin galibi, akan haxa su da wakilan suna ne cikin rubutu.

ومن الصعب التلفظ بها، لأنها في الغالب تأتي متداخلة مع الضمائر الشخصية أثناء الكتابة.

Ga waxansu misalai, inda muka tura haruffan kowane lokaci;

1- Sun tafi	ذهبوا
2- Za su zo yanzu	سيأتون الآن
3- Muna fita da safe	نحن نخرج صباحا
4- Sai suka tashi, suka tafi	ثم قاموا وانصرفوا
5- Ina kuke aiki?	أين تعلمون

Mun ga yadda aka haxa lokatai da wakilan suna cikin rubutu, amma har yanzu akwai wani abu da yafi wannan wuyar ganewa.

لقد رأينا كيف تداخلت الأزمنة مع الضمائر في حالة الكتابة، لكن إلى الآن ما زال هناك أمر يصعب إدراكه.

Shine rashi rubutun waxansu lokatai sam. (٣)

[3] - Neil Skinner da Ibrahim Yaro Yahaya- Hausa a sauqaqe- jagoran Nahawun Hausa- NNPC- Zaria- Kaduna- Nigeria 2010- p.9

وهو عدم كتابة "تبيان" بعض الأزمنة على الإطلاق

Ko da yake ana faxar su da baki. Misali ga waxannan:

إلا أنها تنطق على اللسان

a- Tafi اذهب
b- Ya tafi jiya ذهب بالأمس
c- Ya tafi gobe in Allah ya so سيسافر غدا إن شاء الله
d- Ya tafi maza- maza inji sarki فليذهب بسرعة كما قال الأمر
e- Ina ya tafi? أين ذهب

To, a wadannan misalai guda biyar, ko wannensu lokacinsa daban da na sauran.

ففي هذه الأمثلة الخمس، نجد لكل منها زمنه المختلف عن غيره.

A misali na farko, watau "tafi" babu wakilin suna sam.

ففي المثال الأول "اذهب" لا تجد فيه ضمير يدل على الفاعل إطلاقا

Ana umartan wani da yin abu kenan kamar akan ce "fita" ko "buxe" ko "karanta" da sauransu.

حيث يؤمر فيه المخاطب بعمل شيء، كأن يقال "اخرج" أو "افتح" أو "اقرأ" وما إلى ذلك.

To wannan lokaci akan kira shi "umarni". (٤)

وفي هذه الحالة يسمى "الزمن" صيغة الأمر

Amma sauran misalan nan sun fi wuyar ganewa.

---

[4] - Ibid. p.9

أما بقية الأمثلة، فهي أصعب فهما وإدراكا

Domin gashi mun rubuta "ya tafi" sau huxu, alhali kuwa furucinsu daban suke.

لأننا كتبنا "ذهب ya tafi" أربع مرات، في حين أن النطق بها يختلف من واحدة لأخرى

Dalilin wannan, shi ne domin rubutun boko ya kasa bayyana dukkan abubuwan da harshen hausa yakeyi. (٥)

وذلك بسبب أن الكتابة بالحرف اللاتيني قد تعجز عن توضيح كل الظواهر في "لغة الهوسا"

A Magana huxu xin nan, ko waccensu tana da wakilin suna na uku na namiji da mufuradi-tilo acikinsa (3-n-m-t)[٦]

في هذه الأمثلة الأربعة البسيطة، يوجد في كل منها الضمير الشخص الثالث للمفرد المذكر الغائب

Amma lokutansu daban-daban su ke.

ولكن نوع الزمن مختلف في كل واحد منها عن الآخر

Y. Yahaya suna cewa: Amma su kuma Neilskinner da I. "lokatai sune 'yan kalmomi masu nuna lokaci ko daxewar yin abu".[٧]

أما نايل سكينر وإبراهيم يارو يحيى فيقولان في مفهوم الزمن: "الأزمنة عبارة عن بعض كلمات تبين "نوع" الزمن حتى وإن طال "وقت" فعل الشيء أو الحدث".

---

[5] - Ibid p. 9
[6] - Ibid p. 10
[7] - Neil Skinner da I. yahaya- p-9

Su ma suna cewa su lokatai da wuya furtawa, domin galibi akan haxa su da wakilan suna ne cikin rubutu.

ويقولان أيضا أن الأزمنة من الصعب أن ينطق بها "متوصلة" لأنها في الغالب تكون متحدة مع ضمائر الأسماء كتابيا.

Su ma sun ba da misalai:

- Sun tafi - za su zo yanzu
- Ina ku ke - muna fita da safe

Wannan yana bayyana mana cewa dukkanin su Neil S. da I.Y. Yahaya sun yi tarayya akan cewa ma'anar lokaci na aiki ko na yare a Hausa ya kasu zuwa shuxaxxe, wanda ake ciki da kuma mai zuwa.

وهذا يوضح لنا أن كلا من Neil S. و I. Y. Yahaya يتفقان على أن مفهوم الزمن الفعلي أو اللغوي في الهوسا ينقسم إلى ماض ومضارع ومستقبل.

A inda zamu ga M. A. Z. Sani yana jefa tambaya akan ma'anar "lokaci" a cikin nahawu:

بينما نرى يطرح M. A. Z. Sani سؤالا حول مفهوم الزمن عند النحاة، فيقول:

Me ake nufi da "lokaci" a nahawu?

ما هو المقصود بالزمن عند النحاة؟

وهو نفسه يقوم بالإجابة على سؤاله، فيقول:

" Hakika, lokaci a nahawu yana nufin sa'ar wanzar da aiki ne na cikin jumla"

حقيقة، الزمن في النحو "عند النحاة" يراد به وقت أو لحظة القيام بالعمل في الجملة.

Aiki zai iya kasancewa an wanzar da shi, ya wuce, ko ana wanzar da shi a halin yanzu, ko kuma za’a wanzar da shi anan gaba.

الحدث أو الفعل يمكن أن يكون قد مضى، أو يجري حدوثه في الوقت الحالي، أو سيجري حدوثه في المستقبل "مستقبلا".

Akan haka ne zamu ga M. A. Z. Sani yayi nuni garemu zuwa karkasuwar lokaci manya har gida uku, sune shuxaxxe, lokaci na yanzu, da mai zuwa. Sai dais hi ya ambaci cewa waxannan manyan karkasuwan na lokaci sun qunsa wasu lokatai daban masu fitowa daga cikinsu, sai ya zama jumillar lokatai a Hausa guda bakwai ne (7) waxanda za’a iya taqaice su kamar haka:

وبناء عليه نراه M. A. Z. Sani قد أشار إلى ثلاثة أنواع أو أقسام للزمن رئيسية، وهي الماضي، والحاضر، والمستقبل إلا أنه ذكر أن الأزمنة الثلاثة الرئيسية تشتمل على أزمنة أخرى تنبثق عنها، وبالتالي يكون مجموع الأزمنة في الهوسا، سبعة (٧) أزمنة يمكن حصرها على النحو الآتي:

1- Shuxaxxen lokaci na xaya (S.L1)
   - الزمن الماضي التام الأول
2- Shuxaxxen lokaci na biyu (S.L2)
   - الزمن الماضي التام الثاني
3- Lokaci na sabo (L.S)
   - الزمن الاعتيادي
4- Lokaci na yanzu na xaya (L.Y1)
   - الزمن المضارع الأول "المستمر"

5- Lokaci na yanzu na biyu (L.Y2)

- الزمن المضارع الثاني "الموصول"

6- Lokaci na gaba na xaya (L.G1)

- الزمن المستقبل الأول

7- Lokaci na gaba na biyu (L.G2)

- الزمن المستقبل الأول

Zamu lura anan cewa wasu malaman nahawun Hausa basu sanya sigar umurni ko nema cikin lokatai, a dai- dai lokacin da zamu ga wasu kuma sun ambace su, kamar yadda hakan zai bayyana awajen Magana akan su anjima.

ونلاحظ أن بعض النحاة الهوسويين لم يدرجوا صيغة الأمر أو الطلب ضمن الأزمنة، في حين ذكرها بعضهم الآخر، وسيظهر هذا بوضوح حين الحديث عنها لاحقا.

Amma M.H. Jinju zamu gay a haxa tsakanin ma’anar lokaci dana aiki, wanda hakan ya sanya shi ya ambaci su waxannan lokatan da sunan “lokutan fi’ili” inda yake cewa:

وأما محمد حنبلي جنجو M. H. Jinju فقد ربط مفهوم الزمن بالفعلي، مما دعاه يطلق على الأزمنة هذا التعبير، أو هذا المصطلح lokutan fi’ili، حيث يقول:

Haka kuma qare-karen ma’ana lamirai da manuna sigogin fi’ilai ana rubuta su akan:

وكذلك المعاني الزائدة، الضمائر الشخصية، وعلامات الدالة على صيغ الأفعال (كلها) تكتب على:

1- Kalma xaya, idan qarin ma’ana lamiri yana gabanin manunin sigar, kamar haka:

- الكلمة الواحدة، إذا كانت زيادة معنى الضمير الشخصي (وقعت) قبل علامة الصيغة، مثل:

- Yakan rubuta (ba ya kan rubuta ba)

هو يكتب (بعدم فصل الضمير عن علامة الزمن)

- Nake rubutawa (ba na ke rubutawa ba)
- أنا أكتب (بعدم فصل الضمير عن علامة الزمن)
- Muna rubutawa (ba mu na rubutawa ba)
- نحن نكتب (بعدم فصل الضمير عن علامة الزمن)
- Mun rubuta (ba mun rubuta ba)
- نحن كتبنا (بعدم فصل الضمير عن علامة الزمن)
- Muka rubuta (ba mu ka rubuta)[8]
- لقد كتبنا (بعدم فصل الضمير عن علامة الزمن)

2- Kalmomi biyu idan manunin sigar yana gabanin qarin ma'ana lamirin, kamar haka:

- الكلمتان، إذا كانت علامة الصيغة (وقعت) قبل زيادة معنى الضمير الشخصي، مثل:

- Za ka rubuta (ba zaka rubuta ba)
- Za mu rubuta (ba zamu rubuta ba)
- Za su rubuta (ba zasu rubuta ba)

Abin nifi anan shine, idan lamirin fi'ilin yazo gabanin alamar lokaci, to ya zama wajibi a haxa lamirin da alamar lokacin, kamar yadda yake a sigogin lokatai shuxaxxe, lokaci na yanzu… ds

[8] - M.H. jinju –p.58

ويقصد بذلك أنه إذا تقدم الضمير الفعلي على علامة الزمن فيجب أن يلتصق الضمير بعلامة الزمن، كما في صيغ الأزمنة الماضي والمضارع ...إلخ.

Amma idan alamar lokaci tazo gabanin lamirin fi'ili to ya zama wajibi an raba tsakanin su a rubuce, kamar yadda yake a lokaci mai zuwa na xaya.

أما إذا تقدمت علامة الزمن على الضمير الفعلي فيجب الفصل بينهما كتابيا، كما في الزمن المستقبل الأول.

Tambayoyi:

أسئلة:

1- Yi bayani akan ma'anar lokaci bisa ga abinda ka karanta.
- اشرح في ضوء دراستك مفهوم الزمن.

2- Me ka sani akan alaqar lokaci da aikatau?
- ماذا تعرف عن علاقة الزمن بالفعل؟

3- Bayyana mahimmancin lokaci.
- اشرح أهمية الزمن.

4- Fayyace ma'anar aikatau a wajen Hausawa.
- اشرح مفهوم الفعل عند الهوسا.

5- Ka ambaci aikin aikatau.
- اذكر وظائف الفعل.

6- Bayyana ma'anar lokaci akan ra'ayoyin malaman nahawun Hausa.
- اشرح مفهوم الزمن من وجهة نظر نحاة الهوسا.

Na biyu: Ma’anar Kalmar “zamani” wajen Hausawa

ثانيا: معنى كلمة "zamani" عند الهوسا

Zamu bayyana anan, ma’anar Kalmar “lokaci” da zamani” a wajen Hausawa tare da ambaton bambamci tsakanin su.

سوف نشرح هنا معنى كل من "الزمن zamani" و "الزمن lokaci" عند الهوسا ونذكر الفرق بينهما.

Lura da cewa waxannan kalmomin asalin su larabci ne, zamu bayyana ma’anar su a wajen larabawa, sannan ya bayyana bambamci tsakanin su ta bangaren abinda ko wacce take nufi.

وباعتبار أن هاتين الكلمتين من أصل عربي، سنذكر مفهومهما عند العرب، ويظهر أيضا الفرق بينهما من حيث المعنى الدلالي لكل كلمة.

Kamar yadda bincikiken zai yi bayanin ma’anar Kalmar “hien” wadda take nuni akan wani zamani “na kusa ko na nesa” a wajen larabawa.

كذلك سوف نوضح– أيضا- مفهوم كلمة "حين" التي تشير إلى زمن ما، "قريب أو بعيد" عند العرب

Kalmar “zamani” kamar yadda ta zo acikin qamus din harsuna, shine wani yankin zamani sakakke, kamar yadda take ba da gudunmawa wajen bunqasa wasu lafuza kamar haka;

معنى كلمة "zamani" كما ورد في معاجم اللغة، هو الفترة من الزمن، كما تشارك في تكوين بعض المصطلحات والعبارات، على النجو التالي:

a- Sabbin zamuna	العصور الحديثة
b- Xan zamani	الإنسان العصري
c- Zamanin farko	الزمن الأول
d- Zamanin da ya shuxe	العصور الغابرة
e- Zamani na yanzu	الزمن الحالي أو المعاصر
f- A zamanin da الزمان	كان ياما كان- في سالف
g- Zamanin tunani	الزمن التصوري
h- Zamanin tsammani	الزمن التخيلي

Su waxannan mustalahai (F. G. H) ana amfani dasu wajen hikayoyin Hausa, kamar haka:

وهذه المصطلحات (F- G- H) تستخدم في القصص الهوساوي، كما في:

A zamanin da, ko na yanzu, ko na tunani, ko na tsammani…

كان ياما كان، في سالف الزمان، أو هذا الزمان أو في زمن تخيلي أو تصوري...

Kuma tana nufin rayuwar mutum, na miji ko mace. Kamar haka;

كذلك تفيد معنى "عُمُر" الإنسان ذكرا كان أو أنثى، هكذا:

Kai Baba, Allah (S.W.T) ya ja zamaninka

يا أبت، أطال الله عمرك

Kuma Kalmar “zamani” suna ne tilo na miji, jam’inta “zamuna- zamanoni” ana iya amfani dasu wajen bunqasa wasu kalmomi, kamar haka:

وكلمة "zamani" اسم مفرد مذكر، يجمع على "أزمان – zamanoni- zamuna" وتشترك في تكوين بعض الجمل والعبارات على النحو الآتي:

a- Zamanin sarautar turawa, zamanin bauta ne

زمن الاستعمار الأوربي، كان زمن العبودية "السخرة"

b- Zamanin sarautar qasar nan na uku, anyi hidimomin gwanintar cinikin kayan saqar sabon zamani.

زمن الاستقلال "تحرر" هذا البلد النامي "الذي ينتمي لدول العالم الثالث" ابتدأت حرفة "حركة" تجارة معدات (ماكينات) الغزل والنسج الحديثة

c- Ilimin zamani yana sa ajawo hanyoyin gyaran qasa.

العلم الحديث يساهم في تطور الدولة

كما جاء في هذا الشعرKamar yadda yazo acikin wannan waqar:

- Barno bulaka birni — برنو مدينة كبيرة
- Ta shehu gun qur'ani — مدينة الشيخ حافظ القرآن
- Tsohon garin addini — مدينة الدين العتيقة
- Ko zamani yai zamani — مهما طال الزمن
- Ba za su kauce gaskiya ba ([9]) — لن يحيدوا عن الحق

---

[9] - Tutocin shehu, Alh- Mu'azu na xeja

Na uku: Ma'anar Kalmar "har" wajen Hausa

ثالثا: معنى كلمة "حتى " عند الهوسا

Wannan Kalmar "har" harafin bagiren wuri ko lokaci ce.
Ita ma "har" tana da alaqa da lokaci ko zamani. Misali:

هذه الكلمة "حتى har" هي حرف يفيد أو يدل على ظرف المكان أو الزمان، وهي أيضا ذات صلة مباشرة بالزمن. مثال:

Kamar yadda ta zo cikin suratul Hijri, Allah (S.W.T) yana cewa:

كما جاءت في سورة الحجر، حيث يقول الله سبحانه وتعالى:

(وَاعْبُدْ رَبَّكَ حَتَّى يَأْتِيَكَ الْيَقِينُ)[١٠]

"Ka bautawa Ubangijinka har sai mutuwa tazo maka"

Watau, har sai sanannen lokaci ya zo maka wanda zai iya zama lokacin mutuwa, ko cikar wani abu ko tabbacinsa.

أي، إلا أن يأتي الوقت المعلوم الذي قد يكون الموت، أو اليقين الجازم.

Ko kuma lokacin Al fijir, kamar yadda ya zo acikin :faxinsa maxaukaki, cikin suratul Qadri

وأيضا تعني وقت الفجر، كما في قوله تعالى في سورة القدر :

(سَلَامٌ هِيَ حَتَّى مَطْلَعِ الْفَجْرِ)[١١]

---

[10]- سورة الحجر: ٩٩

[11]- سورة القدر: ٥

" ita aminci ce har sai Al fijir ya fito" watau har sai loakacin Al fijir ya yi.

Na huxu: Ma'anar Kalmar "lokaci" awajen Larabawa

رابعا: معنى كلمة "الوقت" أو "الزمن" عند العرب

Haqiqa ya zo acikin qamus xin larabci da yawa irin su: Al mu'jamul wasix, da Arra'i, da Lisanul arab, da Qamusul muhix, cewa Kalmar "lokaci" tana nufin wani yankin zamani.

حقيقة وكما جاء في معاجم اللغة العربية، ومنها: المعجم الوسيط، والرائد، ولسان العرب، والقاموس المحيط، أن كلمة "الوقت" والتي يراد بها "الزمن" أنها تعني المقدار من الزمان.

Kuma ita Kalmar "lokaci" suna ce, mufuradi-tilo ana jam'inta akan "lokuta- lokatai", watau wani yankin zamani.

وكلمة "الزمن- الوقت" اسم مفرد يجمع على "أوقات" وهي قدر من الزمان.

Kuma ana amfani da ita wajen kawwana (bunqasa) wasu lafuza kamar haka:

وتدخل هذه الكلمة من تكوين بعض العبارات والمصطلحات، منها:

a- Kafin lokaci ya wuce - قبل فوات الأوان

Watau ka tari wani al'amari kafin faruwan shi.

أي أدرك الأمر قبل وقوعه

b- Hannun agogo - إشارات ضبط الوقت

c- Lokaci ya yi - حان الوقت

d- Lokacin sahur - وقت السحر- السحور

Watau, qarshen dare gab da fitowar Al fijir

أي آخر الليل وقبل الفجر

Shi lokaci xaya ne daga cikin manyan alamomin aikatau.

الزمن هو أحد سمات الفعل الكبرى.

Kuma shi babin sarfu ne wanda yake nuni ga lokacin aiki wanda ake nuni gareshi ta hanyar aikatau.

وهو مقولة صرفية تشير إلى زمن الحركة أو الحدث المشار إليهما بواسطة الفعل.

Akwai abin da zamu iya kiran shi da lokacin nahawu, da kuma lokacin fiziya (faruwar abubuwa- physical tense).

فهناك ما يمكن أن نسميه الزمن النحوي، والزمن الفيزيائي.([١٢])

Shi dai lokacin nahawu shi ne wanda malaman nahawu suka sani, ta hanyar kasantuwar shi yana nuni ga sa'ar lokacin da aiki ya gudana acikin ta "shuxaxxe- lokaci na yanzu- mai zuwa".

فالزمن النحوي هو ما تعارف عليه النحاة، من حيث كونه يشير إلى الفترة الزمنية التي حدث فيها الفعل "ماضي- حاضر- مستقبل".

[١٢]- نادية قاسم- الزمن السياقي في التراث اللغوي العربي- رسالة ماجستير- جامعة محمد حيضر بسكرة- كلية الآداب واللغات- قسم الآداب واللغة العربية- ٢٠١٣م.

Amma shi lokacin fiziya (faruwar abubuwa) shi ne wanda malaman taurari dana fiziya suke auna qasa da taurari da sauransu.

وأما الزمن الفيزيائي فهو ما يستخدم لدى علماء الجيولوجيا والفيزياء في قياس الأرض والنجوم وغير ذلك.

Kuma akwai wani ruxani na musamman ga lokaci acikin yarukan duniya, ta yadda ake iya suranta shi acikin waxannan yarukan, tin da akwai karkasuwa irin su shuxaxxe- lokaci na yanzu- mai zuwa

وهناك إشكالية خاصة بالزمن في اللغات الإنسانية، فكيف تتصوره هذه اللغات، حيث هناك أنواع من الماضي والمضارع والمستقبل.

Shi dai lokaci da yanayi da aikatau kowanen su yana da alaqa da juna, bisa yadda ilimin sabon nahawu ya fayyace.

والزمن والجهة والفعل كل منها مرتبط بالآخر، وفقا لما بينه الدرس النحوي الحديث.

To yanzu mun san lokaci da ma'anar shi.

فالزمن معروف الآن لدينا بمفهومه.

Shi hange "Aspect" shi ke siffanta faruwan aiki.

والجهة Aspect هي التي تصف حدوث الفعل.

ya faru acikin lokaci. Shi kuma aikatau shine abin da

والفعل هو الحدث الواقع في قلب الزمن. [١٣]

[١٣]- نادية قاسم- الزمن السياقي في التراث اللغوي العربي- رسالة ماجستير- جامعة محمد حيضر بسكرة- كلية الآداب واللغات- قسم الآداب واللغة العربية- ٢٠١٣م.

Na biyar: Karkasuwan (Nau'o'in) lokaci awajen Larabawa da Turawa da Hausawa

خامسا: أنواع الزمن لدى العرب والإنجليز والهوسا

Yaruka sun bambanta tsakanin su ta bangaren yadda suke amfani da Kalma ko lafazi dake nuni akan lokacin da aikin ya faru acikin shi.

وتختلف اللغات فيما بينها بالنسبة لاستخدام الكلمة أو المصطلح الذي يشير إلى الوقت الذي يحدث فيه الفعل.

Yaren Turanci yana bambance tsakanin Kalmar lokaci "tense" da zamani "time".

فاللغة الإنجليزية تفرق بين كلمة tense و time.

Ita Kalmar "tense" tana nuni akan lokacin nahawu, amma Kalmar "time" tana nuni akan zamani wanda baya cikin harshe. Wato tana nufin lokacin da ba na nahawu ba.

حيث أن كلمة tense تشير إلى الزمن النحوي، أما time فتشير إلى الزمن خارج اللغة، أي أنها تشير إلى زمن غير نحوي.

Kuma Dangane da nau'o'in lokaci acikin yarukan yi nuni ga yaruka guda biyu. Su ne yaren mu duniya, za Larabci lura da cewa xaya ce daga cikin yarukan dangin Afrosiyawiya wadda yaren Hausa take dangantuwa zuwa gareta.

وبالنسبة لأنواع الزمن في اللغات الإنسانية، سوف نشير إلى لغتين أخريين، وهما العربية باعتبارها نموذجا لأسرة اللغات الأفروآسيوية التي تنتمي إليها الهوسا.

Yaren larabci bai san daga nau'o'in lokaci ba sai guda uku "shuxaxxe- lokaci na yanzu- mai zuwa" kuma za'a iya samun lokaci sama da guda xaya cikin jumla xaya.

اللغة العربية لا تعرف إلا ثلاثة أنواع للزمن "ماضي- حاضر- مستقبل أو حال" ويمكن أن يحتوي الجملة الواحدة على أكثر من زمن.

Amma yaren Turanci kuwa yana da nau'o'i guda goma sha biyu, su ne:

أما اللغة الإنجليزية فتعرف اثنتا عشرة نوعا للزمن، هي :

- الماضي البسيط past simple tense
- المضارع البسيط present simple tense
- المستقبل البسيط future simple tense
- الزمن الماضي التام past perfect tense
- المضارع التام present perfect tense
- المستقبل التام future perfect tense
- الزمن الماضي المستمر past continuous tense

- المضارع المستمر present continuous tense
- المستقبل المستمر future continuous tense
- الزمن الماضي التام المستمر past perfect continuous tense
- الزمن المضارع التام المستمر present perfect continuous tense
- الزمن المستقبل التام المستمر[١٤] future perfect continuous tense

Amma shi yaren Hausa, kamar yadda malaman nahawu suka tabbatar yana da lokatai guda bakwai, savanin sigar umurni ko roqo, kuma waxannan lokatai za mu yi Magana akan su acikin darasi na musamman.

أما لغة الهوسا، فكما استقر عليه رأي النحاة، فإنها لديها سبعة أزمنة، وذلك بخلاف صيغة الأمر أو الدعاء، وهذه الأزمنة سوف نتناولها في الدرس الخاص بها.

Na shida: Ma'anar Kalmar "Zamani" a wajen Larabawa

سادسا: معنى كلمة "الزمن- الزمان" عند العرب

[١٤]- سارة حسن – الأزمنة في اللغة الإنجليزية- شرح كامل ومبسط- سلسلة تعليم اللغات- الشبكة العنكبوتية.

Kalmar “zamani” wajen larabawa, kamar yadda ya zo acikin Alqamusul muhix, da Lisanul Arab, suna ne “tilo” ana jam’inshi akan “zamuna” da “zamanoni” watau “Az-manun” da “Azminatun”

كلمة "زمن" عند العرب، وكما وردت في القاموس المحيط، ولسان العرب، اسم مفرد، يجمع على "أزمان و أزمنة"

Kuma tana nufin wani bangaren lokaci, kaxan xin shi da mai yawan shi.

وهي تعني المدة من الوقت، قصيرها "قليلها" وطويلها

Kuma tana nufin “zamani” ko “period” acikin turanci.

وتأتي أيضا بمعنى "العصر- الفترة من الزمن" أو ما يعرف في اللغة الإنجليزية باسم "period"

Kuma ana amfani da ita wajen kawwana (bunqasa) wasu lafuza, kamar haka:

وتشترك أيضا في تكوين بعض العبارات والمصطلحات الآتية:

A-Zamani ya shuxe masa عفا عليه الزمن

Watau, al’amari ya ci gaba ya wuce shi, sai ya zama koma baya, xan da.

أي، تجاوزته الأحداث، وصار متخلفا

B-Zamanin shi ya wuce ولّى زمنه

Watau, an gama yayin shi أي انتهى عهده

C-Na’urar zamani ta lokaci آلة الزمن

D-Azzamanul idafi الزمن الإضافي

Karin lokaci, watau lokacin da ake qarawa ga wani abu bayan qarewar lokacin sa na asali, kamar yadda yake faruwa a qwallon qafa, ko jarrabawa da sauransu.

ويقصد به مدة من الزمن تضاف إلى الحدث بعد انتهاء مدته الأصلية، كما يحدث في مباراة كرة القدم، والامتحانات وغيرها.

Na bakwai: Ma'anar Kalmar "Hien" wajen Larabawa

سابعا: معنى كلمة "حين" عند العرب

Kuma wannan lokacin bashi da wata alama wacce take nuni gareshi tare da waxannan lamiran: “na- ka- ya-ta” kuma wasalin waxannan lamiran gajeren wasali ne.

وليس لهذ الزمن علامة تدل عليه مع الضمائر الآتية: “na- ka- ya-ta” وحركة هذه الضمائر حركة قصيرة "gajeren wasali "

Kuma ya buga misalai akan haka da: ومثل لذلك بالآتي:

- Sanda na tafi
- Sanda ka tafi
- Sanda ya tafi
- Sanda ta tafi

Amma sauran lamiran hadda sakayau sai yace lallai alamar lokaci tana tare dasu, sune: “ka” misali:

أما باقي الضمائر بما فيها دالة المجهول فقال إن علامة الزمن معها، هي "ka " مثال:

- Sanda kika tafi
- Sanda muka tafi
- Sanda kuka tafi
- Sanda suka tafi
- Sanda aka tafi[41]

Shuxaxxen lokaci na biyu wajen Ahmadu Bello

الزمن الماضي الثاني عند أحمدو بللو

da dukkanin su Ahmadu Bello baiyi savani ba Neil Skinner da Ibrahim Yaro Yahaya da M. A.Z. Sani dangane da ma’anar wannan lokaci, inda yake cewa:

لا يختلف أحمدو بللو عن كل من Ibrahim Yaro Yahaya و Neil Skinner و M. A.Z. Sani بالنسبة لمفهوم هذا الزمن عندهم، حيث قال:

41 - see: Neil Skinner & Ibrahim Yaro Yahaya. P. 14

A-Idan za’ayi amfani da wannan lokaci tare da waxannan lamiran “na-ka-ya-ta” to bashi da alamar da take nuni gareshi.

أ- حين يستعمل هذا الزمن مع هذه الضمائر "na-ka-ya-ta" فليس له علامة تدل عليه

B- Wasalin waxannan lamiran gajeren wasali ne gajeren wasali

ب- الحركة في هذه الضمائر قصيرة

C- Idan za’ayi amfani da wannan lokaci tare da sauran lamira alamar da take nuni gareshi tana kasancewa “ka”

ت- حين يستعمل هذا الزمن مع باقي الضمائر تكون علامته التي تدل عليه هي "ka"

D-Lamirin shine yake fara zuwa sannan alamar lokaci sannan aikatau sannan sauran jumlar.

ث- يأتي الضمير أولا ثم علامة الزمن ثم الفعل ثم باقي الجملة

Sannan ya ambaci wasu misalai na jerin jumloli da wannan lokaci.

وذكر أمثلة لترتيب الجملة في هذا الزمن، هي:

- Na tafi

- ka tafi
- kika tafi
- ya tafi
- muka tafi
- kuka tafi
- suka tafi
- aka tafi

Kuma Ahmadu Bello ya sanya alama ataqaice ga wannan lokaci shi ne “sh-lok-2”

ووضع أحمدو بللو رمزا مختصرا لهذا الزمن وهو "sh-lok-2".

Bayan wannan bijirowa na ra’ayoyin malaman nahawun Hausa akan shuxaxxen lokaci na biyu wanda malaman nahawun turanci suke kiran shi da suna “relative past” zamu gane cewa:

وبعد هذا العرض لآراء نحاة الهوسا حول الزمن الماضي الثاني أو الموصول shuxaxxen lokaci na biyu والمعروف في اصطلاح النحاة الانجليزي باسم relative past يتبين الآتي:

A-malaman nahawu sunyi tarayya akan cewa babu alama ga wannan lokaci tare da waxannan lamiran “na- ka-ya-ta”

أ- اتفق النحاة على عدم وجود علامة لهذا الزمن مع الضمائر الآتية: "“na- ka-ya-ta

B-Wannan lokacin yana da alama tare da sauran lamiran, alamar itace “ka”

ب- لهذا الزمن علامة مع باقي الضمائر، وهي ”ka“

C-Alamar tana zuwa ne bayan lamiri kai tsaye kafin aikatau, watau tana zuwa tsakanin lamirin da aikatau

ت- تقع العلامة بعد الضمير مباشرة وقبل الفعل، أي أنها تتوسط الضمير والفعل

D-Yanayin wasalin lamiran dukan su gajeren wasali ne ko kuma abin da ake kira “short vowel”

ث- طبيعة حركة الضمائر كلها حركة قصيرة gajeren wasal أو ما يعرف باسم short vowel.

E-Dukkanin su Neil Skinner da Ibrahim Yaro Yahaya sun ambaci wannan lokaci da suna

Qaramin Qani ga shuxaxxen loakci na cikakke na xaya.

ج-أطلق كل من Neil Skinner و Ibrahim Yaro Yahayaعلى هذا الزمن اسم الشقيق الأضغر للزمن الماضي التام الأول.

F- Muhammad Hambali Jinju shi ne yafi dukkan malaman nahawun Hausa faxaxa bayani akan wannan lokaci

ح-يعتبر محمد حنبلي جينجو Muhammad Hambali Jinju أكثر النحاة الهوساويين الذين أفاضوا في شرح هذا الزمن.

Yanzu kuma za mju bijiro da wasu misalai waxanda suke nuni akan wannan lokacin, tare da gamsasshen fayyacewa na kowane misali tare da lamirin da yake nuni akan shi.

وفيما يلي عرض لبعض الأمثلة التي تدل على هذا الزمن، مع تحليل مفصل لكل مثال مع الضمير الدال عليه.

<u>Wakilin suna “na” a cikin Shuxaxxen Lokaci na biyu</u>

<u>الزمن الماضي الثاني مع الضمير "na "</u>

المثال	الزمن Nu’in lokaci	علامة الزمن Alamar/manunin lokaci	الضمير Wakilin suna	الفعل Aikatau
أنا كتبت الدرس Ni na rubuta darasi	Sh-lok-2	Ø	أنا Na	كتب Rubuta

<u>Wakilin suna “ka” a cikin Shuxaxxen Lokaci na biyu</u>

<u>الضميرالمفرد المذكر المخاطب “ka” في الزمن الماضي الثاني</u>

المثال	الزمن Nau’in lokaci	علامة الزمن Manunin lokaci	الضمير Wakilin suna	الفعل Aikatau
أنتَ كتبت الدرس Kai ka rubuta darasi	Sh-lok-2	Ø	Ka	كتب Rubuta

Wakilin suna “ki” a cikin Shuxaxxen Lokaci na biyu

الضمير “ki” في الزمن الماضي الثاني

المثال	الزمن Nau’in lokaci	علامة الزمن Manunin lokaci	الضمير Wakilin suna	الفعل Aikatau
أنتِ التي كتبتِ الرسالة Ke ce wadda kika rubuta wasiqa. M.H. jinju p.37	Sh-lok-2	Ka	Ki+ka= kika	كتب Rubuta

Wakilin suna “ya” a cikin Shuxaxxen Lokaci na biyu

الضمير "ya" في الزمن الماضي الثاني

الفعل Aikatau	الضمير Wakilin suna	علامة الزمن Manunin lokaci	الزمن Nau'in lokaci	المثال
كتب Rubuta	Ya+Ø= ya	Ø	Sh-lok-2	هو الذي كتب الدرس Shi ya rubuta darasi

Wakilin suna "ta" a cikin Shuxaxxen Lokaci na biyu

الضمير "ta" في الزمن الماضي الثاني

الفعل Aikatau	الضمير Wakilin suna	علامة الزمن Manunin lokaci	الزمن Nau'in lokaci	المثال
كتب Rubuta	Ta+Ø= ta	Ø	Sh-lok-2	Ita ta rubuta darasi

هي التي كتبت الدرس				

Wakilin suna “mu” a cikin Shuxaxxen Lokaci na biyu

الضمير ”mu“ في الزمن الماضي الثاني

المثال	الزمن Nau’in lokaci	علامة الزمن Manunin lokaci	الضمير Wakilin suna	الفعل Aikatau
نحن الذين كتبنا الدرس Mu muka rubuta darasi	Sh-lok-2	Ka	Mu+ka= muka	كتب- rubuta

Wakilin suna “ku” a cikin Shuxaxxen Lokaci na biyu

الضمير ”ku“ في الزمن الماضي الثاني

المثال	الزمن Nau'in lokaci	علامة الزمن Manunin lokaci	الضمير Wakilin suna	الفعل Aikatau
أنتم الذين كتبتم الدرس Ku kuka rubuta darasi	Sh-lok-2	Ka	Ku+ka= kuka	كتبسمي Ambace

Wakilin suna "su" a cikin Shuxaxxen Lokaci na biyu

الضمير "su" في الزمن الماضي الثاني

المثال	الزمن Nau'in lokaci	علامة الزمن Manunin lokaci	الضمير Wakilin suna	الفعل Aikatau
هم الذين كتبوا الدرس Su suka rubuta	Sh-lok-2	Ka	Su+ka= suka	كتب Rubuta

darasi				

Wakilin suna na ba asani ba (a) cikin Shuxaxxen Lokaci na biyu

دالة المجهول"a " في الزمن الماضي الثاني

المثال	الزمن Nau’in lokaci	علامة الزمن Manunin lokaci	الضمير Wakilin suna	الفعل Aikatau
إذا كُتِبَ الدرسُ Idan aka rubuta darasi	Shu-lok-2	Ka	A+ka= aka	كتب rubuta

Daga abin da ya gabata zamu gane cewa:

من خلال ما سبق يتبين لنا الآتي:

A- Malaman nahawu sun yi tarayya akan cewa shuxaxxen lokaci na biyu idan wata jumla ta masa wadda aikau xinta xaya ne daga cikin waxannan lamiran “ni-ka-ya-ta” bashi da wata alama da take nuni gareshi, kuma wasalin waxannan lamiran yana kasancewa gajeren wasali ne ko kuma abinda kira “short vowel”

أ- اتفق النحاة على أن الزمن الماضي الثاني حينما تأتي فيه جملة فاعلها أحد هذه الضمائر ”ni-ka-ya-ta“ لا تكون له علامة تدل عليه، وتكون حركة هذه الضمائر قصيرة gajeren wasali أو ما يعرف باسم short vowel.

B- Sauran lamiran kuwa idan sunzo tare da wannan lokaci to yana da alama wadda take nuni gareshi, wannan alamar itace: “ka”

ب- باقي الضمائر حين ترد في هذا الزمن فتكون علامته الدالة عليه هي ”ka“

C- Wannan lokacin yana faruwa a yanayi guda biyu:

1- Na farko shine idan jumlar ta qunshi xaya daga cikin waxannan kalmomin waxanda aka sani da

suna lamiran dagantaka: wanda- wadda- waxanda- wacce…ds.

2- Na biyu shine idan jumlar ta qunshi xaya daga cikin waxannan kalmomin waxanda aka sani da suna kalmomin tambaya, sune: wa- wane ne- me- mene ne- yaushe- shin- ina- yaya- don me- nawa- sabo dame- ds.

ت- يحدث هذا الزمن في حالتين:

١- الحالة الأولى وهي حينما تشتمل الجملة على أحد هذه الكلمات التي تعرف باسم lamiran dagantaka، وهي wanda- wadda- waxanda- wacce

٢- الحالة الثانية حين تشتمل الجملة على أحد هذه الكلمات والتي تعرف باسم kalmomin tambaya وهي: wa- wane ne- me- mene ne- yaushe- shin- ina- yaya- don me- nawa- sabo dame :

D-Wannan lokaci shi ake kira “shuxaxxen lokaci na biyu” ko kuma “Qanin lokaci na an gama”

ث- يعرف هذا الزمن باسم: shuxaxxen lokaci na biyu أو Qanin lokaci na an gama

E- Ana masa alama ataqaice da (sh-lok-2)

ج-يرمز إليه اختصارا هكذا: .(sh-lok-2)

الزمن المضارع | Lokaci mai ci

الزمن المضارع الأول | lokaci mai ci na xaya

الزمن المضارع الثاني | lokaci mai ci na biyu

أولا: الزمن المضارع الأول (المستمر) Na farko: lokaci mai ci na xaya

M. H. Jinju ya ambace shi da suna "lokacin da ake ciki" kuma yana nufin lokacin da aiki yake faruwa acikin shi, wato lokacin da aka fara aiki, sai dai ba'a qare (gama) shi ba.

ويطلق عليه M. H. Jinju اسم lokacin da ake ciki ويقصد بذلك الزمن الجاري فيه حدوث الفعل، أي الذي بدأ فيه ولكن لم ينته بعد.

Inda ya buga wasu misalai, yake cewa:

حيث ضرب بعض الأمثلة، فيقول:

- Sani yana wanke allonsa.

- ثاني يغسل لوحه
- Sani ya soma wanke allonsa.
- بدأ ثاني يغسل لوحه
- Kafin in ba wani labara cewa, shi sani “yana wanke allonsa”.
- وقبل أن أُخبر أحدا أن ثاني "يغسل لوحه"
- Ya kyautu mu gane cewa, sani yana cikin halin wanke allonsa sa’in da na ganshi
- يستحسن بنا أن نفهم أن ثاني هو في حالة غسل لوحه عندما رأيته
- Ni kuwa na ba da labarin yana ci gaba da aikinsa ne.[42]
- وأنا أخبر الخبر وهو يستمر في عمله.

Kuma zai bayyana garemu daga waxannan misalan:

ويظهر لنا من هذه الأمثلة الآتي:

1- Alamar lokaci wadda take nuni gareshi itace: “na”, kuma tana zuwa ne bayan lamiri kai tsaye sannan aikatau ya biyo bayanta.

42 -see: M.H.J p. 40

- علامة الزمن التي تدل عليه، هي : "na" وتأتي بعد الضمير مباشرة، ويعقبها الفعل مباشرة .

2- Wararen da wannan lokacin yake zuwa, daga ciki akwai:

- المواضع التي يتحقق فيها هذا الزمن، من بينها:

a- Idan kalmomin aikatau suka zo na wannan lokaci bayan aikatau wanda yazo acikin shuxaxxen lokaci kuma yana nufin farawa, kamar yadda yazo acikin misali na biyu.

- أن يأتي التركيب الفعلي لهذا الزمن بعد فعل وقع في الزمن الماضي ويفيد البدء، كما في المثال الثاني.

b- Idan wannan kalmomin na aikatau suka zo wajen bayar da amsa ga jumlar bayanau, kamar yadda yazo cikin misali na uku.

- أن يأتي هذا التركيب الفعلي جوابا لجملة ظرفية كما في المثال الثالث.

Shi kuwa M.A.Z. Sani yana cewa dangane dashi:

ويقول عنه M.A.Z. Sani :

Wannan kuma nuni yake yi da abin da ke gudana ahalin da ake ciki.

أي: هذا يدل على ما يحصل في الوقت الحاضر.

a- Wakilin suna (da Karin sautin sama)

- الضمير الشخصي (مع علامة النبر المرتفعة)

b- Manunin lokaci (naa)

- علامة الزمن (naa)

c- Suna.

- الاسم.

Kuma zai bayyana garemu anan cewa wannan bijirowar na bangarorin farko waxanda ya kamata ace jumla ta qunshe su acikin wannan lokaci, sune:

ويتبين لنا هنا أنه عرض للمكونات الأساسية التي ينبغي أن تحتوي عليها الجملة الواقعة في هذا الزمن، هي:

A-Wakilin suna, kuma Karin sautin dake cikin shi Karin sama ne, “high tone” wanda malaman nahawun Hausa suke kira “Karin sautin na sama”

- الضمير الشخصي وتكون النغمة التي في الضمير wakilin suna مرتفعة high tone، أو ما يعرف عند نحاة الهوسا بـ Karin sautin na sama

B-Alamar lokaci (naa) wato mai dogon wasali.

- علامة الزمن (naa) أي ذات الحركة الطويلة

C-Suna ana nufin da shi anan cikin sigar masdari.

- الاسم (suna) ويقصد به هنا الفعل في صيغة المصدر

Sai tsarin jumlar ya kasance kamar haka:

وبالتالي يكون ترتيب الجملة على النحو التالي:

Wakilin suna → alamar lokaci → Aikatau (cikin sigar masdari)

الفعل في صيغة المصدر ← علامة الزمن ← الضمير

Kuma ya kawo misalai kamar haka:

ويمثل لذلك على النحو التالي:

Wakilin suna الضمير	Alamar lokaci علامة الزمن	Masdari المصدر	Jumla الجملة
	Naa	Rubutawa	Ina rubutawa

أنا i		الكتابة	أنا أكتب
Ka أنتَ	Naa	Rubutawa الكتابة	Kana rubutawa أنتَ تكتب
Ki أنتِ	Naa	Rubutawa الكتابة	Kina rubutawa أنتِ تكتبين
Ya هو	Naa	Rubutawa الكتابة	Yana rubutawa هو يكتب
Ta هي	Naa	Rubutawa الكتابة	tana rubutawa هي تكتب
Mu نحن	Naa	Rubutawa الكتابة	muna rubutawa نحن نكتب
Ku أنتم- أنتن	Naa	Rubutawa	kuna rubutawa أنتم- أنتن تكتبون

		الكتابة	
Su هم-هن	Naa	Rubutawa الكتابة	suna rubutawa هم- هن يكتبون
A دالة المجهول	Naa	Rubutawa الكتابة	ana rubutawa يُكتب[٤٣]

Kuma akan mahimmancin wannan lokacin ne M. A. Z. Sani yake cewa:

وحول أهمية هذا الزمن يقول M. A. Z. Sani

"wannan lokaci kuma, nuni yake yi da abinda ke gudana ahalin da ake ciki"[٤٤]

Amma su Neil Skinner da Ibrahim yaro yahaya sun ambace shi da suna "lokaci na ana yi- ko lokaci mai ci, wato ba ariga an gama ba tukuna.

---

43 - see: M.A.Z. Sani p. 74

44 - ibid. p. 74

أما Neil Skinner و Ibrahim yaro yahaya فيطلقان عليه اسم lokaci na ana yi أو lokaci mai ci أي: الزمن الجاري حدوث الفعل، أو المستمر.

Suna nufin loakcin da ba’a gama aikata fi’ilin ba wato yana nan yana gudana.

ويقصدان بذلك الزمن الذي لم يُنتهَى من الفعل الحادث بعد، أي ما زال الفعل مستمرا فيه.

Kuma sunyi tarayya akan cewa alamar da take nuni gareshi itace “naa” kamar yadda suke ce:

ويتفقان أيضا على أن علامته التي تدل عليه هي "naa " وذلك كما في قولهما:

“alamar wannan lokaci mukan faxi na “naa” agaban kowane wakili kamar haka:

- Ina tafiya

أنا مسافر

- kana tafiya

أنتَ مسافر



- kina tafiya

  أنتِ مسافرة

- yana tafiya

  هو مسافر

- tana tafiya

  هي مسافرة

- muna tafiya نحن

  مسافرون

- kuna tafiya أنتم

  مسافرون

- suna tafiya

  هم مسافرون

- ana tafiya يُسافَر

  "المجهول"

Kuma sun riga sunyi bayani cewa alamar wannan lokaci itace “naa” kuma wasalinta dogo ne, sai dai basu bayyana yanayin Karin sautin ba na sama ne ko na qasa.

وقد أوضحا أن علامة هذا الزمن هي "naa " والحركة فيها طويلة، إلا أنهما لم يوضحا طبيعة النغمة مرتفعة أو منخفضة.

Kuma dole ne fi'ilin ya kasance cikin sigar masdari, kamar yadda yazo cikin misalin "tafiya"[45]

وأن الفعل لا بد أن يكون في صيغة المصدر كما في "tafiya ".

Shi ma Ahmadu Bello yayi tarayya akan cewa alamar wannan lokaci itace "naa" kuma ya kawo misalai akan hakan tare da wakilan suna dukkan su, kamar:

أما أحمدو بللو فيتفق هو الآخر على أن علامة هذا الزمن هي " naa" وأورد أمثلة له مع الضمائر كلها، منها:

- inaa rubutawa — أنا أكتب
- kanaa rubutawa — أنتَ تكتب
- munaa rubutawa — نحن نكتب

45 - See: Neil Skinner & Ibrahim Yaro Yahaya- p. 12

- anaa rubutawa يُكتَب

"المجهول"

sai yake cewa:

فيقول:

"Duk waxannan jumlolin suna nuna mana cewa ana cikin yin aiki ne na rubutu, kuma aikin na ci gaba ne, bai qare ba. [٤٦]

كل هذه الجمل تبين لنا أن عملية الكتابة لا تزال مستمرة ولم تنته بعد. ويواصل قائلا:

"Sabo da haka, ya kamata mu kira irin wannan nau'in na lokaci da suna "lokaci mai ci- lok-mc a taqaice".

ولذلك ينبغي علينا أن نطلق على هذا النوع من الزمن اسم "المضارع المستمر- ورمز له اختصارا بـlok-mc

Kuma zamu lura da waxannan abubuwa:

ونلاحظ هنا أيضا الآتي:

---

46 - See: Ahmadu Bello. P-61

A-jumlar da tazo a cikin lokaci mai ci tana zuwa ne awajen Ahmadu Bello akan wancan tsarin wanda aka ambata abaya.

- الجملة الواقعة في الزمن المضارع المستمر، تأتي عند أحمدو بللو على نفس الترتيب الذي أورده السابقون.

B-Shi fi'ilin ko yaushe yana zuwa ne acikin sigar masdari.

- الفعل دائما يأتي في صيغة المصدر

C-Ahmadu Bello ya sanya masa alama ataqaice wadda take nuni ga wannan lokacin, itace "lok-mc"

- وضع Ahmadu Bello رمزا مختصرا يشير به إلى هذا الزمن وهو " lok-mc"

D-Alamar da take nuni akan wannan lokacin itace "naa" kuma wasalin ciki dogo ne kuma Karin sautin na qasa ne.

- العلامة التي تدل على هذا الزمن هي "naa " والحركة فيها طويلة والنغمة منخفضة.

E-Muhammad Hambali Jinju ya ambace shi da suna "lokaci mai ci na xaya"

- أطلق عليه Muhammad Hambali Jinju اسم " lokaci mai ci na xaya" .

F- Su kuwa Neil Skinner da Ibrahim Y. yahaya sun ambace da suna "lokaci na ana yi" ko "lokaci mai ci"

- أطلق عليه كل من Ibrahim Y. yahaya و Neil Skinner اسم " lokaci mai ci" أو " lokaci na ana yi" .

- Ga wasu misalai nan waxanda suke nuni akan wannan lokaci.

وفيما يلي عرض لبعض الأمثلة والتي تشير إلى هذا الزمن:

Wakilin suna "I/ ina" a cikin lokaci mai ci na xaya

الضمير "أنا- المتكلم المفرد" في الزمن المضارع الأول أو المستمر.

Aikatau الفعل	Wakilin suna الضمير	Manunin lokaci علامة الزمن	Loakci الزمن	المثال
Karantawa يقرأ	Ina أنا Ina+na= naa	Naa	Lok-mc1	أنا أقرأ Ni ina karantawa

<u>Wakilin suna “ka” a cikin lokaci mai ci na xaya</u>

<u>الضمير "ka " في الزمن المضارع الأول أو المستمر.</u>

المثال	Loakci الزمن	Manunin lokaci علامة الزمن	Wakilin suna الضمير	Aikatau الفعل
أنتَ تقرأ Ka na karanta	Lok-mc1	Naa	Ka+naa= kana	يقرأ Karantawa

<u>Wakilin suna “ki” a cikin lokaci mai ci na xaya</u>

<u>الضمير "ki" في الزمن المضارع الأول أو المستمر.</u>

المصدر- الشاهد	Loakci الزمن	Manunin lokaci علامة الزمن	Wakilin suna الضمير	Aikatau الفعل

Kina rubutawa أنتِ تكتبين	Lok-mc1	Naa	Ki+naa= kina	كتابة "يكتب" الفعل في المصدر

<u>Wakilin suna “ya” a cikin lokaci mai ci na xaya</u>

<u>الضمير "ya" في الزمن المضارع الأول أو المستمر.</u>

المثال	loakci الزمن	Manunin lokaci علامة الزمن	Wakilin suna الضمير	Aikatau الفعل
هو يقرأ Yana karantawa	Lok-mc1	Naa	Ya+naa= yana	Karantawa يقرأ

<u>Wakilin suna “ta” a cikin lokaci mai ci na xaya</u>

<u>الضمير "ta" في الزمن المضارع الأول أو المستمر.</u>

المثال	Loakci الزمن	Manunin lokaci علامة الزمن	Wakilin suna الضمير	Aikatau الفعل
Tana karantawa هي تقرأ	Lok-mc1	Naa	Ta+naa= tana	تقرأ karantawa

<u>Wakilin suna “mu” a cikin lokaci mai ci na xaya</u>

<u>الضمير "mu" في الزمن المضارع الأول أو المستمر.</u>

المثال	loakci الزمن	Manunin lokaci علامة الزمن	Wakilin suna الضمير	Aikatau الفعل
نحن نقرأ Muna karantawa	Lok-mc1	Naa	Mu+na= muna	Karantawa نقرأ

Wakilin suna “ku” a cikin lokaci mai ci na xaya

الضمير "ku" في الزمن المضارع الأول أو المستمر.

المثال	Loakci الزمن	Manunin lokaci علامة الزمن	Wakilin suna الضمير	Aikatau الفعل
(إن كنتم للرؤيا تعبرون) (idan kun kasance ga mafarki kuna fassarawa) Yusufu aya-43	Lok-mc1	Naa	Ku+na= kuna	Fassarawa تعبرون- تفسرون
Kuna karantawa أنتم تقرأون	Lok-mc1	Naa	Ku+na= kuna	karantawa يقرأ

Wakilin suna “su” a cikin lokaci mai ci na xaya

الضمير "su" في الزمن المضارع الأول أو المستمر.

المثال	loakci الزمن	Manunin lokaci علامة الزمن	Wakilin suna الضمير	Aikatau الفعل
هم يقرأون Suna karantawa	Lok-mc1	Naa	Su+naa= suna	karantawa يقرأ

Wakilin suna “a ” (na wanda ba’a sani ba) a cikin lokaci mai ci na xaya

الضمير أو دالة المجهول "a " في الزمن المضارع الأول أو المستمر.

المثال	loakci الزمن	Manunin lokaci	Wakilin suna	Aikatau الفعل

	الضمير	علامة الزمن		
karantawa يقرأ	A+naa= anaa	Naa	Lok-mc1	يُقرَأ للطلاب الدرس Ana karanta ma xalibai darasi

<u>Na biyu: Lokaci mai ci na biyu</u> <u>ثانيا: الزمن</u>

<u>المضارع الثاني</u>

Shi ne ake kira “relative continous tense” da turanci, kuma haqiqa Muhammad H. Jinju ya ambace shi da suna “lokacin da ake ciki na biyu”. Anan Yana nufin shine wanda faruwanshi bai gushe ba yana gudana, kuma ya sanya masa alama da Kalmar “na biyu” domin ya banbanta shi da lokaci na farko.

وهو ما يعرف في اللغة الإنجليزبة باسم Relative continous tense.[٤٧] وقد أطلق عليه Muhammad H. Jinju باسم " lokacin da ake ciki na biyu". وهنا يعني الزمن الذي لا يزال حدوثه قائما أو جاريا، ورمز له بكلمة الثاني na biyu لتميزه عن الزمن الأول.

Kuma akan shi ne da kuma wanda ya gabace shi, Muhammad Hambali Jinju yake cewa: “lokacin da ake ciki na biyu, yana nuna cewa aikin yana cikin halin aukuwa (a yanzu).

وفيه وفي سابقه يقول Muhammad Hambali Jinju :

هذا الزمن المضارع يوضح لنا أن الفعل لا يزال في حال حدوثه "ما زال يجري حدوثه حتى الآن".

---

[47] - Modern Hausa English Dictionary, p. 144

“Ana amfani da ‘yan sassa biyu “na” da “ke” domin nuna yanzu ne ake yin abikin”[٤٨]

وتستخدم له علامتان لتدل على أنه الآن لا يزال حدوث الفعل قائما، وجعل "na" للمضارع الأول وجعل "k " للزمن الثاني الذي بين يدينا الآن.

وضرب أمثلة على ذلك فقال:

Misali:

- Yanzu nake rubuta wasiqa
- Yanzu kake rubuta wasiqa
- Yanzu kike rubuta wasiqa
- Yanzu muke rubuta wasiqa
- Yanzu suke rubuta wasiqa
- Yanzu ake rubuta wasiqa.

[48] - See: Muhammad Hambali Jinju- P. 40

Lokaci mai ci na biyu wajen M. A. Z. Sani

الزمن المضارع الثاني عند M. A. Z. Sani

Ya ambace shi da suna "lokaci na yanzu na biyu". Yana cewa akanshi: "wannan ma nuni yake yi da abin da ke gudana a halin da ake ciki."[٤٩]

يطلق عليه اسم "lokaci na yanzu na biyu " ويقول فيه: "يوضح لنا هذا الزمن أن الفعل يجري حدوثه الآن، (هو في حال الحدوث الآن).

A wajen qoqarin banbance tsakanin wannan lokacin da wanda ya gabace shi ne zamu ga yana yana cewa: "banbancinsa da (L.Y.1) shi ne wajen manunin lokaci."[٥٠]

---

[49] - See: M. A. Z. Sani- p. 75
[50] - ibid p- 75

وفي محاولة قام بها للتفريق بين هذا الزمن وسابقه من نوعه نراه قد قال: " الفرق بينه وبين الزمن المضارع الأول المستمر (L.Y.1) هو فقط علامة الزمن.

Kuma ya ambace gavovin zubin jumla acikin wannan lokacin, inda yake cewa:

Zubin wannan lokaci

a- Wakilin suna (da karin sautin sama)
b- Manunin lokaci (kee)
c- Suna

وقد ذكر عناصر ترتيب الجملة في هذا الزمن، فقال:

نظام هذا الزمن:

- الضمير الشخصي وتكون النغمة فيه مرتفعة
- علامة الزمن (kee)
- الاسم

Zamu iya Karin bayani akan haka:

ويمكن إضفاء مزيد من الشرح على هذا:

A- Ya bayyana cewa wakilin suna shike fara zuwa, kuma dole sai Karin sautin dake tare da wannan wasalin ya kasance Karin sama “high tone”

- يقول فيه: يأتي الضمير الشخصي أولا ويشترط أن تكون النغمة المصاحبة لحركة هذا الضمير مرتفعة "high tone ".

B- Ya iyakance manunin lokaci, shine (kee) kuma dole sai wasalin shi ya kasance dogon wasali, wannan shine dalilin da yasanya ya rubuta shi amaimaice (kee), kamar yadda yayi nuni akan cewa dole sai Karin sautin ya kasance na qasa ne “low tone”.

- حدد فيه علامة الزمن وهي (kee)، واشترط فيها أن تكون حركتها طويلة وهذا هو السبب في أن يجعلها مكررة (ee). كما أشار إلى ضرورة أن تكون النغمة فيها منخفضة "low tone ".

C- Kuma ya iyakance shi cikin faxinsa “suna” zamu lura anan cewa ya ambaci suna maimakon aiki, saboda aikin da yazo tare da wannan

lokacin dole ya kasance acikin sigar masdari, shi kuwa masdari suna ne ba aiki ba.

- وحدده بقوله "الاسم" ونلاحظ هنا أنه ذكر "الاسم" بدلا من الفعل، وذلك لأن الفعل الوارد في هذا الزمن لا بد وأن يكون في صيغة المصدر، والمصدر اسم وليس فعلا.

Ya kuma kawo misalai akan wannan lokaci kamar haka:

وقد ذكر أمثلة لهذا الزمن على النحو الآتي:

- (Ni ne) na kee rubutawa
- (Kai ne) ka kee rubutawa
- (Ke ce) ki kee rubutawa
- (Shi ne) ya kee rubutawa
- (Ita ce) ta kee rubutawa
- (Mu ne) mu kee rubutawa
- (Su ne) su kee rubutawa
- (a) a kee rubutawa

Idan muka kalla waxannan misalan da M. A. Z. Sani ya kawo mana zamu gane cewa:

وبالنظر إلى الأمثلة التي أوردها M. A. Z. Sani يتبين لنا الآتي:

A- Wasalin wakilin suna gajeren wasali ne “short vowel”

- حركة الضمير الشخصي حركة قصيرة "short vowel "

B- Karin sautin wakilin suna Karin sama ne “high tone”

- نغمة الضمير الشخصي نغمة مرتفعة "high tone "

C- Wasalin manunin lokaci dogon wasali ne “long vowel”

- حركة علامة الزمن حركة طويلة "long vowel "

D- Karin sautin manunin lokaci karin qasa ne “low tone”

- نغمة حركة علامة الزمن نغمة منخفضة "low tone "

Lokaci mai ci na biyu wajen Neil S. da Ibrahim Y. Yahaya.

الزمن المضارع الثاني عند نايل سكينر وإبراهيم يارو يحي.

Kowannen su Neil Skinner da Ibrahim Y. Yahaya yana ambaton wannan lokacin da suna "qaramin qani ga lokaci mai ci na xaya inda suke cewa:

"Haka ma wajen lokacin ana yi, watau akwai qanin lokaci wanda muke fin amfani da shi a waxansu wurare cikin zance" [٥١]

يطلق عليه كل من Neil Skinner و Ibrahim Y. Yahaya على هذا الزمن اسم الشقيق الأصغر للمضارع الأول المستمر حيث يقولان:

"وكذلك بالنسبة للزمن المضارع "الأول" فهناك شقيقه الأصغر والذي نستخدمه كثيرا في مواضع مختلفة من حديثنا"

[51] - See: Neil Skinner & Ibrahim Y. Yahaya- p. 14

Kuma ya buga mana misalai waxanda suke nuna amfanin walikin suna cikin wannna zamani kamar haka:

وقد ضرب أمثلة تفيد استخدام الضمائر الشخصية في هذا الزمن، على النحو التالي:

- Sanda nake tafiya عندما أمشي
- Sanda kake tafiya أنتَ
- Sanda kike tafiya أنتِ
- Sanda yake tafiya هو
- Sanda take tafiya هي
- Sanda muke tafiya نحن
- Sanda kuke tafiya أنتم/أنتنّ

- Sanda suke tafiya

هم/هنّ

- Sanda ake tafiya.[52]

المجهول

Zamu lura anan cewa su biyun (N.S & I.Y.Y) basu ambaci wani abu ba wanda yake da alaqa da yanayin wasalin wakilin suna ba ko wasalin manunin lokaci.

ويلاحظ هنا أنهما (N.S & I.Y.Y) لم يذكرا شيئا يتعلق بطبيعة حركة الضمير وحركة علامة الزمن.

Kamar yadda za'a ga sun kawo aikin cikin sigar shi ta masdari (tafiya) wannan kuma ya dace da yanayin wannan lokaci.

كما لوحظ أنهما أوردا الفعل في صيغة المصدر (tafiya) وهذا يتناسب مع طبيعة هذا الزمن.

Lokaci mai ci na biyu wajen Ahmadu Bello

الزمن المضارع الثاني عند أحمدو بللو

[52] - ibid- P. 14

Ahmadu Bello yana ambaton wannan lokacin da suna "lokaci mai ci na biyu" kuma ya sanya masa alama ataqaice da (lok-mc1).

يطلق أحمد بللو على هذا الزمن اسم " lokaci mai ci na biyu" ورمز له اختصارا بهذا الرمز (lok-mc1).

Kuma ya banbanta shi da lokaci mai ci na xaya inda yake cewa:

وقد حدد الفرق بينه وبين الزمن المضارع الأول " lokaci mai ci na biyu" بقوله:

" Muna iya cewa abinda ya banbanta wannan da lokaci mai ci na xaya da na biyu, shi ne manunin lokaci".[٥٣]

أي: "نستطيع القول بأن الشيء الذي يميز بين هذا الزمن المضارع الأول المستمر عن الزمن المضارع الثاني، هو فقط علامة الزمن".

Ya kuma ci gaba da bayani, inda yake cewa:

ثم يذكر أيضا موضحا فيقول:

---

[53] - See: Ahmadu Bello- p. 63

“ A maimakon (naa) a lokaci mai ci na xaya, sai mu sa (kee) anan lokaci mai ci na biyu”[٥٤]

بمعنى "فبدلا من العلامة (naa) الخاصة بالزمن المضارع الأول نضع (kee) هنا للزمن المضارع الثاني.

Kuma yana cewa akan yanayin wasali acikin lokutan:

وحول طبيعة الحركة في الزمنين، فيقول:

“ Amma duk lokutan biyu, suna da Karin sautin sama a wakilin suna da kuma Karin sautin qasa a manunin lokaci. [٥٥]

ومعناه: "أما كل من الزمنين المضارع المستمر الأول زالثاني يتميزان بوجود النغمة المرتفعة high tone على حركة الضمير الشخصي، والنغمة المنخفضة low tone على علامة الزمن".

Kuma ya kawo misalai akan haka:

وقد أورد أمثلة تبين هذا، وهي:

---

[54] - ibid- p. 63
[55] - ibid- p. 63

- Na kee rubutawa

أنا أكتب

- Ka kee rubutawa

أنتَ

- Ki kee rubutawa

أنتِ

- Ya kee rubutawa

هو

- Ta kee rubutawa

هي

- Mu kee rubutawa

نحن

- Ku kee rubutawa

أنتم/أنتنّ

- Su kee rubutawa

هم/هنّ

- A kee rubutawa

المجهول

Kuma zamu gan shi yayi nuni cewa dole aikin ya kasance cikin sigar masdari, kamar yadda yake acikin misalan da suka gabata asama.

ونراه أيضا أشار إلى ضرورة أن يكون الفعل في صيغة المصدر، كما هو واضح في الأمثلة السابقة أعلاه.

A qarshe zamu iya cewa:

وفي النهاية نستطيع القول:

1- Sunan wannan lokacin ya banbanta awajen malaman nahawun Hausa kamar haka:

- اختلفت أسماء هذا الزمن لدى النحاة الهوساويين على النحو الآتي:

A- Ahmadu Bello ya ambace shi da suna “lokaci mai ci na biyu”

B- Muhammad H. Jinju ya ambace shi da suna “lokaci da ake ciki na biyu”

C- Kowannen su Neil Skinner da Ibrahim Y. Yahaya ya ambace shi da suna “qanen lokaci na lokacin ana yin a xaya” ko “lokacin ana yin a biyu”

D- M. A. Z. Sani ya ambace da suna “loakaci na yanzu na biyu”

- أطلق عليه Ahmadu Bello اسم " lokaci mai ci na biyu"
- أطلق عليه Muhammad H. Jinju اسم lokaci da ake ciki na biyu"
- أطلق عليه كل من Neil Skinner و .Ibrahim Y Yahaya اسم " qanen lokaci na lokacin ana yin a xaya" أو "lokacin ana yin a biyu "
- أطلق عليه M. A. Z. Sani اسم " loakaci na yanzu na biyu"

2- Malaman nahawu sunyi tarayya akan cewa dole aikin yazo awannan lokacin cikin sigar masdari.

- اتفق النحاة على ضرورة مجيء الفعل في هذا الزمن في صيغة المصدر

3- Ana gane alamar wannan loakci (kee) da cewa tana da dogon wasali da kuma Karin sautin qasa “low tone”.

- تتميز علامة زمن هذا الزمن (kee) بأنها ذات حركة طويلة ونغمة منخفضة low tone .

4- Wasalin wakilin suna gajeren wasali ne mai Karin sautin sama “high tone”

- حركة الضمير قصيرة وذات نغمة مرتفعة high tone.

Lokaci na Sabo الزمن الاعتيادي

Lokaci na sabo xaya ne daga cikin lokutan da ake dasu a Hausa, kuma an kira shi da wannan sunan lura da sabo wajen aikata aikin, ko kuma a wata ma’ana saboda maimaituwan faruwan aikin.

الزمن الاعتيادي وهو أحد الأزمنة الثابتة في لغة الهوسا، وسمي بهذا الاسم نظرا للاعتياد في حدوث الفعل، أو بمعنى آخر نظرا لتكرار حدوث الفعل.

bijiro da ra’ayoyin wasu malaman Kuma zamu nahawun Hausa akan shi, tare da fayyace ra’ayoyin nasu akai, kamar haka;

وسوف نعرض -أيضا- وجهة نظر بعض النحاة الهوساويين فيه، مع القيام بتحليل آرائهم ووجهات نظرهم فيه، على النحو الآتي:

Na farko: Muhammad Hambali Jinju ya ambace shi da suna “Lokacin sabawa” ko “ sabawa” kawai.

أولا: يطلق عليه Muhammad Hambali Jinju اسم " Lokacin sabawa" أو "sabawa " فقط.

Kuma ya iyakance alamomin shi cikin maganar sa:

ويحدد معالمه بقوله:

“In ana maimaita (ko an saba da yin) wani aiki za ayi amfani da (kan) a gabannin fi’ili”. [٥٦]

"إذا تكرر فعل الحدث أو اعتيد القيام به، فعندئذ تستخدم العلامة (kan) لتدل على هذا الزمن، ويكون موقعها قبل الفعل مباشرة.

[56] - See: Muhammad Hambali Jinju. P-39

Kuma ya buga misalai waxanda suke bayyana wannan lokaci da wajen manunin shi acikin jumla ko Magana, kamar haka:

وقد ضرب أمثلة تبين استخدام هذا الزمن وموقع علامته في الجملة أو العبارة، وهي:

- Na kan ci nasara — أنا أنجح (ناجح) دائما
- Ka kan ci nasara — أنتَ تنجح دائما
- Ki kan ci nasara — أنتِ تنجحين دائما
- Ya kan ci nasara — هو ينجح دائما
- Ta kan ci nasara — هي تنجح دائما
- Mu kan ci nasara — نحن ننجح دائما
- Ku kan ci nasara — أنتم تنجحون دائما

- Su kan ci nasara هم ينجحون

دائما

- a kan ci nasara[57]

يُنجح دائما

Daga waxannan misalan zamu ga cewa jumlar da tazo acikin wannan lokaci an tsara ta kamar haka:

ومن خلال هذه الأمثلة نرى أن الجملة الواقعة في هذا الزمن تتكون مرتبة على النحو الآتي:

1- wakilin suna

- الضمير الشخصي

2- manunin lokaci

- علامة الزمن (kan)

3- Aikatau

- الفعل

4- sai sauran jimla.

- ثم باقي الجملة

Haka kuma zamu ga baiyi Magana akan yanayin wasali ko Karin sauti acikin wannan lokacin ba.

[57] - See: Muhammad Hambali Jinju. P-39

كذلك لم يتعرض للحديث عن طبيعة الحركة أو النغمة في هذا الزمن.

Na biyu: M. A. Z. Sani ya ambace shi da suna "lokaci na sabo" kuma ya siffanta shi da faxar sa:

ثانيا: يطلق عليه M. A. Z. Sani اسم " loakci na sabo" ويصفه بقوله:

"lokaci na sabo shi kuma kamar yadda sunan ke nuni, ya danganci aiki ne wanda aka saba yin sa". [58]

"الزمن الاعتيادي وهو كما يشير الاسم، يدل على العمل الذي اعتيد على فعله.

Kuma ya siffanta tsarin jumlar dake zuwa tare dashi kamar haka:

ويصف ترتيب الجملة الواقعة فيه، هكذا:

a- Zagin aikatau (da Karin sautin sama)

- الضمير الفعلي

b- Manunin lokaci (kan)

- علامة الزمن (kan)

c- Aikatau

---

[58] - See: M. A. Z. Sani- P- 73

- الفعل

Sannan ya kawo misalai waxanda suke bayyana haka:

وذكر أمثلة توضح هذا، وهي:

Zagin aikatau	Manunin lokaci	Aikatau
Na	Kan	Rubuta
Ka	Kan	Rubuta
Ki	Kan	Rubuta
Ya	Kan	Rubuta
Ta	Kan	Rubuta
Mu	Kan	Rubuta
Ku	Kan	Rubuta
Su	Kan	Rubuta
A	Kan	Rubuta

Idan muka duba abin da M. A. Z. Sani ya kawo zamu ga cewa:

وبالنظر إلى ما جاء به M. A. Z. Sani نراه يبين الآتي:

1- Wasalin zagin aikatau (preverbial pronoun) na wannan loakci gajeren wasali ne (short vowel), kuma yana da Karin sauti na sama (high tone)

- حركة الضمير الفعلي (preverbial pronoun) في هذا الزمن حركة قصيرة (short vowel) وذات نغمة مرتفعة (high tone).

2- Wasalin manunin lokaci shima gajere ne (short vowel) kuma yana da Karin sauti na qasa (low tone).

- حركة علامة الزمن قصيرة (short vowel) وذات نغمة منخفضة (low tone).

3- Wannan lokacin ya kevanci ayyukan da aka saba aikata su ne kawai.

- يختص هذا الزمن بالأفعال التي تم التعود على القيام بها.

Na Uku: Neil Skinner da Ibrahim Y. Y sun ambace shi da suna “lokaci na al’ada” ko “sabau”.

ثالثا: يطلق عليه كل من Ibrahim Y. Y و Neil Skinner اسم "lokaci na al’ada" أو "sabau".

Inda suke cewa: “wannan mukan bayyana cewa muna da al’adar yin kaza da kaza”[٥٩]

ويحددان ذلك في قولهما: "هذا (الزمن) ممكن أن نقول فيه أننا قد تعودنا فيه على فعل كذا وكذا".

Kuma suna cewa akan manunin wannan lokacin:

وحول علامة الزمن التي تدل عليه يقولان:

“ ‘Yar kalma mai nuna wannan, ita ce (kan)”.[٦٠]

"هناك كلمة صغيرة أو بسيطة تدل عليه، وهي(kan):

Suna kuma cewa akan tsarin jumlar dake tare da wannan lokacin:

وحول ترتيب العبارة أو الجملة الواردة فيه يقولان:

“Ga ta nan tare da wakilin suna daki- daki”.[٦١]

" وها هي علامة الزمن تكون مصاحبة للضمائر الشخصية على التريب، كما في الأمثلة الآتية:

- Na kan yi haka

---

[59] - See: Neil Skinner & Ibrahim Yaro Yahaya- P- 15
[60] - ibid- p. 15
[61] - ibid- p. 15

- أنا تعودتُ فعل هذا

- Ka kan yi haka

- أنتَ تعودتَ فعل هذا

- Ki kan yi haka

- أنتِ تعودتِ فعل هذا

- Ya kan yi haka

- هو تعود فعل هذا

- Ta kan yi haka

- هي تعودتْ فعل هذا

- Mu kan yi haka

- نحن تعودنا فعل هذا

- Ku kan yi haka

- أنتم/أنتنّ تعودتم فعل هذا

- Su kan yi haka

- هم/هنّ تعودوا فعل هذا

- A kan yi haka

- أُعْتِيْدَ فعل هذا

Kuma abin lura anan shine basu ambaci wani abu ba akan yanayin wasali ko Karin sauti na zagin aikatau ko manunin lokaci.

ومن اللافت للنظر أنهما لم يذكرا شيئا عن طبيعة الحركة أو النغمة في كل من الضمير الفعلي وعلامة الزمن.

Na Huxu: Ahmadu Bello ya ambace shi da suna “lokaci na sabo” kuma ya sanya masa alama ataqaice kamar haka (lok-ns).

رابعا: يطلق عليه Ahmadu Bello اسم "lokaci na sab " أي الزمن الاعتيادي ويرمز له اختصارا بالرمز "lok-ns ".

Kuma ya iyakance tsarin maganar ko jumlar da tazo da wannan lokaci tare da misalai kamar haka:

وقد حدد ترتيب العبارة أو الجملة الواردة فيه مع الأمثلة على النحو التالي:

Wakilin suna	Manunin lokaci	Aikatau
Naأنا	Kan	Tsuguna

أنتَKa	Kan	Tsuguna
أنتِKi	Kan	Tsuguna
هوYa	Kan	Tsuguna
هيTa	Kan	Tsuguna
نحنMu	Kan	Tsuguna
أنتم-أنتنKu	Kan	Tsuguna
هم- هنSu	Kan	Tsuguna
المجهولA	Kan	Tsuguna

Haqiqa ya qarfafa dalilin wannan sunan cikin maganar sa: “Da zarar mun karanta waxannan jumloli, zamu lura da cewa duk abinda suke faxi wani abu ne wanda ya zama jiki”[٦٢]

وقد أرجح سبب تسمية هذا الزمن بهذا الاسم في قوله: "بمجرد أن نقرأ هذه الجمل (الأمثلة أعلاه) سنلاحظ أن كل فعل تتحدث عنه "الجمل والعبارات" أصبح أمرا معتادا- jiki.

[62] - See: Ahmadu Bello- p. 63

Sannan ya cigaba da cewa: “watau tsuguno ya zama abu ne da aka saba yinsa, saboda haka ne muka kira wannan (lokaci na sabo)[٦٣]

ثم يواصل قائلا: "إن الانحناء أو الجلوس القرفصاء هذا أصبح أمرا اعتيد عليه، ولذلك نحن نطلق على هذا الزمن اسم (lokaci na sabo) أي الزمن الاعتيادي.

Idan muka lura da Ahmadu Bello bai waiwayi zance akan wasalin zagin aikatau da manunin lokaci ba ta vangaren yanayin wasalin da kuma yanayin Karin sauti.

وبمراجعة Ahmadu Bello في هذا الزمن لم يتطرق إلى وضع حركتي الضمير الفعلي وعلامة الزمن من حيث طبيعة الحركة ومن حيث وضع النغمة.

<u>:Lokaci mai zuwa tare da nau’ukansa</u>

A- Lokaci na gaba na xaya

B- Lokaci na gaba na biyu

63 - ibid- 63

الزمن المستقبل بنوعيه:

أ- الزمن المستقبل الأول

ب- الزمن المستقبل الثاني

Ana nufi da wannan lokaci mai gabatowa (zuwa) wanda aka tabbatar da faruwar aiki acikin shi. Shine wanda Larabawa suka sani da suna "lokaci na gaba na ko kuma "lokaci na kusa". "زمن المستقبل الأول" xaya Kuma alamar shi awajen su itace "س" wadda ake haxata da farkon fi'ilin, misali: "zai aikata – zai سيفعل karanta سيقرأ".

ويقصد به الزمن أو الوقت القادم والمحقق أو المؤكد حدوث الفعل فيه. وهو ما يعرف عند العرب باسم "زمن المستقبل الأول أو القريب". وعلامته عندهم حرف "س" الملتصق بصدر الفعل، نحو "سيفعل- سيقرأ".

Kuma malaman nahawun Hausa suna da ra'ayoyi mu kawo su kamar haka: mabanbanta akan shi, za

وللنحاة الهوساويين آرائهم الخاصة فيه، وسنعرض لهم على النحو الآتي:

Muhammad Hambali Jinju yana cewa: “lokaci na gaba, ya kasu kasha biyu, acikin na farko an tabbatar aikin zai yiwu, acikin na biyu ba lallai bane za ayi aikin”[٦٤].

يقول Muhammad Hambali Jinju: " الزمن المستقبل ينقسم في نوعين. النوع الأول ويتم التأكيد فيه على القيام بفعل الحدث أو الشيء. أما الثاني فليس بالضرورة أن يتم فيه التأكيد على حدوث الفعل.

Kuma yana cewa akan alamar wannan lokacin: “ana amfani da kalma za, kana lamiri, kana fi’li”[٦٥]

وحول علامة هذا الزمن وترتيب الجملة فيه، يقول: "تستخدم كلمة (za) علامة لهذا الزمن وتأتي في أول التركيب الفعلي، ثم ضمير الفاعل، ثم الفعل"

Daga nan ne tsarin jumlar zai kasance kamar haka:

a- Manunin (alamar) lokaci “za”

b- Lamiri

c- Fi’ili

---

[64] - See: Muhammad Hambali Jinju- p.38
[65] - ibid- p.38

ومن هنا يكون ترتيب الجملة أو العبارة الفعلية هكذا:

أ- علامة الزمن (za)

ب- ضمير الفاعل

ت- الفعل

Kuma zamu lura cewa yayi amfani da kalmomi guda biyu waxanda asalinsu larabci ne, sune:

ونلاحظ أيضا أنه استخدم مصطلحين من أصل عربي وهما:

A- "Lamiri" maimakon "wakilin suna", ita kuwa Kalmar "wakili وكيل" itace xayar Kalmar wadda itama asalinta larabci ne, wasu da yawa suna amfani da ita wajen nuni akan "lamirin aikau" ko "wakilin suna".

B- Kalmar "fi'ili" maimakon "aikatau" domin nuni akan aiki.

أ- Lamiri بدلا من wakilin suna في حين أن كلمة wakili وكيل هي الأخرى من أصل عربي، ويستعملها الكثيرون للدلالة على ضمير الفاعل أو الضمير الشخصي.

ب- كلمة fi'ili بدلا من aikatau للدلالة على الفعل.

Sannan ya kawo wasu misalai waxanda suke bayyana yadda tsarin jumlar yake kasancewa da wannan lokacin:

ثم ذكر الترتيب الذي تكون عليه الجملة بهذا الزمن

1- Zan (za + ni= zani → zan) rubuta wasiqa.

سأكتب رسالة

2- Za ka rubuta wasiqa.

ستكتب (أنتَ) رسالة

3- Za mu rubuta wasiqa.

سنكتب رسالة

4- Za a rubuta wasiqa.

ستُكْتَبُ رسالةٌ

M. A. Z. Sani kuma yana cewa: “wannan nau’i na lokaci, shi kuwa nuni yake yi da aikin da za a wanzar tabbas a wani lokaci mai zuwa”. [٦٦]

ويقول M. A. Z. Sani : "هذا النوع من الزمن يشير إلى أن الفعل الذي سيحدث أمر أكيد في زمن قادم".

Kuma tsarin shi kamar haka yake ajere:

ومكوناته الأساسية، وعلى الترتيب، هي:

a- Manunin Lokaci (za a)

علامة الزمن (za a)

b- Zagin aikatau (da Karin sautin qasa)

الضمير الفعلي (بنغمة منخفضة)

c- Aikatau

الفعل

Misali:

وذلك على النحو الآتي:

- Zaa na (zan) rubuta

---

[66] - See: M. A. Z. Sani- p.

سأكتب

- Zaa ka rubuta

ستكتب (أنتَ)

- Zaa ki rubuta

ستكتبين

- Zaa ya (zai) rubuta

سيكتب (هو)

- Zaa ta rubuta

ستكتب (هي)

- Zaa mu rubuta

سنكتب (نحن)

- Zaa ku rubuta

ستكتبون (أنتم- أنتن)

- Zaa su rubuta

سيكتبون (هم- هن)

- Zaa a rubuta

سَيُكْتَبُ

Idan muka lura da waxannan misalan zamu ga cewa:

وبالنظر في هذه الأمثلة يتبين الآتي:

Na farko: Wasalin manunin (alamar) wannan lokacin dogo ne, mai Karin sauti na sama “high tone”

أولا: حركة علامة الزمن طويلة وذات نغمة مرتفعة Karin sauti na sama “high tone”

Na biyu: Wasalin wakilin suna gajere ne, mai Karin sauti na qasa “low tone”

ثانيا: حركة الضمير الشخصي wakilin suna قصيرة، وذات نغمة منخفضة Karin sauti na qasa “low tone”

Na Uku: Dole ne abar tazara kaxan tsakanin manunin (alamar) lokaci da wakilin suna.

ثالثا: لا بد من ترك مسافة قصيرة بين علامة الزمن والضمير.

Na Huxu: Manunin (alamar) lokaci ne zai fara zuwa afarkon jumla, sannan wakilin suna ya biyo bayansa, sannan aikatau, kamar haka:

رابعا: تتقدم علامة الزمن في أول الجملة، ثم يتبعها الضمير، ثم الفعل، على هذا الشكل :

Manunin lokaci	Wakilin suna	Aikatau	Jumla
Zaa	Na= zaa n (zan)	Rubuta	Zan rubuta wasiqa
Zaa	Ki	Rubuta	Za ki rubuta

			wasiqa
Zaa	Mu	Rubuta	Za mu rubuta wasiqa

Neil Skinner da Ibrahim Yaro Yahaya suna cewa: "Lokacin nan gaba ko mai zuwa, watau lokacin da ake ce masa future (fyuuca) da turanci.

ويقول Neil Skinner & Ibrahim Yaro Yahaya : "الزمن المستقبل أو القادم، يعني الزمن الذي يطلق عليه باللغة الإنجليزية اسم " future".

Shi ne mai sauqin ganewa domin akan sa "za" bayan kowane wakilin suna kamar haka:

- Zan tafi

سأذهب

- Za ka tafi

ستذهب أنتَ

- Za mu tafi

سنذهب نحن

- Za a tafi



Hakan na nufin lokaci ne mai saukin ganewa, saboda alamar shi itace (za) sannan sai wakilin suna bayanta, kamar haka:

وهذا يعني "إنه زمن يسهل التعرف عليه، لأن علامته (Za)، ثم بعدها الضمير الشخصي وذلك كما في :

Manunin lokaci	Wakilin suna	Aikatau	Jumla
Za	Na	Tafi	Zan tafi makaranta
Za	Ka	Tafi	Za ka tafi makaranta
Za	Mu	Tafi	Za mu tafi makaranta
Za	Su	Tafi	Za su tafi makaranta
Za	A	Tafi	Za a tafi makaranta

Kuma suna cewa akan manunin (alamar) “za” tare da wakilin suna (na) da (ya) waxanda suke komawa zuwa (zan) da (zai) : “kun gani wajen (zan) da (zai), mukan taqaita su ne, watau bama faxar (za na) ko (za ya) sai dai mu yanka wasullansu na harshe” [٦٧]

---

[67] - See: Neil Skinner & Ibrahim Y, Yahaya- p.12

وحول العلامة (za) مع الضمير (na) و (ya) اللتان تحولتا إلى (zan) و (zai) يقولان: "لقد رأيتم ما يتعلق بـ (zan) و (zai) فإننا اختصرناهما، أي لا نقول (za na) أو (za ya) ولكننا حذفنا (قطعنا) أو بترنا الحركة الأخيرة من كل منهما فأصبحا (zan) و (zai).

Shi kuwa Ahmadu Bello cewa yake yi: “Duk jumlolin da suna nuna cewa akwai wani abu da zai faru, watau “tafiya” anan gaba”.

أي: كل الجمل تبين أن هناك حدثا (أمرا) سيحدث، أي سيجري في المستقبل.

Watau, ba anyi bane, ba ko ana yi bane, ba kuma akan yi ba ne, a’a za ayi ne nan gaba.

أي: لم يتم فعله، ولا يجري حدوثه، ولم يعتاد حدوثه، بل الذي سيحدث في المستقبل.

Saboda haka zamu iya kiran wannan lokaci na gaba (lok-ng)[٦٨]

ولذلك سنطلق عليه اسم "الزمن المستقبل الأول" وقد رمز له اختصارا بالرمز (lok-ng).

Kuma yayi nuni akan wajen manunin (alamar) acikin jumla, da cewa tana riga wakilin suna zuwa, kuma ya buga misalai akan haka:

---

[68] - See: Ahmadu Bello- p. 64

وحول موضع العلامة في الجملة، أشار إلى أنها تسبق الضمير، وضرب أمثلة لذلك، منها:

- Zaa na = zan tafi
- Zaa ka tafi
- Zaa mu tafi
- Zaa a tafi[69]

<u>Na biyu: Lokaci na gaba na biyu</u> <u>ثانيا: المستقبل الثاني</u>

Lokaci na gaba na biyu shine wani yanayi ko fuska ta biyu na lokaci na gaba na xaya.

الزمن المستقبل الثاني هو الصورة الثانية أو الوجه الثاني للزمن المستقبل الأول.

Kuma bambancin lokaci na gaba na xaya da lokaci na gaba na biyu shine, shi faruwar aiki an tabbatar da shi a lokaci na xaya.

والفرق بين الزمن المستقبل الأول، والمستقبل الثاني، هو أن الحدث في الزمن الأول محقق الوقوع.

Amma shi lokaci na gaba na biyu, faruwar aikin da ake sa ran zai wanzu ba lallai ba, watau zai iya faruwa kuma ba lallai bane ya faru.

---

69 - ibid- 64

أما المستقبل الثاني فالحدث المتوقع حصوله فيه غير مؤكد، أي قد يحدث وقد لا يحدث.

Kuma zamu bayyana anan ra’ayoyin malaman nahawun Hausa waxanda aka ambata a baya lokacin bayani akan lokatai.

وسوف نعرض هنا آراء النحاة الهوسا السابق ذكرهم في شرح الأزمنة السابقة.

Kuma zamu kawo su kamar haka:

وسنعرض لهم على النحو التالي:

Na farko: Muhammad Hambali Jinju

Muhammad Hambali Jinju Ya ambace shi da suna “lokaci na gaba na biyu” kuma yana cewa akan shi: “A cikinsa ana amfani da lamirai masu Karin sauti mai faxowa”.[٧٠]

أولا: Muhammad Hambali Jinju

يطلق عليه Muhammad Hambali Jinju اسم " lokaci na gaba na biyu" ويقول فيه: "في هذا الزمن تستخدم الضمائر الشخصية ذات النغمة الهابطة والتي علامتها هكذا (^).

Kuma M. H. Jinju ya ambata cewa shi wannan lokaci za’a iya kiran shi da lokacin da babu tabbacin faruwan aiki acikinsa. Shi yasa ya sanya masa wannan

[70] - See: Muhammad Hambali Jinju. P.38-39

suna “Lokaci na gaba na biyu mara qarfi” savanin lokaci na gaba na xaya wanda ya ambace shi da “lokaci na gaba na xaya mai qarfi” lura da yiwuwar wanzuwar shi.[٧١]

ويذكر M. H. Jinju أن هذا الزمن يمكن تسميته بالزمن غير المؤكد حدوث الفعل فيه، ولذلك أطلق عليه هذا التعبير " Lokaci na gaba na biyu mara qarfi" أي: الزمن المستقبل الأول المؤكد أو القوي، وذلك نظرا لإمكانية حدوثه.

Amma M.H. Jinju bai ambaci wata alama (manuni) ba awannan lokaci, ya kuma bayyana tsarin jumlar da ta zo dashi kamar haka:

ولم يذكر M.H. Jinju علامة لهذا الزمن تدل عليه، وقد حدد شكل العبارة أو الجملة الواقعة فيه على النحو الآتي:

- Na rubuta wasiqa
- Ka rubuta wasiqa
- Na rubuta wasiqa — سوف أكتب رسالة
- Ka rubuta wasiqa — أنتَ سوف تكتب رسالة
- Kya rubuta wasiqa — أنتِ سوف تكتبين رسالة
- Ya rubuta wasiqa — هو سوف يكتب رسالة

[71] - ibid: p. 39

- Ta rubuta wasiqa هي سوف تكتب رسالة
- Ma rubuta wasiqa نحن سوف نكتب رسالة
- Kwa rubuta wasiqa أنتم سوف تكتبون رسالة
- Sa rubuta wasiqa هم سوف يكتبون رسالة
- A rubuta wasiqa سوف تُكْتَبُ رسالةٌ

Kuma daga cikin bambancin wannan lokaci da sauran lokuta shine, wakilin suna na biyu na mace da sauran wakilan jam'i suna canzawa su koma kamar haka:

ومن الفوارق بين هذا الزمن وسائر الأزمنة الأخرى أن ضمائر المخاطب للمفرد المؤنثة وسائر ضمائر الجمع قد تغيرت فيه فأصبحت هكذا:

Ke-ki→ kya

Mu→ mu

Ku→ kwa

Su→ sa

Na biyu: M. A. Z. sani   M. A. Z. :يقول عنه

sani ثانيا:

Yana cewa akan shi: "Wannan ma nuni yake ya da aikin da za a wanzar a wani lokaci mai zuwa, sai dai kuma babu tabbas".٧٢

"وهذا الزمن يشير إلى أن الحدث سوف يتم القيام به في وقت من الأوقات إلا أنه غير مؤكد.".

Kuma ya bayyana tsarin jumlar dake zuwa dashi kamar haka:

وقد أوضح ترتيب الجملة فيه على النحو الآتي:

A-Zagin aikatau (da Karin sautin sama)

الضمير الفعلي ذو النغمة المرتفعة

B-Manunin laokaci (a)

علامة الزمن (a)

C-Aikatau [73]

الفعل

---

[72] - See: M.A.Z. Sani- p.76

[73] - ibid: P. 76

Anan zamu iya lura da waxannan abubuwan:

وهنا يمكن ملاحظة الآتي:

1- M. A. Z. Sani ya bayyana wasalin wakilin suna cewa yana da Karin sautin sama “high tone”, shi kuwa Jinju cewa yayi Karin sautin faxau “falling tone”

- لقد وصف M. A. Z. Sani حركة الضمير الشخصي بأنها ذات نغمة مرتفعة "high tone"، في حين قال عنها Jinju نغمة هابطة falling tone.

2- Manunin (alamar) lokaci wadda M.A.Z. Sani ya ambata (a) yana da Karin sautin qasa “low tone”

- علامة الزمن التي قال بها M.A.Z. Sani وهي (a) تتميز بأنها ذات تون منخفض (low tone).

3- Manunan (alamomin) guda biyu sun haxe tare sun bada Karin sauti mai faxuwa “falling tone”

- التقت العلامتان فكونتا معا النغمة الهابطة falling tone أو ما تعرف أيضا بالنغمة الساقطة.

Kuma ya kawo misalai yadda za’ayi amfani da wannan lokaci kamar haka:

وذكر أمثلة لاستعمال هذا الزمن، منها:

- Naa rubuta

  سوف أكتب

- Kaa rubuta أنتَ سوف تكتب
- Ki a rubuta أنتِ سوف تكتبين
- Mu a rubuta نحن سوف نكتب
- Ku a rubuta أنتم- أنتن سوف تكتبون
- Su a rubuta هم- هن سوف يكتبون
- A a rubuta[74] سوف يُكْتَبُ

Na uku: Neil Skinner & Ibrahim Y. Yahaya

Sun ambace shi da suna "lokaci mai zuwa na biyu" kuma sun siffanta shi da cewa shi qaramin qane ne na lokaci mai zuwa na xaya, kamar yadda suke cewa: " Lokatai huxu xin nan, watau na an gama, da na nan gaba, da na anayi da makasudi su ne manya, amma akwai saura guda uku waxanda zamu iya cewa su ne qannensu".[٧٥]

ثالثا: Ibrahim Y. Yahaya و Neil Skinner يطلقان عله اسم " lokaci mai zuwa na biyu" ويصفانه بأنه الشقيق الأصغر للزمن المستقبل الأول، وذلك كما في قولهما: "الأزمنة الأربعة هذه، الماضي

[74] -See: M.A.Z. Sani- p.76

[75] - See: Neil Skinner & I. Y. yahaya p.13

والمستقبل والمضارع والشرطي الاحتيالي هي الأزمنة الكبيرة، وهناك ثلاثة أزمنة أخرى يمكن أن نطلق عليها الأزمنة الصغرى، أي: الأزمنة الأخوات الصغرى.

Na huxu: Ahmadu Bello رابعا: أحمد بللو

Ahmadu Bello ya ambace shi da suna “lokaci na gaba na biyu” kuma yayi masa alama ataqaice da (lok-ng2) kuma ya ambata cewa manunin (alamar) shi itace (a) kuma yana da gajeren wasali.

يطلق عليه Ahmadu Bello اسم " lokaci na gaba na biyu" ويرمز له اختصارا بالرمز (lok-ng2)، وذكر أن علامته التي تدل عليه هي (a) وهي حركة قصيرة.

Kuma ya bayyana tsarin jumlar mai xauke da wannan lokaci kamar haka:

وقد حدد ترتيب الجملة في هذا الزمن على النحو الآتي:

A-Wakilin suna

- الضمير الشخصي

B-Manunin lokaci (a)

- علامة الزمن (a)

C-Aikatau

- الفعل

Kuma ya bayyana wasu wakilan suna waxanda aka sama xan canji acikin su akan wannan lokacin. Su ne:

وحدد أيضا بعض الضمائر التي حدث لها تغيير طفيف في هذا الزمن، وهي:

Ki→ kya

Mu→ ma

Ku→ kwa

Su→ swa/ sa

Kuma Ahmadu Bello ya bayyana cewa Karin sautin wasalin waxannan wakilan suna na wannan lokaci mai faxuwa ne “Karin sauti faxau” “falling tone”.

ويقول Ahmadu Bello أن النغمة المصاحبة لحركة الضمائر الشخصية في هذا الزمن هي نغمة هابطة "Karin sauti faxau " والتي تعرف اصطلاحا بـ "falling tone ".

Kuma alamar wannan Karin sauti na faxau itace (^) kuma tana zuwa ne kai tsaye bayan wasali, kamar yadda yake faxi :

وعلامة هذه النغمة الهابطة هي (^) وتكون فوق الحركة مباشرة، وذلك في قوله:

“Babu shakka idan aka karanta wakilan suna da Karin sauti faxau (watau /^/), zai nuna cewa…”[٧٦]

